[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Ƙirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

1

A duk lokacin da Allah (S.W.A) ya ƙaddara wanzuwar hallitar Ɗan adam a doran ƙasa, ko ya ƙi ko ya so akwai waɗansu abubuwa da suke yin jerin gwano a gangar jiki da ruhinsa. Inuwa! Wata aba ce da Ubangiji ya ke ƙaddara wanzuwarta manne a jikin kowanne abu, walau mai rai ko akasin haka. A kodayaushe tana bibiye da su matuƙar bawa zai zuba magananṣa zai lura da haka. Kalmar ƙaddara! Kalma ce mai ɗauke da rassa biyu walau ƙaddara mai kyau ko kishiyarta. Ƙaddara abokiyar tagwaitakar inuwa ce domin bawa ba ya taɓa shallake wa ƙaddararsa, sanin haka ya sa na fahimci karin maganar Malam bahaushe ta: 'Tun ran gini tun ran zane." ta zauna ɗaram kwatankwacin yadda ake ɗora ƙwarya a gurbinta.

10/06/1022
Shekara Dubu Ɗaya baya.

Hankalinsa ya fi na kowanne lokaci kai wa matuƙar ƙolokuwar tashi, yana tafe yana taku da sandarsa Waziri da sauran muƙarraban cikin daular suna take masa baya. Tamkar waɗanda saƙon mutuwa ya dirar wa haka fuskokinsu suka fasalta saƙon da ke ƙunshe cikin birnin zuciyoyinsu. Sarki Damina yana kai ɗora ƙafarsa kan jan dutsen da ke a matsayin matattakalar benen hawa tsauni tsidik! Wani gajiyayyan talakansan ya dira a gabansa cikin firgice da tashin hankali, kuka yake tamkar hawayen idanunsa za su ƙare. Ya ruƙo ƙafafuwan Sarki Damina a ɗimauce yana faɗin, "Ya kai babban Sarki, Sarkin sarkunan duniya bakiɗaya sarkin da yake share mana hawaye. Ka taimaka ka roƙar mana afuwa wurin Sarauniya Sha-kundum, yanzu haka ɗana Rabo yana can yana aman jini ta hanci ta baki don mai ɗakina naƙuda take jini ya ɓalle mata tana gangarar..." Tun bai rufe baki ba Sarki Damina ya daka masa razananniyar ƙarar da sai da hantar cikinsa ta kaɗa, yana shirin sake magana Sarki ya fisgi takobin da ke maƙale a kafaɗar Waziri kafin Bawan ya yi wani yunƙuri tuni ya sauke kansa ƙasa. Da sauri wasu ƙaratan Dogarai suka ƙarasa wurin suka zube suna yi wa Sarki godiya, "Godiya muke Sarki Damina mai masoya da yawa, Sarauniya Sha-kunduma ta yi ruƙo da hannayenka. Haushin zuciyarta ya gushe domin ta faɗa mana hanyar maganin samun lafiyar Yarima, idan wannan bai wadatar da kai ba ka yi mana umarni mu kawo maka wani ko da a cikin mu ne ka sake datse rayuwarsa matuƙar zai sanyaya zuciyarka" Bai tanka musu ba ya miƙa wa Waziri takobin da ke ɗigar da jini, har sun cicciɓi gawar bawan da kansa tuni ta samu mutsuguni a

gefen wata bishiya, Sarki ya dube su yana cewa. "A gaggauta ƙone gangar jikinsa tare da yaron nasa da ba shi da lafiya. Ita kuma mai ɗakinsa a zaro jaririn cikinta a kai wa babban dodo sannan a salwantar da gangar jikinta" Yana gama magana ya haye kan tsibirin maƙarrabansa suna biye da shi a baya.

Kamar yadda yake farillah a wurinsu duk lokacin da za su shiga cikin kogon dutsen a yanzu ma sai da suka aiwatar, sai da kowannensu ya saka ƙanƙanuwar aska ya yanki gefen ɗan yatsan hannunsa suka yarfar da jinin a jikin wani sassaƙaƙƙaen gunki, hannun gunki ɗauke yake da kwari da baka daga bayansa an jingina masa takobi a jiki. Kansa a sunkuye yake alamar ƙasƙantar da kai ga wani dungulmin kan mace da suka ɗora masa a gadon bayansa. Sarki Damina ne ya fara yin gaba sannan su Waziri suka rufa masa baya, daga bakin shiga dutsen suka tsaitsaya don sun san ko karan hauka ne ya cije su ba za su taɓa haure bakin ƙofar dutsen ba. Kai tsaye Sarki Damina ya kutsa ciki sandarsa ta zame masa abokiyar tafiya. Daga tsakiyar kogon dutsen ya hangi Boka Mai zamani zaune da wasu ƙanana tukwane a gabansa, daga shi sai ganyen ayaba wanda ya yi makari don rufe al'aurarsa.

"Yau ba ranar zuwan ka ba ce kamar yadda yake a bisa al'ada, me yake tafe da kai don na tabbata banza ba ta kai zomo kasuwa." Boka mai zamani ya faɗa yana karkatar da hankalinsa wurin Sarki Damina. Duk tsananin izza da taƙama irinta Sarki yau ya sauke ta a gefe ya fusakanci Boka yana mai bayyana damuwarsa, Sarki Damina ya zube gwiwowinsa kamar wanda ya aikata wani mummunan zunubin da yake neman gafara. Murya ɗauke da damuwa ya furta, "Ya kai Boka Mai zamani lamarin halin da talakawanmu suke ciki tabbas tura ta fara kai bango. A yau mun wayi gari da samun ɓillar annobar haɓo a cikin gari fiye da tsammani, babban abin da ya ɗugunzuma hankalina abin bai tsaya iya waje ba hatta ahalina na fuskantar wannan barazanar, a taimaka a roki Sarauniya Sha-kundum ta yafe mana tun da laifin wani ba ya taɓa shafar wani." Boka mai zamani ya miƙa masa busasshen hannunsa mai ɗauke da zaƙwa-zaƙwan farata, taurin hannunsa tamkar busasshen katako sannan ya ce, "Ina tukwicin ziyarar Sarauniya Gunki Sha-kundum kafin na san abin yi? Domin sanin kanka ne tuni bakin alƙami ya riga da ya bushe." Sai a lokacin Sarki Damina ya tuna da ƙoƙon tukwicin ziyara, cikin sake ƙanƙan da kai ya furta. "Sha-kundum ta dafa aikinka ta shiga lamuranka boka mai dogon zamani. Ka ga taka ka ga ta kakanninmu, iyayenmu duka sun wuce sun barka. Ya kai wannan boka mai dauwamamman ruhi da dogon zamani a yi mini afuwa bisa mantuwar da na yi, amma duk wani hukunci da Sha-kundum za ta yanke ni mai biyayya ne." Boka na gama jin haka ya miƙe ya tunkari bakin wata rijiya wacce faɗinta ya fi girman ƙaramin ɗakin, yana zuwa ya fara taka matattakalar da ke cikinta ya shige. Shigarsa ke da wuya bakin rijiyar ya shafe tamkar ba a taɓa wanzar da komai a wurin ba. Yana shiga kai tsaye ya tunkari gunkin wata mace da ke tsaye da tulelen tsohon ciki a jikinta, hannunta ɗaya tallafe da tsohon cikin ɗayan kuma yana riƙe da garkuwa alamun ta kare kanta da shi. Sai da ya sunkuya ya miƙa gaisuwa sannan ya furta, "Ya ke Sarauniya sha-kundum! Ya ke mammallakiyar wannan Daular a yau ma na sake dawowa da neman yafiyar al'ummarki.Na tabbata kina saurarena kamar yadda kika daɗe kina jina. Haƙiƙa talakawanki sun dawo da wata buƙata domin a yau sun wayi gari da samun annobar haɓo shin wane taimako za ki yi musu?" Hawayen ne ya ziraro daga cikin idanun gunkin, boka ya ƙarasa ya kanga kunnensa a jikin ƙirjinta. Ya jima a haka sannan ya ɗago cike

da girmamawa ya ce, "Tabbas zan isar musu kamar yadda kika buƙata, ki ƙara haƙuri nan ba da jimawa ba za ki dawo cikin ainihin hallitarki ta zahiri. Za ki ci gaba da mulkar al'ummarki kamar yadda kika mulke su a ɗaruruwan shekarun da suka gabata. Komai ya zo ƙarshe tun da ke kika tabbatar min da haka, sarauta da izzar mulki na baibaye da rayuwarki. Taɓewa da hallaka tana ga Maharba da Mafarauta har ƙarshen rayuwarsa." Yana gama maganar ya juya jiki a sanyaye kamar kazar da aka jefa da gishiri, yana taka matattakalar bene ɗaya rijiyar ta fara dawowa kamar yadda take da farko a wurin.

Kan shimfiɗarsa ta farko ya koma ya zauna ya dubi Sarki Balarabe yana faɗin, "Ta faru ta ƙare..." Da sauri Sarki ya katse shi da cewar, "Allah sa ba laifinmu ne ya sake hauhawa ba."

"Ka buɗe kunnenka da kyau ka saurari abin da Sha-kundum ta gaya min game da ku." Boka mai zamani ya faɗa fuska babu walawa. Shiru Sarki ya yi yana sauraron Boka. "Tabbas Sarauniyarmu Sha-kundum ta sake dawo wa kamar yadda ta faɗa a lokacin da numfashin zai ɗauke..." Baki na rawa Sarki ya katse boka da cewar, "A ina aka wanzar da ruhinta? A wane yanki ne mu sa a kawo mana ita? Idan ta kai bangon duniya na rantse da hatsabibanci Sarauniya da izzar mulkina sai na sa an ɗaukota a faɗin duniya." Boka ya bushe da wata irin mahaukaciyar dariya har yana birgima a ƙasa tamkar jakin da yake birgima a cikin sahara. Sarki sai da ya fusata ya doki ƙasa da tafin hannunsa sannan Boka mai zamani ya koma kan buzunsa  ya furta, "Haba Sarki Damina ai duk gaggawar ungozoma ta bari a haihu, haka duk mai niyyar yin sammako ya bari duhun dare ya gifta. Sarki Damina a kwai gaggarumar matsala, kamar yadda duk faɗin garin nan babu wanda ya taɓa gani ko jin sautin Sarauniya Sha-kundum sai ni, to tabbas a wannan karon ko ni ba ni da masaniyar a ɓangaren da wannan sabuwar sarauniyar take. Babban abin baƙincikin ma waɗanda suka sulwantar mana da ruhinta a cikinsu halitar Saruniya ta sake wanzuwa..." Tun bai ƙarasa magana ba jikin Sarki Balarabe ya fara rawa kamar wanda ake kaɗa wa gangi, a fusace ya miƙe tsaye yana huci tamkar kumurcin macijin da ke tsaka da fusata. A fusace ya furta, "Boka mai zamani ka na nufin Sarauniyarmu ta ɓullo daga cikin zuri'ar maharba da mafarauta ne?" Boka ya jinjina kai yana faɗin, "Ba harsashe ba ne Damina domin Sha-kundum ta tabbatar mini kuma kai shaida ne bata taɓa yin ƙarya, ta ba ni muhimmin saƙo gare ku na farautar Maharba a ko ina suke a faɗin duniya. Sai dai babban tashin hankalin ta yi alƙawarin ba za ta sake magana ba har sai na sada da ta da ainihin ruhinta. A sanyaye Sarki Damina ya furta, "Tirƙashi! Ana dara ga dare ya yi. Bayan wannan ina tafe akan buƙatar Yarima Nomau, babban boka lamarin ciwon yaron nan a kullin ƙara ta'azzara yake. A da muna haɗa shi da ƴan mata ɗaya zuwa biyu a rana amma yanzu har ta kai ga mata biyu ba sa iya gamsar da shi, kafi kowa sanin shi kaɗai na mallaka kuma har abada ba zan sake haihuwa ba. Idan na tuna ba ni da magaji lamarin na sake ɗugunzuma hankalina." Boka mai zamani ya hura ƙasar gabansa nan take wata ƴar ƙorama ta bayyana a wurin, sai da ya barbada wani garin magani sannan ya zura hannunsa ya warasu haɗe da runtse idanunsa tare da fara karanta waɗansu irin ɗalasuman tsafi, ƙirjin Sarki Damina ban da bugawa babu abin da yake yi saboda fargabar abin da Boka zai sanar da shi. Boka mai zamani ya jima a haka sannan ya buɗe idonsa yana kallon Sarki Damina haɗe da furta, "A kodayaushe maganar ɗaya ce! Kamar yadda na sanar maka Yarima Nomau ba zai taɓa warkewa ba matuƙar bai sadu da da inuwar wannan macen da nake gani a tattare da shi ba. Tabbas zai warke sai dai bazan taɓa

ce maka ga wa'adin lokacin da zai ɗauka cikin wannan tuburewar ba. Na ga haske jingine da su daga inuwar yarinyar nan na ga akwai rabo a tsakani, sai dai ka fi kowa sanin yadda aka yi aka samu Yarima Nomau don haka idan har ya samu rabo da wannan yarinyar Ɗa ko Yar da za su haifa dole zai zama mallakin Babban dodo ne, idan ba haka ba duk daren daɗewa za su zama masifa a daular nan. Kuma wannan hasken ba komai yake bayyana mini ba illa kusantowar warakarsa, don na lura akwai yuwuwar samun waraka nan ba da jima wa ba." Ajiyar zuciya Sarki ya yi don tun da yake zuwa wannan kogon bai taɓa jin labarin da ya faranta ransa kamar na wanan ranar ba  Ya dubi Boka fuska ɗauke da murmushi ya furta, "Ya kai babban malamin madogararmu shin zan iya sanin wacece yarinyar nan kuma a wane yanki take?" Boka Mai zamani ya girgiza kai yana cewa, "Lamarin Yarima Nomau ya wuce duk yadda kake tsammani, daga ni har bokayen duniya babu wanda yake da wannan amsar don haka ina mai baka shawara kar ka wahalar da gangar jiki da ruhinka akan abin da babu takamaimar amsa. Wani hanzari ba gudu ba, daga bayan wannan inuwar na hango wata baƙar ƙura wacce ta lulluɓe sararin samaniya sai dai ni kaina ban fahimci wacce irin ƙura ba ce koma dai wacce iri ce ina fatan za ta zame mana alkairi." Sarki Damina ya miƙe ya fara zagaye cikin kogon dutsen sai da ya zagaye boka mai zamani sannan ya ce, "Wannan ba zai zame mana matsala ba domin mun dogara da Sarauniya Sha-kundum da babban dodo na tabbata su za su kawo mana waraka a rayuwa. Yanzu wanne irin magani ta ba mu wanda za mu aiwatar mu da al'umnarmu?"

Boka mai zamani ya miƙe ya ƙarasa bakin rijiyar ya miƙa hannu ciki nan take ruwan cikinta ta kawo har sama sannan ya ɗebi ruwan da ƙoƙo ya miƙa wa Sarki Damina yana faɗin, "Wannan ruwan a je a zuba shi cikin kogon Ɗanbille duk wanda wannan annobar ta same shi ya ɗauka ya sha kai koda bata kama mutum ba zai iya wanka domin yin rigakafi. Wannan ce iya maganar da ta umarce ni na sanar da ku don haka za ka iya tafiya ya sarkin sarakunan duniya." Sanin ƙa'ida da dokar Sarauniya ya sa Sarki bai musa ba ya miƙe ba tare da ya furta koda kalma ɗaya ba, har ya je bakin ƙofa ya ji muryar Boka yana faɗin, "Ka da ka manta a kai wa Babban dodo Mai tsohon ciki biyu da idanun dattijai biyu." Gyaɗa kai kawai Sarki ya fice daga kogon dutsen.

Garin Dabur

Daga cikin bukkar da nake kwance ina bacci na fara jin hayaniya sama-sama, ina yunƙuri tashin na ji muryar mahaifiyata ta karaɗe majiyar sautina da cewar, "Yau wacce baƙar rana muke gani da yammacin haka? Ya abar bauta kada ki yi fushi da wannan mummunan zunubin domin ba mu da sa hannu a ciki, ka hukunta masu wannan zunubin da gaggawa don sun cutar da ƴar tsintuwar da bata ji ba bata gani ba." Ihun da Kandala take jerawa ne ya sa ni fito wa saboda duk wanda ya ji kukan nata ya san ba na lafiya ba ne. Jikina ne ya ɗauki tsuma sakamakon ganin halin da take ciki kace-kace da jini, a gefe ɗaya mutane daga jinsin maza da mata sun yi carko-carko a kanta suna kallon halin da take ciki. A gabanta na tsugunna raina ya kai ƙololuwar ɓaci, na dube ta fuska babu walwala na furta "Waye ya yi miki haka Kadala?" Ilahirin jikinta rawa ya ke don haka na kama hannunta na haɗa su da nawa na sake furta, "Babu abin da zai faru da ke ki gaya min waye ya yi miki haka?" Cikin yanayin azaba ta furta, "Ban san sunansa ba amma na ji wasu suna ce masa Barde." Ban jira ragowar maganar ta ba saboda tun farkon ganin halin da take ciki shi ne mutum ba farko da ya fara faɗo min a rai, saboda sanin

hali ya fi sanin kama. Barde riƙaƙƙen ɗan akuya ne baya iya kwana biyu ba tare da ya kusanci wala macen bil'adam ko dabba ba.

Ina miƙe wa na riski muryar Goga ya fara fito yana busa ƙaho wanda yake alamtawa sauran ƴan uwa na nesa da na kusa akwai fita ta gaggawa. Kafin ya gama busar da yake tuni gidanmu ya cika damƙam da sauran ƴan uwa maharba da mafarauta kowanne yana tafe cikin shirin dawa, ɗaya bayan ɗaya na kalle su kowannen su yana jiran umarnin da zan bayar. Jin na yi shiru ya sa Goje ya ɗaga gorarsa sama da hannun ɗaya, ɗayan hannun mai riƙe da kwari da baka ya sauke ya fara zabga mini kirari. "Burugu ce da kanta ba aike ba mace mai kamar maza ko cikin maza sai an tona. Cau cau cau cau ƙurungu mugun kifi sa'a a dawa sa'a a cikin gari wani aiki sai jan wuya makutsa daji, a lafiya uwar gidan kere amanar kura kyaci da gashi. Dawa dai, dawa gidan maza tsanani yana dajin Gurɓu ku bar faɗa musu wahalar sanar da su daɗin maza na cikin dawa mata na gida suna yin girki, wuya a dajin gwiɓau wuya a dajin fatalaki wuya ta ƙare a kan Barde yau ya taɓo ajalinsa." Ilahirin jikina ban da rawa babu abin da yake yi saboda tsumin da ya tayar min har nake jin da ace Barde na gabana babu abin da zai hana ban tsarge ruhinsa gida biyu ba, duk da kowa ya san Barde a cikin garinmu ba kanwar lasa ba ne.

Da sauri na faɗa bukkarmu na ɗabo gurun damatsan hannuwana da wuya, na kunce fatar mesar da ke ɗaure a ƙuguna na ɗaura ta damisa sannan na ɗauko kwari da baka haɗe da zabgegiyar adda na fito wurin da su Goga suke tsaitsaye. Suna ganina suka yi yunƙurin saka kai a hanzarce na dakatar da cewar, "Wannan fitar ba taku ba ce saboda Barde gidanmu ya taɓo ba ku ba, na yi rantsuwa da abar bauta ba zan dawo gida ba sai na sauke kan Barde daga gangar jikinsa, weeeehuuuuhuuuuu sai ni sarauniyar baka jikar marigayi Baushe amanar kura kawanciyarka ka huta muna tafe idan dabbobi sun ƙare. Sai ni yaƙi ban san wasa ba Abar bauta ta buɗa mana matuƙar na saka kai ko yau ko yanzu ban san namiji ba sai na ga tabo a jikinsa, wahala a hanyar tugu wuya a hanyar badake wuya ko da magani babu daɗi ko ana ha maza ha mata sai na dawo da kan Barde a hannuna." Ina gama zabga kirari cikin haɗin baki tawagar da ke wurin suka furta, "Dawa dai Sarauniyar kwari da baka, Abar bauta ta buɗa miki a dajin Gurɓu." Har na saka kai zan fita na dawo wurin Mahaifiyata na russuna saitin kunnenta ina faɗin, "Ki roƙar mini abar bauta da ta rinjayi ɗayan ruhin kar ya ziyarce ni ina tsoron kada Barde ya yi nasara akaina." Cike da ƙwarin gwiwa ta furta min, "Sa'a dai Sarauniya abar bauta ta buɗa miki ɓoyayyan ruhi ba zai ƙara ziyartar ki ba." Ina gama sauraronta na fice daga cikin gidan cike da ƙwarin gwiwa na nufi wurin da na tabbatar Barde na zama da ƴan koronsa.

Daular Sarki Damina.

Daga kogon boka mai zamani ya so kai ziyara bukkar babban dodo amma sai ya ga mafi dacewa ya fara zuwa wurin al'ummarsa ya umarci rundunar mayaƙansa da su fita yi masa farautar duk wata halitar bil'adam, musamman daga tsagin maharba da mafarauta kamar yadda suka saba yi a baya. A tsaitsaye suke dubbanin mutanen daular don a zatonsu maganin warakar annobar da ke damunsu aka kawo musu, Waziri ne ya yi gyaran murya sannan ya furta, "Ya ku waɗannan jama'a ya kamata kowa ya nutsu don jin saƙon da Sarauniya sha-kundum ta aiko." Tamkar ɗaukewar ruwan sama haka wurin ya yi tsit, Sarki Damina ya yi

gyaran murya sannan ya dube su ɗaya bayan ɗaya  ya sanar da su duk yadda suka yi da boka Mai zamani sannan ya ɗora da cewa, "Ina umartar manyan mayaƙan dakarun daular nan da su hanzarta fita cikin gaggauwa don yi mana farautar bayi kamar yadda suka saba a baya, kuma su yi sani cewa ya zama wajibi su farmako mana La'anannun hallitar can ta maharba da mafarauta a ko ina suke a faɗin duniya. Wannan umarni ne daga Sarauniya sha-kundum idan ba haka ba bala'in da muka shiga da wanda muke ciki a yanzu shafar mai ne akan abin da zai faru da mu a gaba." Yana rufe baki zaratan dakarun mayaƙan suka fara fita a guje zuwa mahallansu kowanne na fito wa da manyan makamai, runduna guda suka yi tsaya a gaban sarki Damina. Sai da ya ƙare musu kallo sannan ya kasa su gida huɗu, manyan zaratan mayaƙan ya ce su bi gabas hanyar da za ta sada su da ƙasar Dabur. Runduna ta biyu ya ce su bi Yamma hanyar da za ta sada su da ƙasar Baƙasud, runduna ta uku ya ce su bi kudu hanyar da za ta sada su da ƙasar Mubali sai tawaga ta huɗu da ya umarce su da Arewa wacce za su isa da Ƙasar Surima. Lokaci ɗaya suka bazama a yunwace da farauto kowanne irin bil'adam kamar yadda Sarkin da yake mulkarsu ya ba su umarni.

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananjn ban tausayi😰  ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Ƙirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

2

Fita ta ke da wuya na ci karo da Mahaifina da ya sawo kai ciki kafaɗarsa maƙale da barewa da ingarman zaki, ganin yanayina ya tabbatarsa masa akwai wani abu da yake faruwa don ya san fitarsa ban yi da shi zan shiga dawa ba. Cike da ladabi na miƙa masa gaisuwa irin tamu ta maharba ina faɗin, "Dawa dai Sarkin sarakuna uban dawa ga tsini ga mashi, ina gwanin wani ga nawa gamji kake ka fi ƙarfin saran maƙiya ɗan butar uban nan. A lafiya garnaƙaƙi uƙubar Gabatarawa, Abar bauta ta buɗa maka ka ci gaba da maganin munafukan mafarauta, sha zamanka ka ci gaba da kai dabbobi ƙasa wallahi ko yau ko gobe ko baka nan muna yi maka yaƙi." Cikin jin daɗi Mahaifina ya jingina gorar hannunsa da tawa sannan ya furta, "Dawa dai Sarauniya Abar bauta ta buɗa miki ko dare ko rana a dokar daji. Cau cau cau amanar Baushe wata wuyar sai a tsakiyar tsaunin Mani." Ɗora kokarata na yi a wuya na saɓi hanya tare da furta, "Sa'a dai ruwan saman mai dukan basarake da faƙiri, shawarar Duba amanar Duna." Kai tsaye mazaunin Barde na tunkara da ke cikin ƙasurgumin dajin Gurɓu, duhun almuru har ya fara karaɗe gari don haka na ƙara ƙaimi domin na cin musu don ba na son Barde ya sake shaƙar doguwar iskar numfashi.

Ganin dajin na sake yi min nisa kuma ina gudun rasa Barde a yammacin, ya sa na lalubi ramin bushiya cikin nasara na fisgota da ƙarfi tsiya, ƴar ƙaramar aska na ciro ya tsaga bayanta sannan lalubi ganyan tunfafiya na murje a bayanta, na damƙi ƙayoyi na soka a tsakiyar kanta. Sai da na kalli kusurwa huɗu da ita a hannuna sannan na saita hanyar da za ta sada ta da mazaunin su Barde na dire ta a ƙasa tare da furta, "Bisa ga Barde amanar Lado, ko tsuntsu kika gani kar ki bar shi ya kubce."

Tun ban rufe baki ba ta zabura da matsanancin gudu sannan na rufa wa sawunta baya. A lokacin da na ƙarasa wurinsu tuni na riski zaren carbin rayuwarsu ya kusa tsinkewa, ilahirin jikinsu ƙayoyi ne kwatankwacin yadda suke lulluɓe a jikin bushiyar da na aika musu, ganina ya harzuƙa Barde ya dube ni cikin huci yana cewa, "Uwar dawa me ye haɗina da ke da za ki aikata min haka ina cikin shaƙatawata? Ba don ina ganin mutumcinki ba da tuni na roki Abar bauta ta la'anci ruhinki kamar yadda kullin muke yi wa Baƙar Daula wannan addu'ar..." Tun bai rufe baki ba na ƙarasa wurinsa haɗe da yi masa mahangurɓar da ta kusa gigita lissafin rayuwarsa, a

fusace na sake kai masa duka a maƙoshi ina faɗin, "Barde yau akuyancinka ya kai ka wurin da ba za ka sake sanin wata ƴa mace ba sai a rayuwarka ta gaba idan ka na da rabo, ka roƙi Abar bauta da ta yafe maka zunubinka wataƙila ka samu sauyi a rayuwar da za ka dawo nan gaba." Wata sakaran dariya Barde ya saki sannan ya ce, "Wai kina nufin ƴar shilar da na latsa ta gidan ku ce? Ya aka yi haka bayan na san ke kaɗai kika wanzu a cikin gidanku?" Ban ba shi amsa ba sai wani mahaukacin duka da riƙa kai masa ta ko ina, ganin haka ya sa ya damƙi ƙasar gabansa haɗe da ɗaukan cinnaka ya ɗora a kai ya dunƙule su wuri ɗaya sannan ya ɗaga hannunsa sama ban yi aune ba na ji ya watso min ƙasar da ta rikiɗe zuwa jinsin cinnaku. Nan take muka fara sabon artabu kowanne yana son nuna ƙwarewarsa da ƙarfin jarumta da na tsatsuba, ganin hanyar da ya ɓullo da ita ba mai ɓille wa ba ce ya sa ya dube ni cikin hakki yana faɗin, "Kin cika zabuwa mai tsoro don na tabbata da ace ƙarfin damtse za mu gwada babu abin da zai hana ban yi nasara a kan ki ba, ya ke ƙasƙantacciya la'ananniya marar rabo, ya ke gajiyayyiya watsatssiya ƴar taka hayen maharba ba ƴat na koya ba. Wallahi ko giwa ta yi mushe ta fi ƙarfin bakin karnuka, dawa dai dawa ga mazaje ba mata ba Aradu mai tarwatsa ƙananan la'anannu ni Barde kabari nake duk daren daɗewa ina sauraronka." Wata irin kuɗa na ji har tsakiyar kaina yayin da maganganun Barde suka fara amsa-amo a majiyar sautina, daga bayana na fara jiyo sautin haniniyar dawakai tare da ƙarar ƙarafa da miyagun makamai, sannu a hankali na waiga don ko kaɗan na ƙi jinin wannan yanayin da nake riskar rayuwata a ciki. A duk lokacin da wannan yanayin ya riske ni na kan gaza sarrafa gangar jiki da ruhina don na banzatar da abin da nake gani a zahiri ba tare da wanda nake mu'amala da su sun riski abin da nake tozali da shi ba. Kamar wacce guguwa take fisga haka na riƙa jin ana fisgar gangar jikin da ke jingine da ruhina zuwa ga mayaƙan da nake riska suna tunkaro ni gadan-gadan, a koyaushe ina jin baƙincikin yadda nake yaƙar ƴan uwana wato jinsin Maharba da Mafarauta waɗanda su ne nake ganin rundunarsu cikin ƙwayar idona.

Ƙaddara wata abada ce da take sarƙe da gangar jiki da ruhi! Ni tawa ƙaddarar salonta mai tafiyar kura ne, ko a tarihi ban taɓa riskar makamanciyar irin tawa ƙaddarar ba.

Na fito daga cikin jinsin Maharba da Mafaruta, don haka na fi jin daɗin rayuwar cikin dabbobin daji akan mutane. Sai dai kash! Na tsinci ruhina a jikin wani gangar jikin da ba ta ahalina na Maharba ba, na rasa yadda aka yi nake iya rayuwa cikin jinsi biyu. Ko na aikata wani mummunan zunubin a rayuwata ta baya ban sani ba? Idan haka ne na cancanci hukunci irin wannan tun da gangar jikin da nake rayuwa da ita bata ji ba bata gani ba? Ban gama zayyana wa kaina jerun gwanon tambayoyin ba na hangi yadda suka zagaye ni tamkar yadda ale zagaye bakin rijiya, kamar yadda kullin nake ji a wannan karon haka gangar jikina ta riƙa ingiza ruhina ba don na so ba tafi da gudu na riƙa kai sara ina kare kaina. Da alama Barde mamakin abin da nake aikatawa yake don duk wanda yake tare da ni ba ya gani ko fuskantar abin da nake gani a maganaina. Ganin ya samu wannan damar ya sa ya biyo ta bayana a zabga min sara a kafaɗata, wanda fitar jini daga jikina ya haddasa wata irin gigitacciyar tsawa a dajin kamar yadda yake faruwa a duk lokacin da jini ya fita daga jikina. Abin sai ya haɗe min hagu da dama don na rasa wanne daga ciki zan kare duba da rundunar dake kawo min sara ga Barde da yake niyyar yin galaba a kaina. Ban yi aune ba wata irin juya ta fara katantawa da ni tun iya daga tsaye har na gagara mallakar kaina, wani saran na sake riska a gadon bayana wanda silar haka ya sa na durƙushe a wurin ga rundunar da ke gabana na son hallaka ni nan take.

Daular Sarki Damina.

Bayan watsewar tawagar rundunar mayaƙan Sarki Damina, daga harabar wurin kai tsaye keɓaɓɓan gida ya nufa wurin da Yarima yake rayuwarsa a ciki. Gidan an keɓe shi ga Yarima kaɗai saboda gata da kulawar da ake bashi sakamakon mummunar larurar da yake fama da ita, idan kuka zauna kuna ma'amala da shi ba za ka taɓa tsammanin yana da wannan ciwon ba har sai ya motsa za ka tabbatar da haka. Tun daga bakin ƙofar gidan har zuwa ƙofar ɗakin Yarima Maza ne suke gadinsa sakamakon mummunar lalurar da yake tare da ita, wannan dalilin ya sa hatta masu yi masa hidima maza ne don gudun abin da kaje-ya-zo. Saboda kafin a farga da lulararsa a baya mata ne suke yi masa hidima wani abin mamaki duk ranar da aka wayi gari sai an samu gawarwakin ƴanmata waɗanda ya yi musu fyaɗe, waɗansu su galabaita gudun ƙarin wahala Sarki ya sa a ƙonne su ko a binne su da ransu. Ba wannan ne dalilin da ya sa Sarki Damina ya kwashe mata ya sa aka zuba masa maza ba, saboda duk wani abu da zai faranta ran Yarima shi ya ke so bai da mu ba ko da matan yankin za su ƙare. A lokaci wata jarabta ce ta same su matan daular suka daina haihuwar ƴaƴa mata sai maza, wannan ne ya fargar da Sarki Damina ya taka tsibirin Boka mai zamani ya tuntuɓe shi game da haka, nan take ya sanar masa da matuƙar Yarima zai ci gaba da salwantar da rayuwar ƙanana yara mata tabbas za su wayi da ƙarewar ƴaƴa mata a gabaɗaya yankin. Idan kuwa haka ta kasance Sha-kundum za ta yi fushi da su fushi mai tsanani. Wannan dalilin ya sa Sarki yake saka ake zaɓar cikakkun mata da ƴan matan da suka isa ake kaiwa Yarima duk lokacin da larurarsa ta motsa.

Shigar Sarki ɗakin ya tarar da Yarima na ta wani irin kakari tamkar wanda yake gargarar mutuwa, hakan ce take faruwa a duk lokacin da larurar Yarima ta tashi idan ka ga yana wannan halin sai ka rantse ba zai ƙara rayuwa ba. Cike da tausayawa Mahaifinsa ya ƙarasa gabansa yana zura masa ido, duk dakiya irinta Sarki Damina sai da ya zubda masa ƙwallah. A haukace Yarima ya cakumo Mahaifinsa cikin fitar hayyaci da ɗimauta yana yunƙurin haike masa, da sauri Sarki Damina ya fara yunƙurin ƙwatar kansa amma tsananin ƙarfi irin na Yarima ya sa ya kasa, a kan dole dogarawan da ke kewaye da ɗakin suka runƙuro suka taimaka wa Mai martaba. A wahalce Sarki ya ke sauke ajiyar zuciya sannan ya furta, "Ku ɗebo masa ƴan mata biyar don ba na son na rasa yarima, shi kaɗai na mallaka ko matan garin nan za su ƙare sai an nemo masa wasu a faɗin duniyar nan." Tun bai kai ga rufe baki ba wata gihitacciyar tsawa ta ratsa ciki da wajen ma'adanar sautinsu. A razane Yarima ya rungume mahaifinsa don wannan ita ce tsawa karo ta biyar da suka sake riskar irinta. A baya duk ranar da aka yi musu tsawa irin wannan lokaci ɗayamatan Daular suka riskar kansu cikin ɓallewar jinin Al'ada har tsofaffi waɗanda lokacin yin su ya gushe musu, a gaggauce ya fita don isa ga bukkar babban Dodo don ya sanar musu wannan tsawar da wacce irin masifa ta zo musu. A daidai ƙofar keɓantaccan gidan Yarima ya tsaya ya ɗaga kansa yana kallon sararin samaniya, kururuwar dattijuwar ce ta dawo da shi daga duniyar harsashen da yake yi. Waɗansu manyan barada ne riƙe da gashin wata mai tsohon ciki da alama naƙuda take jini na bin ƙafarta, ɗayan yana riƙe da wani matashin saurayi da fuskarsa ke fidda habbon jini daga hancinsa. Tsohuwar na riƙe da su ana jan su tare tana kururuwa da roƙon Dogaran akan kar su aiwatar da abin da Sarki ya umarce su, gyaran murya ya yi lokaci ɗaya Dogarawan suka tsaya cak kamar waɗanda suka haɗiyi taɓare nan

take. Bawan da ke tsugunne a gabansa ne ya lura da inkiyar da Sarki ya yi don haka ya furta musu, "Sarki na buƙatar ganin ku a gabansa." A gaggauce suka ƙarasa gabansa bisa lura da yanayinsa suka fahimci ƙarin haske yake nema game da busasshiyar tsohuwar da take riƙe da mutanen da ya bayar da umarni a binne su. Wani narkeken Dogari mai ƙirar samudawa ne ya kwanta a gaban Sarki Damina, sai da ya lashi saman ƙafarsa sau bakwai sannan ya yi sujjada a gabansa yana faɗin.

"Abar bauta ta ja da zamanin adalin Sarki mai cikakken iko. Wannan tsohuwar mahaifiyar baiwarcen ce, muna ƙoƙarin cika umarninka ta nemi..." Bai ƙarasa maganarsa ba Sarki Damina ya ɗaga masa hannu tare da faɗin, "A kawo min ita." Tun Sarki bai gama maganar ba Tsohuwar ta yunƙura cikin tsananin firgici, ganyen da ke maƙale a ƙugunta wanda ya kasance shi ne tufafin da suke rufe al'aurar su, tuni ya samu matsuguni a ƙasa. Tun daga sama har ƙasa gudawa ce take bin ƙafafuwanta, jan ciki ta fara yi cike da tashin hankali da nadama tana cewa. "Ya Abar bauta ki yi gaggawar kawo min mafita daga wannan baƙin zalincin azzalumin bawan na ki." Da ƙarfin gaske Dogarin ya ƙarasa ya fisgi ƙafarta ɗaya wacce nan take ta yi ƙara ƙaras! Da alama ya karya ta ya fara ja bai dire ta ko ina ba sai a gaban Sarki Damina. Sandar da ke hannunsa ya saka ya dokare wuyanta nan take ta fara kakari sannan ya miƙa hannu zuwa idanunta, zaƙwa-zaƙwan faratansa ya saka ya zaro ƙwayar idanunta nan take ta ƙwalla wata gigitacciyar ƙara jini ya wanke fuskarta. A cikin wani ƙanƙanin ƙoƙo ya jefa ƙwayar idon sannan ya yi gaba, Fadawan da ke take masa baya ne suka bi shi sannan ya juyo ya ce, "Kada a binne ta a kaina ɗakin zuma ta ƙarasa tsokar jikinta." Daga haka kai tsaye ya wuce Bukkar babban dodo don lamarin tsawar da ta saba haddasa musu tashin hankali ba ƙaramin tsinka hantar cikinsa ta yi ba.

Tattakawa ya yi har ya shige gidan ƙasa wanda a nan ne bukkar babban dodo ta samu matsuguni, sai da ya yi sujjada sau bakwai a gaban bukkar sannan ya zura idanun tsohuwar a wata ƙanƙanuwar ƙoramar da ke gefen bukkar. Ta gefen tagar ya fara zayyane buƙatar da ke tafe da shi, sai da ya gama bayanin matsalolinsa daga cikin bukkar aka fara magana da wani irin yare cikin murya mai matuƙar ban tsoro. Ga wanda zuwansa ne na farko a lokacin da ya saurari muryar za ta iya kurumta sauraronsa, sai da aka yi yare sama da goma sannan aka fara maganar cikin harshen hausa.

"Tabbas jinin sarauniya Sha-kundum ne yake zuba a daidai wannan lokacin, hasalima rayuwarta tana cikin wani hali. Rasa rayuwarta a karo na biyu tamkar rushewar daular na ne gabaɗaya, na yi rantsuwa da tsabbun da na gada a wurin iyaye da kakannina matuƙar sakacinku ya sa kuka sake rasa Sha-kundum shakka babu kun rinƙa ganin masifu kala-kala kenan har ƙarshen rayuwarku." Hankalin Sarki Damuna ya fi na kowanne lokaci tashi, ga rabuwar shawarwari da ya samu daga wurin Boka mai zamani da babban dodo. Cikin damuwa ya furta, "Ya babban Dodo mai share mana hawaye kai ne mai ciyar da mu da shayar da mu a wane yanki wannan Sarauniya tamu take saboda na..." A tsawace aka furta, "Idan za ka zagaye faɗin duniya babu wanda zai tabbatar maka a nahiyar da take. Hasali ko da za ka yi tozali da ita ba za ka tantance fa ba sai dai alamu su nuna mana da isowarta ga mahaifarta, a kaf faɗin duniyar nan Boka Mai zamani ne kaɗai ya san kalar surar Sarauniya Sha-kundum kasamakon abin da

ya faru a shekara ɗari biyar baya da suka shuɗe, kuma ko da ta ƙaraso daular nan ba na jin jinin da ta sake wanzuwa a ciki na Maharba da Mafarauta zai bar jinin daular nan ya yi tasiri a jikinta. Sarainiyarku ta sake wanzuwa a cikin jinsin Maharba da Mafarauta, haka kundin ƙaddarar yake don haka ba mu da damar ninke babin ƙaddararta. Game da lalurar matan Daular nan ka ɗauki Mahaifiyarka mai babbar turaka kai ta wurin Yarima ya mu'amalanceta ni nake gaya maka ciwonsa zai daɗe bai sake tashi ba kuma munanan al'amura za su jima ba su sake faruwa ba. Idan ya gama ka kawo min dattin al'aurarsu zan taimaka muku na yi wani aiki da shi amma idan na gama haɗa shi wajibinka ne ka sadu da Mahaifiyarka domin kammalar aikin bakiɗaya."

Ajiyar zuciya Sarki ya sauke sannan ya furta, "A duk lokacin da aka ambaci wannan jinsi na Maharba zuciyata da raina na matuƙar ɓaci, amma babu komai haka shafin ƙaddarar yake za mu karɓe shi hannu bibbiyu. Ya kai babban dodon mai azurta wannan daular ka yi sani ko jinin Mahaifiyata ka ce na bawa Yarima zan bashi matuƙar sarautar nan ba za ta kuɓuce daga ahalina ba." Yana gama maganar ya sake yin sujjada sau bakwai sannan ya fice daga bukkar, kai tsaye ya wuce gidan mahaifiyarsa da suke yi mata laƙabi da mai babbar turaka. Yana shiga bayin da ke yi mata hidima suka fice don haka suke yi a duk lokacin da Sarki Damina ya ziyarce ta duk da sun fahimci a mafi yawan lokuta zuwansa ba alheri ba ne. Mahaifiyarsa Ladi na ganinsa gabanta ya faɗi tana shirin yin magana ya ce, "Ta so mu je na sadaki fa yarima." Idanunta ne ya ciko da ƙwalla ta ce, "Har gobe ba zan daina dana-sanin haihuwarka ba Damina, Mai martaba ya cuce ni shi da baƙon bafulatani..." Bata rufe baki ba Sarki Damina ya fisgi hannunta daga wurin da take zaune ya furta, "Saboda kin ci darajar Mahaifiyata shi ya sa na tako da kaina, wannan girma ne da daraja na baki da a cikin bayi ne Dogarai zan aika musu. Ki gode wa Abar bauta da ba dauwama za ki yi da Yarima yana mu'amala da ke ba, babban dodo ya kawo mana waraka ko ki taso ko na sa dogarai su fitar min da ke."

Hmmmm Wace ce sha-kundum kuma meye alaƙarta da ƴar maharba? Waye baƙon Bafulatani? Kuma ƴar maharba na mutuwa ko yaya? Me ye silar ciwon yarima kuma yaushe zai warke? Amsoshin na gaba ku dai kar ku bari a yi babu ku🏂💃

Na gaishe ku kyauta Cau cau cau cau, Allah buɗa mana fans🏂

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananjn ban tausayi😰 ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi

wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Kirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

3

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰 ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

Takunsa mai girgiza hankulan ƙananan dakuru ne ya karaɗe majiyar sautina, haniniyar dokinsa ta musamman ce a duk lokacin da ya ziyarce ni don ya kasance zara a cikin dubbannin taurari. A kodayaushe na kan rasa wane ne shi da yake faɗo wa cikin duniyata har ya kawo mata agaji a duk lokacin da nake yunƙurin sare wa da miƙa wuya ga mutuwa. Idanuwan suna kan fuskarsa ya yin da na faɗa duniyar tunanin samuwarsa, ban yi tsammani ba na riski sautinsa ya karaɗe dodon kunnena yana faɗin. "Sare wa da rashin nasara ba taki ba ce, a kullin ina gaya miki ke ɗin mai nasara ce! Ke ta daban ce don haka rayuwarki ma ta daban ce! Don haka kada ki sallama wa mutuwa rayuwarki don ba ki cancanci mutuwa yanzu ba, ki taimaka ki cika muradi da burinki. Surarki, nasabarki, tsatsonki, zuciyarki da asalinki ba sa daga cikin jerin masu rauni." Nutsuwata da hankalina gabaɗaya na sallama masa ina saurаron maganganun da yake furta min, ba yau na saba jin haka daga gare shi ba sai dai kalaman yau sun sha bambam da waɗanda yake sanar min. Ina yunƙurin yi masa magana cikin tsawa na ji ya furta, "Ki tashi na ce ki aiwatar da ƙudurunki cikin jarumta domin ke ba ki kasance gajiyayyiya ba." Tamkar wacce aka ƙarawa ƙaimi haka na ji wani masifaffan ƙarfi ya mamaye ilahirin jikina, a zabure na waiga wurin Barde da ya yi yunƙurin kawo min duka sai dai ɓarin makauniyar da na yi masa a fuska ne ya azabtar da ruhinsa. Ƙaraji yake tamkar wanda ake zare wa rai saboda azaba, kamar yadda na ƙudura a zuciyata haka na sake jadaddawa. Daga jikin ƙuguna na zaro wata ƙanƙanuwar wuƙa na ƙarasa gaban Barde kafin ya yi wani yunƙuri na kauda kai gefe haɗe da tsige al'aurarsa daga gangar jikinsa. Maƙarrabansa su baƙi-baƙi na ganin haka kowannensu ya cika wandonsa da iska saboda sun lura a yunwace nake da su ina iya tsalle na dira a gabansu na yi musu makamancin abin da na yi wa Barde, saboda duk tafiyarsu ɗaya hallayarsu ɗaya duka tare suke aikata kowanne irin ɓarna sai dai Barde ya fi su yin ƙaurin suna wurin aikata badaƙala.

Ina yunƙurin juya wa wurun tawagar da ke farmakar rayuwa na neme su na rasa tamkar ɗaukewar ruwan sama, jinin da ke ci gaba da zuba daga jikina ne ya haddasa min raunin garkuwar jikina, na fara takawa ina layi ga idanuna da suke yi mini dishi-dishi har ta kai ba na iya bambamce takamaimar hanyar da zan bi na koma ga muhallina. Kwatsam! Ban yi aune ba

na ji na faɗa jikin makamanciyar halitata ta bil'adam wanda hakan ya haddasa min sakin ragowar jikina a jikinsa. Muryarsa ba baƙuwa ba ce a gare ni hasali ma takan faranta zuciyata domin shi ɗin wani ɓangare ne daga tsakin zuciyata, ya kasance jini da tsokata ta yadda a kowanne hali nake ciki ina iya tabbatar da siffarsa mai cikar haiba da kamala. Idanuwana ne suka fara lumshewa, na riski ya huro min iskar bakinsa akan fuskata yana faɗin, "Abar bauta ta dafa miki a duk lamuranki ya ke sarauniyar maharba amanar Goje, ba kyau ba daɗi murucin kan dutse baki fito ba sai da kika shirya. Wane Mutum wawan mutum rana mai haske duniya kowa ya ƙarasa a bar shi ya kawo ƴar tsatson maharba. Cau cau cau cau sai ke Damisa amanar Duna, da wuya a dajin Gurɓu da wuya a dajin Dagumba wata wuyar sai mun tsallaka dajin Bagege. A lafiya shawarar Goga a lafiya amanar Goga, a lafiya wakiliyar Goga ko yau ko gobe kwarankwatsa dubu ko bakya nan ina yi miki yaƙi." Kirarinsa ne ya sake ƙarfafa zuciyata na ɗago a wahalce na jingina kerena (Ɗaya daga cikin makamin maharba ne.) A jikin Barandaminsa cikin amsa gaisuwa irin tamu ta Maharba na furta, "Sa'a dai mai dawa amanar Shamuwa amana sai ɗan amana, amana ta kai maka har dajin Gaduru." Ina rufe baki ya ciccibe ni ya ɗora a kafaɗa sannan ya wuce gida da ni. Tun a cikin dajin na ji yana yagar ganyayen magunguna da zan yi amfani da su, muna ƙarasawa gida aka kwantar da ni akan fatar kura wacce ta zame mana mashinfiɗin da muke hutawa. Hayaniya ce ta fara tashi a wurin matasa maza da mata suka cika damƙam, ganin halin da nake ciki ya sa Mahaifina ya sallami sauran mutanen da ke tsaitsaye a kaina, cike da takaici ya tsugunna a daidai kaina ya yin da ya yi tozali da irin jini da yake fita daga jikina sakamakon mummunan saran da Barde ya yi, yanayin fuskarsa ne ya bayyana min ɓacin ran da ya ziyarci zuciyarsa. Runtse ido ya yi ya furzar da iska mai zafi sannan ya furta, "Abar bauta ta ci gaba da dafa wa lamuranki ya ke sarauniya. Haƙiƙa ina baƙinciki raunin da yake ziyartar ruhinki, wanda dalilin haka yake sa a yi yunƙurin yin galaba a kan ki." Hannunsa na kama da hannuwana biyu, ina jin hawayen baƙinciki na neman ɗiga daga idanuna. Sarewa da karaya ba hali ko ɗabi'ata ba ce amma a wannan karon ina jin ƙwarin gwiwata ta yi rauni fiye da kullin, Mahaifina na lura da halin da nake ciki don haka ya shafa kaina tare da furta, "Namiji ba ya sarewa da ƙarfin magauta. A zahiri ke macece amma ni nasan nagartaccen jarumin namiji na haifa. Kada ki taɓa bari wani ya lura da rauninki, ko da wasa kar na sake ganin ruwan hawaye a ƙwayar idonki domin zai ba wa magautanki ƙwarin gwiwa a kan ki har su yi nasara su kai ruhinki kushewa." Daga wurin da nake kwance na dube shi sannan na furta, "Wuya bata raunata zuciyar 'yan maza koda kuwa a tsakiyar rundunar mayaƙan maƙiya ne, raunina ya dogara a kan ɓoyayyan lamarin da yake faruwa da ni ta yadda ba na iya mallakar gangar jiki da ruhina. Na yi rantsuwa da abar bautar da ke raya dare zuwa rana ta samar da yalwatacciyar ni'ima da kyautata noma, ba zan sake bayyana raunin da zai bawa magauta dama akaina ba koda kuwa rikicitaccen al'amarina zai ci gaba da farmakar rayuwata." Mahaifiyata ce ta miƙo masa ƙaron marke da ganyen zaƙami, ya saka su akan fatar zomo ya ƙwanƙwasa su da dutse sannan ya fara shafa min a wurin da yake zubar da jini. Ba a ɗauki lokaci ba jinin ya tsaya na riski muryar mahaifiyata tana faɗin, "Baushe me za a yi wa yarinyar nan a kan karyewar asirin jikinta, tun da abar bauta ta wanzar da ruhina ban taɓa bada maganin ƙarfe ya karye ba. Amma yarinyar nan babu abin da ba a bata ba duk lokacin da wannan al'amarin zai same ta sai ta rasa duk wani tsarin jikinta." Da kansa ya ɗauke ni ya kaina cikin bukkar mahaifiyata sannan ya tsaya a bakin ƙofar bukkar yana faɗin. "Kyauta ita kaɗai gare ni a faɗin duniya, don haka ba zan yi ƙasa a gwiwa ba don sake roƙar mata abar bauta akan ta

shiga lamurunta idan akwai zunubin da ta aikata ta shafe mata shi. Ban san zunubin da ta aikata ba da farauta take yi mata gudun mutuwa, ban san ya aka yi tsatson maharba yake son bijirewa zuri'arsa ba. A duk binciken da na yi babu tasirin tsafi ko asiri a jikin Kyauta, rauhanai sun sanar mini akwai wani ɓoyayyan al'amari game da ita sai dai sun garara sanar da ni komai daga cikin al'amuranta. Zan ziyarci abar bauta da mataimakanta ta taimaka min domin ita ce madogararmu mai taimaka mana da kawo mana mafita, ba zan rasa ki ba Kyauta domin lokacin mutuwarki bai zo ba har sai mun shiga Dajin Mugazu ta karɓo kambun sarauta da hannunta." A hankali na yunƙura na tashi zaune azabar da nake ji ta sa na cije bakina sannan na furta, "A taimaka a sada ni da Abar bauta akwai maganar da nake son tattaunawa da ita." Da mamaki ɗauke a fuskokinsu na ga sun kalle ni, Mahaifiya ta ƙaraso wurina ta ɗago ni tana cewa. "Abar bauta za ta saka miki albarka ziyararki babbar nasara ce albarkacin tsafi da farauta." Mahaifina ne ya kama ni muka wuce tsaunin Abar bauta ya yin da Mahaifiyata ta ci gaba da ba wa Kandala kulawar da ta da ce tana gasa ta da ruwan zafi don warkewar raunin da ke ƙasanta.

Daular Sarki Damina.

Duk yadda Mai babbar turaka ta kai ga ƙin amince wa da buƙatar Sarki fir ya ƙi saurarontà, da ƙarfin tsiya ya fisge ta ganin tana son kunto masa matsala ya cicciɓe ta ya ɗora a kafaɗa. Ciccila ƙafa ta rinƙa yi tana dukan kafaɗarsa bai saurari roƙonta ba ya fice da ita, a tsakar gidan keɓaɓɓan gida ya dire ta sannan ya kalli waɗansu ƙosassun dakaru masu siffar adawa ya ƙwala musu kira, tun bai rufe baki ba suka ƙaraso wurinsa sannan ya ce, "A gaggauta sada ta da Yarima almuru ya ƙarato zan kai gaisuwar ibada da roƙon ruwa." Kuka Mai babbar turaka take rusawa kamar ranta zai fita, yana shirin tafiya ta rarrafa tana jan ciki haɗe da ruƙo ƙafarsa tana faɗin, "Damina ni ce fa mahaifiyarka wacce ta ɗauki cikinka tsawon lokaci yanzu da kanka za ka sada ni da Yarima ya haike min ina ji ina gani?" Taɓe baki Sarki Damina ya yi ya tsugunna sannan ya ruƙo haɓarta ya furta, "Ban fiya son ja'inja da ke ba don ina matuƙar ganin mutumcinki." Ya ɗago yana kallon dogaran tare da furta, "A yi gaggawar wuce wa da ita." Daga haka ya fisge ƙafarsa mai babbar turaka ta faɗi gefe haɗe da kifa kanta a ƙasa tana ci gaba ta rusa kuka mai cin zuciya. Da ƙarfin gaske suka fisge ta duk irin magiyar da take yi musu bai sa sun saurara mata, saboda sanin kansu ne matuƙar suka saɓa wa umarnin Sarkin Damina tabbas za su tsinci talatarsu a laraba domin na su hukuncin sai ya ninka nata sau dubu.

Suna gab da shiga ɗakin, Mai babbar turaka ta dubi Nalami dogari cikin karayar zuci ta furta, "Ka taimaka ka bar ni ko na taƙi kaɗan ne zan bar musu wasiyyar da ba na son ku buɗe ta har sai bayan babu rayuwata. Jikinsu ne ya yi sanyi duk da kasancewar ba sa daga cikin masu tausayi, ganin tausayi na neman tasiri a zuciyarsu ya sa suka fisge ta da ƙarfin tsiya. Kamar mayunwacin zaki haka Yarima ya kurma wata uwar ƙara haɗe da janyo Mai babbar turaka da ƙarfin tsiya, ganyan da ke maƙale a ƙugunta da ƙirjinta ne ya faɗi gefe Yarima ya haɗe ta da jikinta tare da sauke buƙatarsa a haukaca akanta. Cikin fitar hayyaci ta riƙa ambatar sunan Damina tana tsine masa da aibanta shi da miyagun kalamai marasa daɗin saurare, sai da Yarima ya dawo cikin hayyacinsa ya fahimci Mai babbar turaka ta galabaita. A wahalce ta dubi Yarima yana faɗin, "Yarima mahaifinka ya yi min abin da ba zai taɓa albarka ba, akwai laƙanin da nake son taimakon wannan daular da shi amma yana cikin turakata..." Da sauri Yarima ya

tallafo kanta yana faɗin, "Laƙanin me ye kar ki tafi ba ki gaya min ba." Cikin kakari ta furta, "Ka tabbatar da ka yi tozali da sabuwar sarauniyarmu kuma ita ce za ta ɗauko..." Daga haka harshenta ya sarƙe idanunta suka ƙafe ta faɗi matacciya.

Zuwanmu tsibirin keda wuya muka samu dubbannin jama'ar yankinmu sun yi dafifi akan tsiribirin, da yake duk ranar talata da daddare muna taruwa akan tsibirin domin miƙa buƙatunmu ga abar bauta. Mun yi amanna akan duk wanda ya faɗi buƙatarsa a kan tsibirin tabbas buƙatarsa za ta biya. Kasancewar sun lura da halin da nake ciki ya sa suka buɗe min hanya muka wuce don isa ga abar bauta saboda akwai ƙudurin da nake son sanar da ita duba da rikitattun al'amuran da suke baƙuntar rayuwata. Muna gab da ƙarasawa muka riski sautin wakiliyar Abar bauta, ba mu sake tsinkewa daga lamarin ba sai da muka yi tozali da ita ta fito matsayar da ko a tarihin rayuwa ban taɓa jin ta fito harabar wurin ba. Kamar ɗaukewar ruwa sama haka wurin ya yi tsit kowanne ya baje majiyar sauti da maganansa, ko a mafariki ban taɓa tozali da siffar wakiliyar Abar bauta ba sai dai labarin da magaba suke ba mu akan samuwarta da tasirinta ga rayuwarmu.Tun bayan kafuwar yakinmu a tarihin da muka taɓa fuskanta, abar bautar wancen yankin bata taɓa fito wa ba sai a ranar da wani mummunan al'amari ya faru da su wanda sanadin haka ya sa aka kafa tarihi har muka mayar da ranar Talata a matsayin ranar karɓar addu'a kuma ranar biyan buƙata, domin a cikinta ne al'ummar Maharba suka samu ƙarfin iko da nasara akan Baƙar Daular da ke gaba da yankinmu. Sannan mahaifina ya tabbatar min a bisa al'ada duk lokacin da Abar bauta ta bayyana akwai wani mummunan al'amari da zai faru wanda zai hargitsa al'ummarmu.  Ban gama dawo wa daga duniyar tunani ba na riski sautinta tana faɗin, "Ya waɗannan al'aumma yau na bayyana kaina ne domin na shaida muku mummunan al'amarin da yake tunkaro mu kwatankwacin mummunar ƙaddarar da ta faru a baya. Kogon bincike ya ƙone ƙurmus! Hasken wutar abar bauta ta ɗauke. Buzun zakin abar bauta ya miƙe yanzu haka yana cen yana fidda aman wuta.

A yau na tsaya a gabanku domin na tabbatar muku da bala'in da yake tunkaro rayuwarku, ga taron rundunar baƙar inuwa tana tunkaro mu don haka ya zama wajibi mu haɗa ƙarfi da ƙarfe mu sake tserartar da yakinmu domin gujewa abin da ya faru ɗaruruwan shekarun da suka gabata, a zahiri dukkan alamun da suka bayyana a baya sune suke sake bayyana a wannan lokacin domin yanzu haka tazarar da ke tsakaninmu da wannan baƙin yaƙin bai fi taƙi kaɗan ba. Ina jin tsoron kada farmakin Baƙar Daula ya wanzu a gare mu duk da muna da tsarin da ko tsuntsu ba za su iya gani da idanunsu ba matuƙar ya kasance ɗaya daga cikin ahalinmu na Maharba." Ras! Na ji gabana ya faɗi musamman da na tuna Kandala bata daga cikin zuri'ar Maharba, hasalima tsarinmu ya katange da ita." Ina tsoron kar wani mummunan al'amari ya faru da ita. Hankali a tashe na furta, "Ba zan bari ba Kandala! Ba zan taɓa bari a cutar da ke ba tun da kaina na ɗauki alƙawarin kulawa da rayuwarki. Zalincin baƙar Daula ba zai taɓa ɗarsuwa a kanki ba koda zan rasa rayuwata tun da ni ce sillar salwantar iyayen da suka haifo ki don haka zan bada jini da ruhina akan ki.

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Kirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

4

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰 ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

Gudun kada Abar bauta ta fahimci abin da nake faɗa ya sa Mahaifina ya damƙi hannuna mara ciwon sannan ya yi min raɗa a kunne da cewar, "Ɗaure bakinki ya fi miki alheri akan mummunan fushin da abar bauta za ta yi da ke." Idanuwana na ɗago ina kallonsa, har ƙwayar idona ta ciko da ƙwallah sai na haɗiye abina don na tuna gargaɗin da mahaifina ya yi min akan

zubar ƙwallata. Muryata na rawa na furta, "Ina gudun abin da zai faru da Kandala don ka san tsarinmu ba zai taɓa tasiri a tattare da ita ba. Ta kasance bata daga jinin Maharba da mafarauta, idan baka manta ba da bakinka ka gaya min Abar bauta ta tsarkake iya zuri'ar wannan yankin namu ne kawai, ka na ganin idan wani abu ya faru da Kandala zunubi da munanan abubuwa ba za su ƙaru a kaina ba duba da abubuwan da suke faruwa da ni? Na yi sanadiyar mutuwar iyayenta, kuma tun da dokar dajin na lashi aniyar kare haƙƙinta kamar yadda iyayenta za su kula da ita. Don Allah kada ka dakatar da ni saboda ina tausayin rayuwarta, ta rasa iyayenta a yankinmu, ta rasa zuri'arta a yankinmu, ta rasa budurcinta a yankinmu shin wannan kaɗai bai isa ya sa a tausayawa rayuwarta ba?" Jikin mahaifina ne ya yi sanyi tamkar wanda aka zare wa laka, ya dube ni haɗe da sauke ajiyar zuciya sannan ya furta, "Shi kenan Kyauta! Abar bauta ta kawar da muguwar rana a kan ki, za ta shiga lamuranki ba za ta da mu kunya ba albarkacin tsafi da farauta." Jin daɗin kalamansa ya sa na sakar masa murmushi a daidai lokacin na ji Abar bauta ta sake cewa, "A daren yau zuwa gobe za a katange yankin nan daga baƙar guguwar da ta taso mana. Ya zama wajibi a zubar da jini ga rauhanai don su sake dafa mana akan sha'anin rayuwarmu, wannan shi ne abin da zan iya sanar da ku don na taimaka muku. Idan kuka bijirewa umarnina zan iya sauya sheƙa daga wannan yankin zuwa wani na kafa daulata, munanan abubuwa za su yi ta faruwa a kan ku haɗe da farmakai daga sauran ƙasashe musamman Baƙar Daular da kullin burinta ta shafe tarihin Maharba a faɗin duniya." Cikin aminta da kalaman abar bauta da ba ta yarda ya sa muka amsa mata da faɗin, "Uwar gijiya abar bauta ta dafa mana ta shafe matsalolinmu, mun dogara da ke don haka ke ce mai yaye mana damuwa da ba mu waraka a kowanne lokaci. Mun ji mun amince za mu yi abin da kika ce domin mu ma su bin umarninki ne, mun dogara da tsafi da sihiri sune madogarar abar bauta ita kuma ita ce madogararmu a koyaushe."

Fuskar abar bauta ce ta fasalta irin farincikin da ta yi da mu, don haka ta ɗaga hannunta sama ta wara ƴan yatsunta nan take wani mulmulallan haske ya dira a kai. Ta dube mu ta sake kallon haske sannan ta furta, "Albarkacin tsafi da sihiri, albarka da tabbata a gare ku ya ku wannan zuri'a ta mafarauta masu albarka. Shin akwai mai son a bincika gobensa don sanin abin da zai faru da shi? Akwai mai ciwo mu warkar da shi? Ko akwai mai son mu ninka nasara da tsaririn tsafinsa don ya gagari kowanne rauhani a dajin farauta?" Tun bata rufe baki ba mahaifina ya ɗaga hannu sama, kasancewar mahaifina sarkin Maharbin yankinmu ya sa mutanen garinmu suke matuƙar ba shi girma domin mutum ne mai adalci da son talakawansa. Ganin mahaifina ya yi magana ya sa alummar da ke wurin suka fara  kai masa gaisuwa cikin girmamawa, "Sarki ya zo mutuwa ta zo, mutuwa mai kai ƴan maza ƙasa ko da son rai ko babu. Abar bauta ta riga da ta buɗa maka kwarankwatsa dubu sai ka gama lafiya amanar ƙauran garin Dume, amana ta kai mana amana ta kai maka mun baka amana ka ba mu gaskiya ko sun ƙi ko sun so sai mun bar wuya a dajin Gagarar maza. Sa'a dai maza sa'a dai uban dawa wuya mai sa ƙarar kwana ga ƙananun maharba uban dawa sai ya kai labari ko da daɗi ko babu." Sunkuyar da kai Mahaifina ya yi alamar gaisuwar tana kai masa sannan ya ɗago ya amsa musu da cewar, "Dawa dai mazaje! Ba kyau ba daɗi, idan wuya ta yi wuya yaro ke guduwa ya bar babansa. Kwarankwatsa dubu ranar Talata mai zuwa sai na kai hallitun dawa dubu biyar da ɗoriya ɗan butar uwa, Abar bauta ta buɗe mana dai." A hankali muka riƙa takawa har kan tudun tsira sannan mahaifina ya tura ni daga gabansa kaɗan ya fara yi mata magana."Abar bauta ta yafe min kada ta yi fushi da

ni a yau ma na sake dawowa da 'yata Kyauta domin ta shiga lamuranta. Ɓoyayyun al'amura na sake bayyana a tattare da ita, don haka na sake dawowa da ita don na ji ko akwai wani taimako da Abar bauta za ta yi domin Kyauta ta rinƙa rayuwa kamar kowa." Daga can duhu-duhun wurin da mutane ke tsaitsaye na hango wani matashin saurayi yana ƙara kutso kai sakamakon jin bayanin da Mahaifina ya yi, muna haɗa ido ya sakar mini murmushin da ban san dalilinsa ba, sai dai abin da ya ɗaure min kai ba kasafai na cika tozali da matashin ba sai a ranaku makamantan waɗannan da muke kai wa Abar bauta kukanmu.Hasali ko kaɗan ba ya daga cikin zuri'armu domin gabaɗaya mun san kanmu waɗanda suke rayuwa a yankin. Ina cikin wannan tunanin na riski muryarta tana faɗin, "Akwai ɓoyayyun lammura game da Kyauta don haka nake gagara bincika abin da yake damunta, a duk lokacin da na bincika gobenta ba na samun biyan buƙatata. A duk faɗin yankin nan babu wanda zan bincika rayuwarsa ta gaba na samu tangarda sai Kyauta, ina mai yi maka albishir da cewa ita ɗin ta musamman ce don haka waɗansu abubuwa suke baƙuntar rayuwarta. Babban abin da za mu saka a gaba shi ne, mu mayar da hankali wurin zagaye garin nan domin idan muka zagaye gari na yi ammana da tsafi da sihiri babu abin da za same mu." Wurin ne ya yi tsit muna sauraron ci gaban bayanin da abar bauta take. Sai da ta sake hawa can ƙololuwar samman tsauninta sannan ta ci gaba da cewa, "Albarkacin ranar talata da nasarorin da ke cikinta muna miƙa wuya ga alƙaluman tsafi akan zan sanar da talakawa su nemi waɗannan kayan tsarin su aiwatar da shi domin neman warakar su. Da farko za ku saro kan wani ƙasurgumin kumurcin maciji da ke Dajin Bawaya, sai ku kawo min na jiƙa shi da ruwan sihiri haɗe da tumfafiya, idan ya kwana ɗaya a jiƙe sai a dake kan macijin ku samo mana ruwan kogin haladu a wanke idon matasan makafi a haɗa da ƙasar kabarin Jarumi Baushe uban Yaɗiya, idan kuka yi haka ku kawo min na haɗa sauran mahaɗin da kaina. Zan baku shi ku je ku zagaye garin nan da shi kuma duk abin da za ku gani kada baki ya furta ko zuciya ta tsorata, duka waɗannan abubuwan za a same su ne a cikin ƙasa da kwana biyu." Duk da zuciyoyinmu sun fara karaya bai hana mun amsawa abar bauta ba, tana gama jawabin ta dafa raunin da ke jikina haɗe da ɗaura min wata baƙar fata wacce da alama ta baƙar wahainiya ce. Nan take raunin jikina ya warke wani ƙarfi ya ratsa ni tamkar wani abu bai taɓa faruwa da ni ba, daga haka ta sallame mu sannan kowa ya watse gidansa.

Sannu a hankali na rinƙa waige-waige don ganin na lalaubo matashin da nake ɗora zargi a kansa, amma sai haƙana ya gagara cim ma ruwa. Na neme shi sama da ƙasa na rasa! Dama na san za a rina wai an saci zanin mahaukaciya. A duk lokacin da na yi tozali da shi haka ce take faruwa don haka nake tunanin yana tattare da mummunar manufa game da yankinmu. Saboda na tabbata banza ba ta kai zomo kasuwa, kuma tamkar wanda yake wa rufa ido ban taɓa ji wani ya yi magana ko ƙorafi akansa ba. Kasancewar ba a ranar na saba ganin hallitun da ƴan uwana ba sa iya ganinsu ba ya sa na ja bakina na yi shiru, amma haka kawai jikina ya ba ni ziyararsa a gare mu ba alheri ba ce.

Matashin saurayin na barin wurin kai tsaye ya bi ta wata ɓarauniyar hanya da ke ƙarƙashin ƙasa, cike da fargaba ya rinƙa falfala gudu don yana tsoron tonuwar asirinsa musamman da ya tuna irin kallon zargin da Kyauta take yi masa. Sai da ya yi gudu mai nisa sannan ya isa wurin wasu rundunar dakarun mayaƙa, haki yake yi kamar ransa zai fita sannan ya sanar da su duk abin da ya ji game da yankin su Kyauta sannan ya ɗora da cewa, "Matsala dai ɗaya ce kamar

yadda na gaya muku a baya, duk lokacin da na shiga yankin nan ba na iya ganin kowacce halita da idona face manyan dabbobi da ƙanana. Da taimkon Shugaba Usaina ta ba ni wani laƙani shi ne nake iya ganin yarinya ɗaya da idanuna kuma nake iya jin sautin abin bautarsu, ita ma a yadda na lura tana ganina sai dai ina tsoron kar asirinmu ya tonu." Shugaban Dakarun ne ya bushe da dariyar ƙeta sannan ya furta, "Ka gama aikinka don haka za ka iya tafiya ga Daularmu mai albarka, na tabbata idan muka kai wa Sarki wannan zuri'a ta Maharba sai ya yi mana ƙarin girma ya ɗaukaka darajarmu.

Runtse idonsa matashin ya yi tare da faɗin, "Shugaba Usaina! Shugaba Usaina." Nan take wani haske ya mamaye wurin babu jimawa ya ɓace ɓat. Gurfane yake a gabanta yana sauraron abin da za ta faɗa, sanin faɗin rai da izzarta ya sa ya ƙagara har ya ɗago don a tunaninsa ko ta bar wurin bai sani ba. Suna haɗa ido ya sauke kansa ƙa sa cikin girmamawa ya furta, "Sha kundum ta dafawa aikinki." Miƙewa ta yi ta fara taku ɗaiɗai ta rinƙa zagaye shi sannan ta furta, "Na saurari bayaninka don haka ina mai umartarka da ka iya bakinka idan ba haka ba sai na fisge rai daga gangar jikinka. Tabbas Boka mai zamani ya yi gaskiya Sha kundum ta sake bayyana a wannan yankin da kake min leƙen asiri sai dai babbar matsalar da har yau ya gagara bayyanar da suffar yarinyar. In dai ina numfashi Sarki Damina ba zai taɓa samun cikar burinsa na jininsa ya gaji karagar mulkinsa ba, na yi rantsuwa da abar bauta sai dai zuri'arsa ta ƙare a wahale yana ji yana gani zan gina Daular nan da jinin da ba na shi ba." Ta kai ƙarshen maganarta a tsawace kamar wacce aka ɓata wa rai, a razane matashin ya gyaɗa kai yana shirin sake magana ta katse shi da cewar, "Fitar da sirrina tamkar ka sanya takobi ka datse rayuwar da kake ciki ne, ka kiyaye idan ba haka ba wankin hula zai iya kai ka dare." Godiya ya yi mata sannan ya tashi zai fita ta sake katse shi da cewar, "Ka tabbatar da ka bawa yarima mugunyar ruwan sihiri a daren nan kafin wayewar gari." Amsa mata ya yi cikin ladabi sannan ya fice daga ɓangarenta.

Dare ne ya tsala sosai ban da kukan tsuntsaye da na ƙananan dabbobi babu abin da yake tashi, cikin sanɗa da ɓadda-bami take tafiya a hankali tana waige don kar wani ya ganta har ya fahimci abin da yake tafe da ita. Kamar yadda ta saba a duk daren da take neman biyan buƙatarta haka ta tunkari tsaunin Boka Mai zamani, kamar yadda ya ga zuwanta a cikin ƙoramar sihirinsa haka ya ji takunta zuwa kogon dutsensa. Tun daga bakin ƙofa Boka Mai zamani ya rungume ta a yunƙurinsa na son su fara aikata masha'arsu kamar yadda suka saba duk lokacin da ta ziyarce shi, a hankali ta zame shi daga jikinta tana faɗin, "Sha kundum ta ci gaba da rufa mana asiri dangane da ɓarnar da muke aikatawa Sarki Damina." Boka mai zamani ya bushe da mahaukaciyar dariya sannan ya furta, "Wane mutum In ji mutuwa shalelena? Asirinmu ba zai taɓa tonuwa ba don ba na jin wancan sakaran zai iya kusanto da Sha kundum cikin wannan Daular, hasalima rashinta tare da mu shi ne mafi alheri domin na tabbata idan tana yankin nan asirinmu ya gama tonuwa. Yanzu dai ya kamata a baiwa kura ajiyarta." Takawa ta fara yi a hankali tana zame ganyen da ke jikinta daga wanda ya rufe al'aurarta har zuwa na ƙirjinta sannan ta furta, "Ranar biyan buƙata rai ba a bakin komai ya ke ba mudubina. Indai wannan ne ai ta kwana gidan sauƙi jariri a ɗakin mayya. Amma abin da yake tafe da ni bai wuce kan maganar wancan sakaran Yariman ba, shin maganar da na ji Sarki ya faɗa gaskiya ne zai iya warkewa? Saboda ina ɗagawa Sarki Damina ƙafa ne don na san a halin da yarima yake ba

zai iya mulkar Daular nan ba." Boka mai zamani ya ƙarasa wurinta yana yawo da hannunsa a sassan jikinta sannan ya furta, "Tabbas a bincikena matuƙar Sha kundum ta bayyana a Daular nan zai iya warke wa amma da sharaɗin sai an bankaɗo sirrin da ba kowa ne ya sani ba kuma ba kowa ne zai gan shi ba. Mai wannan ikon yanzu haka ta bar duniya, Mai babbar Turaka ita ce ta san da wannan ɓoyayyan sirrin wanda ko da Sha kundum ba ta dawo daular nan ba matuƙar aka bankaɗo shi Yarima zai warke, yanzu haka gawar Mai babbar turaka na ɗakin yarima na kashe ta ne a lokacin da take ƙoƙarin sanarwa da Yarima sirrin ɓoyen da bankaɗe shi ba alheri ba ne a game da ke, ni kuma duk abin da zai muzanta shi zan iya kawar da shi. Sarki Damina yana kallonki a matsayin mahaifiyar Yarima alhalin Hasana ita ce Mahaifiyarsa kece Usainarta, Ko kin san har gobe Mahaifiyar Yarima tana raye a faɗin duniyar nan? Ko kin san Yarima ba shi kaɗai ne Ɗan da Sarki Damina ya mallaka ba? Ko kin san ƴaƴan Sarki Damina Uku ne a faɗin duniya? Idan bacci kike ki farka domin a duk lokacin da Damina ya gano kece kika nemi salwantar da rayuwar yarima da mahaifiyarsa na tabbata kashinki ya bushe. Ki yi duk abin da za ki yi ki nemo tagwayen jarirai ki kawo min domin na cika miki wani aiki da su idan ba haka ba komai zai iya faruwa, kuma ki tabbata jariran sun fito daga cikin jinin Maharba domin har gobe jininsu na tasiri akanmu tun da sune suka yi galaba a kan mu a lokacin da mummunan al'amari ya faru da Sarauniya Shakundum." Jakadiya da tun shigar Mai ɗakin Sarkin Damuna take laɓe a ƙofa ta riƙe bakin cikin mamaki, a hankali ta furta, "Tabbas Usaina ta cika tattaciyar marar imani amma na yi rantsuwa da Sarauniya Sha kundum da mulkinta sai kwaɓarta ta yi ruwa, a kullin fata da burina bai wuce Sarki Damina ya auri Jummai don na tabbata ko da tsiya da azziki sai Jummai ta haihu a gidansa. Jakadiya bata ƙarasa wannan tunanin ba ta hango harshen wutar itace kafin ta yi wani yunƙuri Bayin Sarki Damina suka haske ta da shi, a tsawace babban bawansa ya furta, "Jakadiya Lami me kike yi a wurin Boka mai zamani a talatainin tsohon daren nan duba da kin san haramun ne matuƙar ba a sanar da Sarki Damina wannan ziyarar ba?" Daga cikin kogon dutsen cikin Boka mai zamani da Usaina mai ɗakinsa ne ya kaɗa, nan take zufa ta fara keto musu cikin faɗuwar gaba ta furta, "Halaka ta zo mini matuƙar Sarki Damina ya san da ni a kogon dutsen nan." Kafin boka mai zamani ya yi magana daga cikin rijiyar da gunkin Sarauniya Sha kundum take suka ji wata irin tsawa wacce ta haddasa razanar Jakadiya ta faɗo cikin kogon dutse a hargitse. Ganin haka ya sa Sarki Damina da Fadawansa suka rufa mata baya, don ya kawo ziyarar cikin dare ne sakamakon mummunan mafarkin da ya yi akan Yarima da wata matashiyar buduwa mai ɗauke da kwari da baka a hannunwanta."

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Ƙirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko

yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

Free page 5

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰 ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

Daga wurin Abar bauta kowannenmu gida ya zarce don ɗauko makamai da kayan shiga farauta, sai da muka ƙara tsare kanmu da magunguna sannan muka fita wajen gari a daidai matsayar da Mahaifina ya sanar da jama'a za a haɗu domin ya rarraba wuraren da za a tunkara. Ilahirin mutanen da ke wurin maza ne sai mata biyu daga ni sai Dela wacce ta kasance ƙawa ce a wurina kuma aminiya, ta kasance ƙanwar saurayina Goga kuma duk farautar da muke fita kusan tare muke fita. Goha na ganina ya ƙaraso wurina haɗe da kara gorarsa jikin tawa yana faɗin, "Dawa dai Sarauniyar kyawawa, ko yau ko gobe sai daji ya buɗa miki a lokacin farauta." Cikin so da ƙauna na mayar masa da martanin murmushi haɗe faɗin, "Sa'a dai jarumina Abar bauta ta tsarkake duk wuya duk daɗi sai ka kai labari."

Lokacin da muka gama taruwa a wurin Muzuru uban balbela ne ya fara busa ƙaho nan take wurin ya ɗauka haɗe da bushe-bushen hayaƙin magani. Mahaifina ne ya ɗaga gorarsa sama nan take wurin ya yi tsita kowa yana sauraron abin da zai faɗa. Sai da ya kalle mu ɗaya bayan ɗaya sannan ya furta, "Gaisuwa ga zuri'ar Maharba an buga da ku an bar ku. A daka a kirɓa sai gwaza maza kuke gumbar dutse kowar ja da ku na yarje muku ɗan butar nan ku kai shi ƙasa ko da Ubanai yake yawo, wuya a dajin gudundu wuya a hanyar gwiɓau wuya a artabun baƙin daji wuya a ƙasurgumin dajin farautar gumurzin maciji aradu ko wuya ko daɗi sai mun saro kansa don bin umarnin abar bauta." Yana gama maganar cikin haɗin baki muka furta, "A lafiya mazaje sai kai hayaƙi mai sanya hawaye a idanun jama'a ko maza ko mata, sa'a dai cau cau cau Abar bauta ta buɗa mana." Murmushi ya yi ya karyo ganyen ƙafar shamuwa ya murtsuka a cikin wani ƙaton daro wanda yake cike da ruwa. Sannan ya ciro wata ƙanƙanuwar layar da ke wuyansa ya tsoma ta a ciki ya cire, ya fara karanta waɗansu alƙaluman tsafi sannan ya tofa a ciki. Ɗaya bayan ɗaya haka ya riƙa ba mu muna muka sha sannan ya rarraba mu gabas, yamma, kudu da arewa. Mahaifina ne ya fara kukan kura ya wuce gaba sannan mu da karnukanmu muka rufa masa baya kowa ya bi hanyar da aka ba shi umarni ya bi, take ƙura ta turnuƙe wurin cike da rashin tsoro muka tunkari dajin Bawaya dajin da ko mahaifina ya sha ba ni labarin hatsari da sarƙaƙiyar da ke cikinsa. A tarihin garinmu tun kafuwar dajin ba a taɓa samun mutumin da ya shiga dajin ya dawo da ransa ba, hasali duk irin tasirin farautarmu mahaifina ya ba ni labari sama da shekara talatin kenan babu wanda ya taɓa saka ƙafarsa cikin dajin da sunan farauta saboda Abar bauta ta dakatar da shiga dajin, har sai a wannan ranar da ta bayar da umarni farautar macijin.

A lokacin da muka nutsa dajin mun yi tafiya mai nisa muna cin karo da manya da ƙananan dabbobi, tun muna tafiya da yawanmu har ta kai ga mun rarrabu kowanne ya yi hanyarsa, sai ya rage daga ni sai Nalami autan kunkuru muka ci gaba da nutsawa cikin ƙasurgumin dajin. Haka kawai na ji kaina na sarawa tsigar jikina na tashi yanayin da bai taɓa riskata ba, ga wani irin jiri da yake ɗaukata lokaci-lokaci. A hankali na dafa wata baƙar bishiya haɗe da jingina kaina a jiki saboda yanayin da nake ji ga wani irin sara da nake ji a duk gaɓɓan jikina, Nalami ne ya ƙaraso wurina cikin ƙarfafa gwiwa ya furta min, "Zuri'ar Maharba bata daga cikin raunana don haka babu namin dajin da zai yi galaba akan ki albarkacin tsafi da Abar bauta." A hankali na yunƙura ina faɗin, "Nalami jikina yana ba ni wannan shi ne dajin Bawaya dajin da za mu yi baƙin artabu da hatsabibin macijin nan." Waige-waige ya fara yi hannunsa riƙe da itace mai ɗauke da harshen wuta ya fara haskawa. Garin ganyen idon rana ya kunto daga ƙugunsa sannan ya fara turarashi, sannu a hankali muka fara ganin wata irin walƙiya haɗe da mummunan gurnani mai tarwatsa zuciyar ƙananan jarumai. Miƙe wa na yi a hankali na ƙara ƙwarara gwiwata sannan na ci gaba da baza kunnuwana don jin daga wurin da macijin zai bayyana. Daga gefen da na tashi na ji abu na motsi nan take muka ƙurawa wurin ido, wani abin tsoro a tunaninmu a jikin bishiya muke ashe girman macijin ne ya yi tamkar wata murgujejiyar bishiyar kuka. Baya muka fara yi sai da muka matsa sosai na hangi wata sarƙar zinare da tagulla a wuyansa, idanunsa na fitar da wani hasken kaɗan-kaɗan. Nalami ne ya kwarara ihu nan take dajin ya amsa, ya zabura a guje da niyyar tunkarar macijin gadan-gadan. Da sauri na riƙe shi muna haɗa ido na furta masa, "Ba a gaggawar gasgata ɗan ɓarawo har sai an jarraba shi. Ba ta haka za mu ɓullo masa ba

dole sai mun yi takatsantsan." Gyaɗa min kai ya yi a hankali muka zaro bindigarmu, muka saita shi sai dai wani abin mamaki nan take bindigar ta fara fidda farin hayaƙi. Daga can bayana na fara jiyo ihun wata mace, sosai na kasa kunnena duk da ina gaban baƙin macijin da koyaushe zai iya hallaka mu. A hankali na riƙa ja da baya ina bin hanyar da na ji sautin wannan matar yana tashi, ƙarasawata bakin wani ɗan kogo ya sa na fahimci daga wannan wurin sautin yake fitowa. Leƙa wa na yi ina zura harshen wutar don haska abin da yake ciki, nan take na ci karo da wata mace mai tsoron ciki wacce da alama naƙuda ce ta taso mata gadan-gadan. Kallon tuhuma na bita da shi a lokacin da ta ɗago hannun tana miƙo min alamar na taimaka mata, garin ƙafar rauhanai na ɗauko na turara don na tabbatar da mutum ce ko kuwa iska ce take son cutar da ni. Wannan garin mahaifina ya samu laƙaninsa a wurin Mahaifinsa yana taimakawa wurin farauta a duk lokacin da kake kokwanto kasancewar hallita. Ganin bata ɓace ba ya sa na kutsa kaina ciki na tsugunna a wurinta ina faɗin, "Ga ki jinsin mutum amma meye ya kawo ki wannan baƙin dajin da tsohon cikinki?" Kamar kurma haka ta rikice tana kuka ta rungumo ni jikinta tana shafa ni, ban fahimci abin da take nufi ba don haka na buɗe baki zan yi mata magana na ji ta riƙe ni sosai ban yi aune ba na ji kukan jariri ya ratsa kunnuwana, ajiyar zuciya ta sauke ta ɗago jaririn haɗe da saka wani fiƙaƙƙan itace ta yanke masa cibiya. Ganyen fatar da ke kare da gefen ƙirjina na ciro na miƙa mata ta naɗe jaririn da shi, ta ɗago ta kafe ni da idanunta ganin haka ya sa na yunƙura zan miƙe na ji ta ruƙo hannuna. Sai kawai ta fashe da kuka tana faɗin, "Albarkacin Sha kundum ki taimaka ki karɓi jaririn nan saboda kin kasance daga cikin masu sa'a, a ƙallah na shafe sama da shekara ashirin da biyar a cikin baƙin dajin nan ban taɓa ganin wani mahaluki ya shigo shi ba.  Sha kundum ta yanke mini baƙar wahalar da na jima ina sha ga shi har zuwanki ya zame min waraka, ni kam na san tawa ta ƙare amma ki taimaka ki ɗaukar min alƙawarin kula da jaririn nan kuma ki min alƙawarin za ki sada shi da wata Daula mai cike da sarƙaƙiya da rikitattun al'amura. Ki yi min alƙawarin duk daren daɗewa za ki sada shi da mahaifinsa idan har yana raye, duk wani ƙarin haske zan baki dange da waye mahaifinsa domin kafin zuwana nan mahaifinsa shi yake mulkar Daular bakiɗaya. Kamar yadda ƴar uwata ta gaya min ga shi yau ya tabbata, ta saka boka ya aiko rauhanai sun kawo ni nan ne domin biyan buƙatar kanta. An kawo ni nan an tsaface ni ta yadda ba zan taɓa haifar abin cikina ba har sai ranar da wani jinsin bil'adam ya kawo ziyara wurin nan. Ta alƙarwarta min za ta auri mijin kuma za ta salwantar da rayuwar yarima, don ta gaya min koda wani ya shigo wurin nan ba zai taɓa ɗauka ni mutum ba ce duba da dajin nan yana da kamanceceniya da dajin ƙare kukanka. Sai ga shi yau na haife cikin da ya shafe shekara sama da ashirin da biyar a jiki, tabbas wuya bata kisa kuma na amince Maharba na da farar zuciya domin da mutanen yankina ne sai dai su kashe ni su zari abin da yake cikina."Jikina ne ya yi sanyi da jin kalamanta, na dube ta cike da tausayawa na furta, "Ki taso ki biyo ni na yi alƙawari zan taimaka miki. Amma ba zan tafi da jaririnki ba domin ni ma wani aiki ne a gabana na sarar kan macijin da ke cikin dajin nan." A madadin ta amsa mini na sai na ga ta saki murmushi tana faɗin, "Sara da makami ba zai taɓa baki nasarar kashe macijin can ba, ki ɗebi ciyawar tukunyar maƙiya ki murje a hannunki da shi, sannan ki shafe duka jikinki sai ki saka ƙwara uku a baki ki tauna ki tunkare shi cikin jarumta ki tabbatar da kin kai kansa doron ƙasa, domin wannan ne kaɗai makarin ruhinsa shi kenan za ki yi nasara akansa." Da mamaki na dube ta na furta, "Ya aka kika san haka?" Ta rungume jaririnta haɗe da bashi mama ya kama yana sha sannan ta furta, "Shekara ashirin da biyar a dokar dajin nan ba wata ashirin da biyar ko makwanni ashirin da biyar ba ne. Ki yarda da

ni ba zan cutar da ke ba kuma ki yi min alƙawarin za ki kula min da yarona har ki kai min shi mahaifarsa." Tana rufe bakinta na ji ihun Nalami don haka a gaggauce na amsa mata da na amince na fice daga cikin kogon, a kwance na same shi shame-shame cikin azaba. Yana jin na taɓa shi ya furta, "Kar ki wahalar da kan ki a kaina mutuwa zan yi Kyauta, maza hanzarta ki kare kan ki kada a yi biyu babu." Magungunan saran macijin da ke ɗaure a ƙuguna na kunto ina saka masa amma babu wanda ya yi aiki, ina shirin kun ce wani na ji ya riƙe hannuna yana faɗin, "Wannan ba kamar sauran macizan da kika sani ba ne, ki bar wahalar da kan ki tawa ta zo ƙarshe. Sa'a ta kai miki abar bauta ta baki nasara akan wannan macijin cau cau cau mai gayya mai aiki." Hawaye ne ya zubo min a hankali na furta, "Jarumi uban yaɗiya ya amshi ziyararka, dawa ba daɗi a dajin Bawaya." Ina ji ina gami numfashin Nalami ya ɗauke, gurnanin macijin ne ya sake ankarar da ni don haka na miƙe da sauri na fara lalubar ciyawar da matar nan ta faɗa min, dama na santa a ido sai dai ban san laƙanin da ta sanar da ni ba. Na jima ina abu ɗaya har muka fara wasan ɓuya da macijin yana watso min dafinsa ina kaucewa. Har na fara fidda rai sannan na hangi ciyawar a saman wani shuri, da sauri na dira a kan shurin nan take ya rushe na tsinki ciyawar na murjeta na fara shafe jikina.

Kai tsaye na tunkari macijin ya fara ja da baya ganin yana shirin guduwa ya sa na tafi da gudu na damƙi jikinsa, laushi ya fara yi da sauri na ɗare samansa ya tura kansa a doron ƙasa nan take ya faɗi matacce. Takobin da ke rataye da ni na zaro ba a ɗauki lokaci ba na datse kansa, na sakala takobina ta cikin ƙwayar idonsa na fara jan kan da karfi don nauyin kansa ya kusa girmana a a tsaye. Bakin kogon na ƙarasa sai dai wani abin mamaki na nemi matar sama ko ƙasa na rasa sai jaririnta da ke gefe yana mutsu-mutsu ga wata azurfa a kan cikinsa da wata ƙaramar aska. Daga wurin ƙafafuwansa wani ƙaton ganye ne da aka zuba wasu abubuwa da ban san na meye ba. A hankali na ƙarasa na ɗauki jaririn na rungume tare da kwaso kayan da ta ajiye masa, na fara jan kan macijin a wahale sannan na ɗauki hanyar da za ta sada ni da yankinmu.

Daular Sarki Damina.

Tun da boka mai zamani ya ji muryar babban bawa sarki Damina da sauri ya sanyar jelar dokin hannunsa a cikin sihirtacciyar ƙorama ya yarfawa Usaina ruwan, nan take ta ɓace daga wurin. Shigar Jakadiya ya sa Boka mai zamani ya buga mata tsawa don ya tabbata ta ji duk irin tattaunawar da suke yi, a madadin Jadiya Lami ta razana sai ta rushe da matsanancin kuka tana birgima haɗe da dafa ƙafafuwan boka mai zamani. Mamaki ne ya kama shi matuƙa don haka ya zura mata ido yana shirin magana, sarki Damina ya kutso kai cikin kogon dutsen. Shigar su ke da wuya rijiyar ta sake sakin wata razananniyar tsawa wacce ta sake ba wa boka mai zamani tsananin mamaki, don rabonta da yin haka tun lokacin da yake yaƙinin an sake haihuwar Yar sarki Damina ta uku wacce tankasance macce. Sarki Damina ne ya buga wa Jakadiya Lami tsawa yana faɗin, "Me kike yi a wurin nan da tsohon daren nan?" Jakadiya Lami ta sake rarrafawa gaban Sarki Damina ta lashi ƙafafuwansa sannan ta furta, "Wani kyakkyawan mafarki na yi game da yarima don haka na garzayo wurin Boka mai zamani da ya fassara min mafarkina da farar safiya na yi maka albishir da shi, kawai ina sako kaina na ji yana magana da Aljanu yana cewa Mai babbar turaka kwana ya ƙare." Babu alamun tausayi ko mamaki Sarki

Damina ya dubi Boka mai zamani ya ce, "Wai haka ne?" Cike da rashin gaskiya Boka mai zamani ya fara gyaɗa kai. Sarki Damina a tsawace ya ce, "Idan haka ne mai ya sa baki same ni da maganar ba? Shin ba zunubi ba ne zuwa kogon boka mai zamani matuƙar ba da izininmu ba?" Tuni jikin Jakadiya ya fara rawa amma sai ta dake ta furta, "Na yi mafarki Yarima ya warke har ya yi aure matarsa ta haifo jariri namiji, wani ƙarin farinciki jaririn da yarima yake haifa har gani na yi ya zama nagartaccen jarumi yana kai maza ƙasa." Nan take sarki Damina ya faɗaɗa fara'arsa sannan ya nuna wa Jakadiya hanya ya ce ta fice, Jakadiya cike da mamaki ta fita don jin kunnenta ta ji muryar Usaina sai dai da shigar ta ba ta ganta ba kuma ta tabbata boka mai zamani ne ya yi wani abin da ta ɓace.

Mafarkin da Sarki Damina ya yi ya ga Yarima rungume da jariri ga wata matashiyar mace hannunta riƙe da kwari da baka ta saita shi ta sakar masa shi ya faɗi jini na zuba. Ko da Boka ya gama jin jawabin Sarki Damina sai ya ƙarasa bakin rijiyar ya leƙa cikinta. Wani abu da ya ba shi mamaki inuwar jariri ya gani rungume a hannun wata mai saƙale da kwari da baka. Wannan lamarin ya sake susuta tunaninsa a sanyaye ya juyo ya furta, "Ina buƙatar a bar ni na yi nazari zuwa wayewar gari idan lamarin ya gagare ni sai na nemi agajin Abar bauta." Saboda takaici Sarki Damina ko amsa bai ba wa Boka ba ya fice daga kogon dutsen." Sai da ya tabbatar da sun yi nisa da fita sannan ya sake saka jelar dokin ya yarfa a wurin da Usaina take tsaye, nan take ta bayyana tana sakin shu'umin murmushi. Boka mai zamani cikin damuwa ya furta, "Baya ta haihu fa." Usaina ta fara wata irin tafiya tana karkaɗa jiki ta ce, "Da aka yi yaya hatsabibina?"

"Hallaka na sake kusanto ki da ni domin a yanzu haka ƴar uwarki ta sauka kuma da alama jariri namiji ta haifa, ni na sani dama zuri'ar Maharba ba za su taɓa ƙyale mu wataya ba. Sun karya makarin asirinmu akanta kuma alamu sun nuna yaron na tare da zuri'arsu. Ƴaƴan Sarki Damina huɗu kenan maza uku mace ɗaya. Biyu suna cikin masarauta biyu suna tare da zuri'ar Maharba. Matuƙar suka haɗu wuri ɗaya su huɗun daga nan ƙofofin nasarorinmu za su kulle." A hargitse Usaina ta dafe ƙirji tana faɗin, "Ka na nufin Hasana ta haife tayin cikin da ke jikinta? Bayan Yarima ka na nufin akwai wani jinin sarki Damina a Daular nan da ban sani ba?" Boka mai zamani ya bushe da dariya sannan ya furta, "Tabbas haske biyu nake gani a Daular nan wanda yake alamta jinin Damina ne, haske na farko Yarima ne Haske na biyu kuma da alama makusancinki ne kuma ya yi nesa da Damina tun da haka tauraronsu ya nuna min. Sai haske na uku da tun shekaru sha biyar na riske shi a zuri'ar maharba tare da hasken wannan jaririn da a yanzun nan na riske shi tare da su. Sai Hasana da haskenta ya dushe ba na iya ganin komai a kanta ban sani ba za ta kusanto nan ko kuma ajali ya risketa ya yin haihuwa oho? Abu ɗaya bincikena ya nuna min ta haife shi tana rayayya kuma baya tare da ita. To kin ga kenan dabara ta rage wa mai shiga rijiya."

Tirƙashi shin wane haske ne bayan jaririn hannun Kyauta tun da boka ya ce haske biyu ne a hannun maharba? Shin ina Hasanar Usaina ta nufa da ta bawa Kyauta jaririnta? Za su iya aiwatar da maganin kafin rundunar mayaƙan nan ta riske su ko kuma za su riske su? Ka da ku manta matashin nan fa ya sanar da su duk abin da yake faruwa a garin su Kyauta kun ga ba lallai su yi sanya ba? Tabbas labarin yanzu aka fara domin salonsa daban yake bayyana harsashenku ta sigar Commenta don mu ji me kike tsammanin. 💃

*Ummu Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Ƙirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

Free page 6

🥳 in ka ji busa tabbata Sarauniya ce ta ƙaraso, ina kuke matan ƙwarai, mata ba muna mata ba, shin kin jaraba kayan *HONEY-DROPS* me kike jira har yanzu?, Manyan mata, mata masu aji na ta dafifi wajen kwasar kayan gyara, me ya sa za ki kashe kanki da ƙuruciyarki, ko tsohuwar ma na zuwa karɓar nata, kina fama da matsalar bushewar gaba, ɗaukewar sha'awa da ni'ima, ƙaiƙayi ko ƙurajen gaba, jin zafi yayin tarawa da maigida, sanyi ya taɓa miki mahaifarki?, Kina ta allura da shan magunguna ba su miki aiki ba, wane kalar infection kike fama da shi?, Staphylococcus, Gonorrhea, Syphilis, UTI, STDs ne?, Share hawayenki kukanki ya ƙare je ki nemi *HONEY-DROPS INFECTION FLUSHER* ke da sanyi sai dai ki ba da labari, kin gama cacar kuɗi, cikin kwana uku zaki fitsarar da duk wani sanyi da dattin da ke tattare a mararki, ki gyara zamanki gidan aurenki don sanyi kashe mace yake har buzunta, duk wani magani da za ki sha muddin da sanyi a jikinki iyakar shi cikinki, ba zai sauka ba. Magani ne ingantacce made of herbs, In kin gama da wannan akwai na gyaran other room, akwai Exclusive Gumba ta manyan mata ke nan, ko matar Gwamna ita take sha, ga Gumbar babbar mace mai tada tsohuwar soyayya, akwai fa tsuumi na matan gaske, akwai *HONEY FLOOD TSUUMI* kan ƙiftawar ido ni'ima ta yi ta kwararo miki, akwai BUJENTA JAGAB, da Tsuumin Ɗafau, daga jin sunan kun san akwai zance na bar muku ku ƙarasa, akwai sauran kaya masu zafi🔥

Muna da bridal package

Diamond - 100k
Gold - 50k
Silver - 30k

Ga kuma na postpartum (wanda suka haihu don dawo da martabarsu)

Diamond - 50k

Gold - 30k
Silver - 15k

Kuna iya samun mu ta 08167888934, ko 08067770852

Ban tabbatar mun yi tafiya mai nisa ba sai da na ɗauki hanya don nufi cikin garinmu, sai dai tsawon tafiyar da galabaitar da na yi ne ya sa na yanke shawarar hutawa ga jaririn hannuna sai mutsu-mutsu yake wanda nake zargin yunwa yake ji. A bakin wata ƙorama na tsugunna na saka hannuna na rinƙa ɗebo ruwan ina bashi, bai sha da yawa ba hasali ma bacci na ga ya ci gaba da yi kamar ba shi yake mutsu-mutsu ba. Bakin wata bishiyar tsamiya wacce take maƙotaka da bishiyar kuka na koma na zauna don na huta, na rungume jaririn tare da kan baƙin macijin da nauyinsa yake wahaltar da gangar jiki da ruhina. Jingina kaina ke da wuya sama-sama na fara jin takun tafiya da haniniyar dawakai, ajiyar zuciya na sauke cike da fargaba don ina tsoron kada mummunan yanayin da nake fuskata ya raunatar da ruhina har na kasa kare rayuwar jaririn da na yi alƙawarin tsayawa kai da fata don kula da shi. A ɓangare guda ga mahaɗin maganin da zai ceto yankina wato macijin da ke tare da ni wanda rasa shi tamkar rushe yankinmu da bautar da mu a baƙar daular da zalincinta ya kewaye duniya. Ido na ƙurawa jaririn da ke bacci na sake matsa shi gam a jikina kamar wani zai ƙwace shi har sai da na ji yana motsi alamar matsewar da na yi masa ya takura. Harshen wutar itacen ce zame min fitila don haka na ɗago shi da hannuna ina haska wurin da nake tsammanin daga nan wurin motsin yake, ƙura ce ta garwaye wurin lokaci ɗaya dakarun suka zagaye ni kamar yadda suka saba a duk lokacin da suka ziyarce ni, ziyarar da take sabbaba mini karayar gangar jiki da ruhi har na kasa bambamce a wace duniyar na ke. A hankali ya fara takowa haye a kan dokinsa fuskarsa kamar kullin ɗauke da murmushi yana sake kusanto ni, sauka ya yi daga kan dokin ya ƙaraso wurina ya tsugunna. Idonsa ya kai kan jaririn hannuna take hantar cikina ta kaɗa duk da na san ba ni da ragonta a ɓangaren jarumta, amma ba zan yaudari kaina ba tun da na san sarkin yawa ya fi sarkin ƙarfi. Kafin ya yi wani yunƙuri na furta masa, "Wane ne kai? Kuma me ya sa kake ziyartata a lokacin da nake cike da ƙwarin gwiwa da cin alwashi? Me ya sa duk faɗin yankinmu ni kaɗai haka take faruwa da ni?" Sai da ya saki yalwataccan murmushi sannan ya furta, "Saboda ke ba irinsu ba ce. Ke zara ce a cikin taurari, kina rayuwa da jinin yanki biyu mafi alheri ga daula guda. Ki ba wa jaririn nan kulawar da ta da ce domin shi jininki ne, zuri'arki ne kuma danginki ne..." Tun bai ƙarasa ba na katse shi da furta, "Na kasance ɗaya daga cikin jinin maharba, mahaifiyarsa da bakinta ta ce min ita ba ta daga cikin ahalinmu ta yaya zai kasance dangina, ahalina kuma zuri'ata. A cikin dokar daji na haɗu da mahaifiyarsa yanzu haka ina fargabar yadda zan sanar da dangina wane ne shi da yadda na same shi ba tare da wata shaida ba, ka dubi girma da tsafin abar bauta kada ka sake hargitsa lissafin rayuwata ko ka nemi cutar da ni kamar yadda ka saba a..." Miƙewarsa ce ta katse ragowar maganata, sai da ya yi taku uku sannan ya juyo ya furta, "Na fi mahaifiyarsa sanin ainihin abin da ya faru a ɗaruruwan shekarun da suka gabata, ki yarda da ni ni mai ƙaunarki ne ba zan cutar da ke ba. Abu ɗaya na sani akwai wani mummunan lamari da zai faɗo rayuwarku nan ba da jimawa ba, dalilin haka zai sababba rikicewar al'amura da dama. Amma ina mai shawartarki a duk in da za ki tsinci kan ki; ki kasance mai juriya da jajircewa, da sannu za ki fahimci saƙona gare ki." Yana zuwa nan a zancensa kamar ɗauke war walƙiya haka suka ɓace min sama ko ƙasa.

Maganganunsa ne suka ci gaba da yi mini yawo a kwanyata, a hankali na yunƙura na fara jan kan macijin da ke gefena na rungume jaririna na ci gaba da tafiya. Sai da na yi tafiya mai nisa daga nesa na fara hango bukkokin garinmu, a wahalce na sauke ajiyar zuciya saboda sanyin farincikin da na ji. A lokacin da na ƙarasa wasu daga cikin dangina sun fara dawowa saboda tuni asuba ta yi haske ya fara ratsowa, mahaifiyata ce ta fara hango ni cike da murna ta tarbe ni nan take aka shiga iface-iface da samun nasarar da na yi. Lura da jaririn hannuna ya sa suka fara bi na da kallon zargi da tuhuma, a daidai lokacin mahaifina da zugarsa suka dawo sai dai a yadda na lura mun myi rashin maza da yawa. Ganin haka ya sa matan da suka ga babu mazajensu suka fara koke-koke da alhinin rashinsu. Mahaifina da sauran tawagar ne suka ɗauki kan macijin zuwa tsibirin abar bauta, ya yin da mahaifiyata ta ja hannuna har zuwa ɗaki ta fara jero mini jerin gwanon tambayoyi. Iya abin da na sani shi na sanar da ita, jiki a sanyaye ta yi wa jaririn wanka ta tatso nonon akuya ta bashi nan take ya hau sha. Tana gama shayar da shi muka tunkari tsibirin abar bauta sakamakon kiran gaggawar da ta aiko ana yi min, ta cikin mutane na riƙa kutsawa har na isa gare ta; ya yin da idanun mutane suka dawo kaina.

Kamar yadda badakaren ya rarraba su ɓangare daban-daban haka shi ma ya saɗaɗa ta wani lungu don yunƙurinsu na yi wa yankin ƙawanya, sai da suka zagayen yankin da sihirtaccan yashin baƙar daula mai karya kowanne irin tsafi da sihiri sannan suka bi ta hanyoyi daban-daban, kusan lokaci guda suka bayyana a lungu da saƙon garin kowannensu ɗauke da miyagun makamai wasunsu ɗauke manyan bulalai, ya yin fa wasunsu suke riƙe da manyan itatuwan da ake ɗaure bayi a jiki, dubannin jama'ar da suka hango a kan tsibirin ne ya tabbatar musu da sun dira a yankin da bawan nan yake yi musu leƙen asiri. Don haka suka yi kukan kura suka nufi wurin da niyyar su afka musu farad ɗaya, jin ihunsu ya fargar da su Kyauta nan take hankulansu ya tashi don kowannensu ya ajiye makamansa balle su yinƙurin kare kansu. Sai dai duk yadda suka kaiga yin amfani da layar ɓata ko shashatau haƙansu ya gagara cimma ruwa, don haka suka zage aka fara musayar ƙwanji.

Daular Sarki Damina.

Ajiyar zuciya Usaina ta sauke cike da damuwa da ƙuncin ta furta, "Tabbas akwai gagarumar matsala domin a kowanne lokacin kwaɓata na iya yin ruwa tsululu, zan fara binciken hasken da ke cikin Daular nan bayan Yarima idan har na gano shi tabbas sai na hallaka shi a ruwan sanyi, ba na ta Yarima dama tuni na rufe babin rayuwarsa tun da; da shi da matacce duk ɗaya suke a wurina. Sai wancan hasken da ya ɓulla cikin zuri'ar maharba shi ma dole na daƙile shi ya koma duhu, ka yi sani ya kai boka mai zamani koda zan rasa raina na yi rantsuwa da albarkar Sha kundum jinin Damina ba zai ƙara hawa kan karagar mulkin nan ba." Boka mai zamani ya janyota jikinsa yana ƙoƙarin biyan buƙatarsa sannan ya furta, "Mutum irinki na matuƙar burge ni, ƙwarin gwiwarki da dakiyar zuciyarki abin a yaba miki ne. Sai dai ki sani ko shi Damina bai taɓa sanin yana da wani ɗan bayan Yarima ba, shi wannan hasken ya fito daga jikin wata baiwarsa ne hatta ita kanta baiwar ba ta san ɗan da ta haifa jinin Damina ba ne. Lamarin akwai ɗaure kai amma zan taimaka miki domin cimma burinki tamkar cika nawa ne, yanzu dai mu bar wannan maganar ki zo ki ramawa kura aniyarta." Usaina bata musa masa ba don haka ta ci gaba da karye-karye cikin salo mai jan hankali, duk da kasancewarsa tsoho tukuf mai yawan shekaru bai

sa ya gagara nuna mata jarumtarsa ta nagartattun ƴan maza ba, ba su suka gama aikata masha'arsu ba sai gabannin asuba. Gudun kada gari ya waye asirinta ya tonu ya sa ta yunƙura za ta tafi, har ta je bakin ƙofa ta koma wurin Boka mai zamani tana faɗin, "Na manta da tukwicin ziyarata, ka ba ni wani abin mana don na faranta ran maigidana." Ɓata fuska Boka ya yi a daƙile ya furta, "Kada ki tunzura ni kishi ya hana ni baki sirrin mallaka, don na tabbata ko Damina bai kai ni kishinki ba." Fari ta yi masa da ido ba tare da ta furta komai ba, ya zura hannu cikin ƙoramar sihiri ya ɗauko jaririn kunkuru, sai da ya sakata ta kwanta ya ɗora kunkurun a cikin gabanta na ƴan sakanni. Sannan ya saka a cikin tashi al'aurar kamar yadda ya yi mata, ya samu dutsen wuta na sihiri aya ajiye jaririn kunkurun ya buga masa nan take ya dagargaje, hannu ya saka ya ɗauke shi ya zuba a cikin wata sihirtacciyar ƙwarya sannan ya tsiyaye mata ruwan a ƙanƙanuwar ƙwarya ya miƙa mata yana faɗin, "Ki tabbatar da kin ba wa Damina ya sha, kuma ki tabbata kin yi tsarki da shi kafin ki yi mu'amala da shi, da idonki za ki gani ba sai na baki labari ba." Cike da farinciki Usaina ta karɓa ta fice daga cikin kogon dutsen a sirrance ta wuce ɓangarenta ba tare da kowa ya ganta ba.

Gari na wayewa Sarki Damina ya saka aka ɗauko gawar Mai babbar turaka a lokacin har ta bushe ta sandare, lokacin da aka je ɗauko gawar Yarima na zaune ya haɗe kai da gwiwa. Ganin mutane ya sa ya tashi a haukace ya yi kansu yana ƙoƙarin yagar naman jikinsu, da ƙyar suka samu aka fita da ita sai dai daga dakarun da suka je ɗauko gawar babu wanda bai raunata ba. Da ƙyar da suɗin goshi suka samu suka maƙala masa sasari a ƙafa da hannu, don yadda suka lura da yanayin ciwon nashi ya fi na kullin tsanani. Saboda yadda ya karya ƙofofi da windunan ɗakin, a lokacin da ya kama ɗan yatsan hannun wani dogarin sai da ya cire shi daga tsintsiyar hannun. Wannan mummunan labarin ba ƙaramin ɗaga hankalin Sarki Damina ya yi ba, haka ya daure ya cije har aka kai masa gawar mai babbar turasa. Kamar yadda yake bisa al'ada duk macen da ta mutu a hannun yarima ko sarkin daular wannan na nuna gawarta za ta albarkaci daular da dodon tsafinsu, kuma ta kan iya zama matsala ga shi yarima ko sarkin da ta mutu a wurinsa. Ana kai wa Sarki gawar ya cire wasu daga cikin gaɓɓan jikinta domin a camfinsu matuƙar ba a yi wannan al'adar ba Yarima ko sarkin da ya yi silar mutuwarta zai yi mummunar mutuwa a hannun mace, wala matarsa ta aure ko macen shaƙatawa. Saboda duk ranar Alhamis sukan ware ta a zuwan ranar shaƙatawa tsakanin maza da mata, mahaifi idan ya yi sha'awar ƴarsa duk ƙarfin sha'awarsa sai dai ya bari sati ya zagayo. Ba abin kunya ba ne a wurinsu don uba ya yi wa ƴarsa ciki kamar yadda suke zube wa a filin da rana tsaka suke mu'amalarsu kowa na ganin ɗan uwansa. Ranar dama suna ware ta ne saboda irin haka shi ya sa suka yi wa ranar laƙabi da ranar nishaɗi. Kaifaffiyar wuƙa mai walƙiya aka ɗauko masa, tsirara aka yi wa gawar mai babar turawa aka kwantar da ita a kan tabarmar kaba, sannan aka ajiyewa Sarki Damina kujera mai ɗauke da siffar mutum a durƙushe alamar ƙasƙantar da kai wuyansa saƙale da kwari da baka. Bayan ya ɗauki wuƙar sai da ya kira sunan Sarauniya Sha kundum sau uku sannan ya sa wuƙar ya fara yankar maman mai babbar turaka, ya zuba su a cikin wani baƙin kasko wanda da alama bai taɓa ganin ruwa da sunan wankewa ba. Yana gama yanka ya buɗe bakinta da kyar ya yanki harshenta, daga haka ya daddatse dungulmin hannu da ƙafarta ya sake zuba wa a kaskon ya miƙawa uwar madafa. Jikinta na rawa ta karɓa ta wuce don gasa wa yarima ya cinye, daga haka aka ɗauki gawar mai babban ɗaki aka kaita ɗakin babban dodo bayan ya tsaface ta aka kaita ramin matattu. Babban rami ne aka tanade shi

domin zuba gawarwaki, duk wanda ya mutu a yankin can ake kai su matuƙar ba Sarki ne ya bayar da umarnin a ƙone shi ba.

Hankali a tashe mazanmu da mata suka shiga kiciniyar kare kan su sai dai tuni suke yi yunƙura cin mu da yaƙi, ganin haka ya sa Mahaifiyata ta miƙo min jaririn hannunta tare ta damƙa min hannun Kandala a cikin nawa ta furta, "Ki kula da su kamar yadda kika ɗauki alƙawari domin ina da yaƙini waɗannan sun fito daga cikin Baƙar Daula ne domin su farmake mu su bautar da mu, ba na son rayuwarki ta gurɓata a can ku bi yamma da gari domin ku tseratar da rayuwarku. Duk garin da kuka samu a gaba kada ku yi sanya ku yi ƙoƙarin ɗaukar al'adarsu matuƙar ba al'adar da abar bauta za ta yi fushi da ku ba ce." Hawaye na zuba na furta, "Kina ganin zan iya tafiya na bar kuna cikin wannan halin? Ba na son na rasa ku domin tafiyata tamkar rasa ahalina na maharba ne..." Ba rufe baki ba mahaifiyata ta hankaɗa ni cikin ƙaraji tana faɗin, "Tarayyarki da mu tamkar kasancewarki a baƙar daula ne, baƙar daular da gara kura da yi fata-fata da naman jikinka a kan kasancewar bawa a cikinta. Jikina yana ba ni maganar abar bauta ce za ta tabbata lokacin tarwatsewar  yankin nan ya zo." Ina ji ina gani na riƙe hannun Kandala ɗayan hannuna rungume da jariri muka nufi wata siririyar hanya da take da mahaɗa da tsibirin abar bauta. Lokacin da muka shiga siririyar hanyar kukan ƙananan yara da na masu matsakaicin shekaru suka ratsa dodon kunnena, ihun mahaifiyata da na ji ne ya sa ni gagara haƙuri har na leƙa kaina don ganin abin da yake faruwa, muna haɗa ido da ita na ga ta girgiza min kai alamar na tafi a daidai lokacin wasu manyan dakaru suka fara ɗaure hannuwan mutanen yankinmu a jikin wani murtukeken ita ce. Ana ɗaure su ana tafka musu manyan bulali a jiki, wanda saukar bulala ɗaya ba sa ɗagota sai da fatar gangar jikin mutum, gawargwakin ƙananan yara da manyan da aka karkashe a wurin ba za su irgu ba, ana cikin haka jaririna ya fata motsi da alama kuka zai yi. Duk yadda na kai ga aikata wani abu daga cikin al'amuran tsafi da siddabaru abin ya gagara, ganin yana son tona wurin da muke laɓe ya sa na saka ɗan yatsana na rufe masa baki. Inuwata da wani Badakare ya hango n a ji yana nuna wa wani ɗan'uwansa hanyar wurin da muke laɓe da bashi umarnin ya kamo mu, jikina na rawa na kama hannun Kandala muka fara gudu hankali a tashe. Ba zato ko tsammami na ji na bugu da wani abu, ɗago kaina ya sabbaba min hautsinewar ciki. Hautsinewar da ta sa gumi ya fara karyo min nan take, domin haɗuwar karonbattar da na yi bata da maraba da mun yi gudun gara mun faɗa gidan zago.

😂 Wollah akwai ƙura fa.Ni kaina na ji faɗuwar gaba yasin 😰 wannan baƙar daula ko kaɗan bata yi ba.

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰  ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala

cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
 Wiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Kirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

Free page 7

🥳 in ka ji busa tabbata Sarauniya ce ta ƙaraso, ina kuke matan ƙwarai, mata ba muna mata ba, shin kin jaraba kayan *HONEY-DROPS* me kike jira har yanzu?, Manyan mata, mata masu aji na ta dafifi wajen kwasar kayan gyara, me ya sa za ki kashe kanki da ƙuruciyarki, ko tsohuwar ma na zuwa karɓar nata, kina fama da matsalar bushewar gaba, ɗaukewar sha'awa da ni'ima, ƙaiƙayi ko ƙurajen gaba, jin zafi yayin tarawa da maigida, sanyi ya taɓa miki mahaifarki?, Kina ta allura da shan magunguna ba su miki aiki ba, wane kalar infection kike fama da shi?, Staphylococcus, Gonorrhea, Syphilis, UTI, STDs ne?, Share hawayenki kukanki ya ƙare je ki nemi *HONEY-DROPS INFECTION FLUSHER* ke da sanyi sai dai ki ba da labari, kin gama cacar kuɗi, cikin kwana uku zaki fitsarar da duk wani sanyi da dattin da ke tattare a mararki, ki gyara zamanki gidan aurenki don sanyi kashe mace yake har buzunta, duk wani magani da za ki sha muddin da sanyi a jikinki iyakar shi cikinki, ba zai sauka ba. Magani ne

ingantacce made of herbs, In kin gama da wannan akwai na gyaran other room, akwai Exclusive Gumba ta manyan mata ke nan, ko matar Gwamna ita take sha, ga Gumbar babbar mace mai tada tsohuwar soyayya, akwai fa tsuumi na matan gaske, akwai *HONEY FLOOD TSUUMI* kan ƙiftawar ido ni'ima ta yi ta kwararo miki, akwai BUJENTA JAGAB, da Tsuumin Ɗafau, daga jin sunan kun san akwai zance na bar muku ku ƙarasa, akwai sauran kaya masu zafi🔥

Muna da bridal package

Diamond - 100k
Gold - 50k
Silver - 30k

Ga kuma na postpartum (wanda suka haihu don dawo da martabarsu)

Diamond - 50k
Gold - 30k
Silver - 15k

Kuna iya samun mu ta 08167888934, ko 08067770852

Girma da siffar Badakaren ne suka sake hargitse lissafin rayuwata, a hankali na sake ja da baya ya yin da yake sake tunkaro mu gadan-gadan hannunsa ɗauke da wani mummunan ƙarfe wanda aka naɗe jikinsa da manyan ƙusoshi, a zafafe ya ɗaga da niyyar buga min a tsakar ka cikin shammata mahaifina ya kai masa duka a wuyansa. Take suka fara kokawa ganin haka ya sa mahaifina ya yi mini alama da mugudu ni da Kandala, gudu muke kamar ranmu zai fita don na gama tsorota da yanayin azzaluman mutanen da suka fito daga baƙar daula. A yadda na bar mahaifina da Badakaren ina jimamin halin da mahaifina yake ciki don na tabbata zai yi wuya idan bai yi wa mahaifina taron dangi sun hallaka shi ba, sai da muka yi tafiya mai nisan gaske sannan muka raɓa cikin wata bishiyar ɗorawa mai duhu muka zauna muna hutawa, waige-waige nake yi don ganin hanyar da zan samu ruwan da zan ɗebo mana musha saboda zafin ranar da ya busar da maƙogaronmu. A wahalce Kandala ta kalle ni idonta na zubda ƙwallah tana faɗin, "Kyauta ƙishirwa za ta kashe ni maƙoshina ya bushe." Jijjiga jaririn nake saboda kukan da yake ta tsalawa wanda na tabbata kukan wahala ne sannan na furta mata, "Riƙe min shi ki kula da kyau zan duba mana ko da ƙorama a kusa idan muka sha sai na duba ko zan samu wani naman dawan na gasa mana." Karɓarsa Kandala ta yi na miƙa cikin dajin ina duba hagu da dama ko zan samu ƙaramar ƙoramar da zan ɗebo mana ruwan, ko kaɗan ban yi tunanin wurin da zan ɗebi ruwan ba babban burina bai wuce mu samu ruwa kowanne iri ba ne. Daga can nesa na hango wani bafulatani yana tafe da shanunsa wanda hakan ne ya tabbatar min da kiwo yake, gudu-gudu sauri-sauri haka na rinƙa tafiya don na ƙarasa na cimma masa koda zai sa ya taimaka min, yana ganina ya fara bina da kallon tuhuma don ko bai faɗa ba na san suturar jikina yake kallo wacce ta bambamta da irin ta shi, kallon kaina na yi daga ni sai

guntuwar fatar da ta rufe min ƙirjina da wacce na suturta al'aurata, sannan na ɗago na kalle shi yana sanye da farar rigar saƙi ta kala-kalan zarurruka, sandar hannunsa ya ɗaga na ji yana yin yaren da nake tsammanin fullaci ne sannan ya yo kaina da sauri zai sauke min ita. A razane na ja da baya cikin hakki ina faɗin, "Abar bauta bata wanzar da zalinci a doron ƙasa ba don haka kada ka cutar da ni."  Sauke sandar ya yi ƙasa sannan ya furta, "Hai meye abar bauta kuma? Ke kam aljani ne ko mutum?" Dafe kaina na yi saboda matsanancin ciwon da yake min sannan na furta, "Ni mutum ce tare nake da ƙanwata ka taimaka mana ka ba mu ruwa mu sha." Kallon da yake min ne na tabbatar min da har lokacin bai gama aminta da ni ba, don haka na ga ya runtse ido yana ci gaba da fulatanci sannan ya kara sandar hannunsa a saitin kaina. Ya ɗan jima a haka sannan ya buɗe idonsa ya ce, "Zan taimaka maka ina ƙanwar taka?" Hanyar da na baro su Kandala na nuna masa, ya ƙurawa wurin idanu sannan ya ciro kurtunsa ya miƙo min. Har na ɗaga kai zan sha na tuna halin da na baro su Kandala, da sauri na sauke shi na ce masa. "Ka taimaka ka cika ladanka ka bar ni na kaiwa ƙannena su sha. Idan ka yi haka abar bauta za ta albarka ci kiwonka." Ɓata fuska na ga ya yi don haka gabana ya faɗi, ina shirin roƙonsa na riski muryarsa yana faɗin, "Kada ki sake danganta ni da abin bautarku domin Yesi Almasihu zai yi fushi da ni saboda na haɗa bautarsa da waninsa." Shiru na yi ina mamakin maganarsa domin a iya sanina bayan abar bauta babu wani abu da ake bauta wa a faɗin duniya. Da yake ina cike da son biyan buƙatar kaina sai na gyaɗa masa kai cike da godiya, har na juya zan nufi hanyar na ji yana faɗin, "Ki bar hanyar ɓata ki dawo kan shiriya ko za ki samu gidan daɗi wato aljanna domin mu mabiya Yesu Almasihu mun kasance masu karamci da taimakawa saboda Allah." Ko kaɗan ban gane abin da yake nufi ba don haka ban amsa masa ba, sai na kawar da maganar cikin amsar da na bashi da cewar, "Zan gaggauta kai wa ƴan uwana akwai jariri ina tsoron kada ya mutu." A hargitse ya fura, "Jariri kuma?" Na gyaɗa masa kai, jin haka ya sa ya kaɗo shannunsa ya rufa min baya muka tunkari wurin da su Kandala suke. A galabaice muka same su don haka cikin hanzari na karɓi jaririn na fara bashi a lokacin tuni ya gaji da kuka ya sake yin bacci, sai da ya sha ya ƙoshi sannan na miƙa wa Kandala ita ma ta sha ta rage mini. Tausayin Jaririn ne ya kama shi ya dube ni yana faɗin, "Idan ba za ki damu ba ko na tatso masa nonon Naggen can ya sha." Ban san lokacin da murmushi ya suɓuce min ba na furta masa, "Na gode sosai da taimakonka." Nonon saniyar ya tatsa da ɗuminsa ya miƙo mini na ɗan riƙa bashi kaɗan-kaɗan yana sha. Sai da na lura ya ƙoshi sannan na miƙa wa Kandala ta shanye sauran, miƙe wa na yi na yi na yi masa godiya muna shirin tafiya ya furta min, "Yanzu ina za ku tafi ke da kika ce baki da kowa?" Idanuna ne suka ciko da ƙwalla na furta masa, "A da ni ƴar gata ce gaba da baya, sai dai a yanzu ba ni da kowa ban san inda za mu tafi ba." Tambaya ya sake jefo min nan take ya bashi labarin abin da ya baro mu daga yankinmu, ya tausaya mana sosai don haka ya yi alƙawarin kai mu rugarsu domin ya taimaka mana, duk da ya gargaɗe ni a kan na ɓoye addinina idan kuwa na bayyana shi a rugarsu za su iya korata daga garin. A yadda ya ba ni labari tun tasowarsu iyaye da kakanni babu wani addini da suka sani face Kiristanci, a kan shi suka kafu Yesu Almasihu suke bautawa don haka ba su yadda akai musu kowanne irin addini saɓanin nasu ba. Ba ni da zaɓi don a lokacin burina bai wuce mu samu mutsuguni ba duba da ɗanyan goyon da muke tare da shi, a yadda na ayyana da ace daga ni sai Kandala ne za mu ci gaba da tafiya har mu nufi wani yankin da ba sa tsauwala wa game da addinin da ni kaina na gaje shi tun iyaye da Kakanni. Jiki babu ƙwari na sake rungume jaririn muka fara tafiya, ya wuce gaba shi da shannunsa muna biye.

Ba ƙaramin artabu aka sha tsakanin Badakaren da Mahaifin Kyauta ba, ganin mahaifin Kyauta na yin neman yin galaba a kansa ya sa Badakaren yin fito nan take wasu daga cikin Dakarun suka yi dirar mikiya a wurin, duka suka riƙa kai masa ta ko'ina sannan suka fisgo shi da ƙarfin tsiya suka ɗaure hannunwansa a jikin murtukeken itacen da tuni aka ɗaure mafi yawa daga cikin mutunen garin mazansu da matansu. Yayƴayen da aka raunata iyayensu aka ɗadɗaure su sai bi suke suna dafe ƙafafuwansu suna kuka, haka waɗanda aka kashe iyayensu suna kwance akan gawarwakinsu suna tashinsu suna ihu gwanin ban tausayi. Mata masu ciki da tsofaffi haɗe da ƴanmatan yankin duk an ɗaure su jikin itacen da aka zura musu shi cikin kafaɗunsu. Duk wannan azabar da ake gana musu garin tsit ya yi sai kukan ƙananan yara saboda duk wanda aka ji ya yi ihu zane shi suke yi da bulalar hannunsu ba za su bar dukansa ba har sai sun kwaile masa fatar jiki. A haka suka tasa ƙeyar mutanen garin gabaɗaya suka tafi da su, har sun yi nisa shugaban Dakarun ya sa wasu daga cikin dakarun suka koma suka tarkato ƙananan yaran, waɗanda aka lura da suna kwance kan gawarwakin iyayensu sune aka tasa ƙeyarsu ya yin da waɗanda suke kuka suna bin iyayensu da aka ɗebi wasu, wasu kuma aka bar su a wurin. Tafiya ce mai nisan gaske ga babu ruwa balle abinci babu hutu balle su samu salamar azabar da ake yi musu, idan suka lura gungun itace ɗaya ba sa sauri gabaɗaya suke haɗa wa su zane su, ilahirin jikinsu a farfashe yake yana tsattsafar da jini ya yin da ƙananan yaran da aka tafi da su saboda wahala wasu suka riƙa faɗuwa suna suma. Duk yaron da ya suma ba sa bi ta kansa sai dai su wuce idan kuma da kogi ko rami a wurin sai dai su wurga shi a ciki. Ƙalilan daga cikin yaran ne suka samu ƙwarim gwiwar ci gaba da tafiya a haka har dare ya riske su, a kan dole suka yada zango a wani baƙin daji. Duk da kasancewar su a wurin babu abin da aka ba su da sunan ci ko sha, kuma a yadda suke a ɗaure haka suka ci gaba da zama. Mutum ko fitsari da kashi yake ji sai dai ya yi a wurin, suna ji suna gani Dakarun suka yo farautar naman dawa suka gasa suka ci amma su ko ruwa ba su samu ba. Wani tsoho daga cikinsu ne ya galabaita da ƙishirwa don haka a wahalce ya roƙe su akan su bashi ruwa ya sha, wani gajere daga cikin dakarun ne ya ɗebo garwashin wuta kai tsaye ya yi kansa gadan-gadan. Ganin haka ba ƙaramin ɗaga hankalinsu ya yi ba, nan take jikinsu ya fara karkarwa. Yana zuwa ya buɗe bakin tsohon ta ƙarfin tsiya ya zuba masa garwashin a ciki. Saboda azaba nan take tsohon ya fara sakin kashi da fitsari cikin fitar hayyaci, Dakarun na ganin haka suka bushe da wata irin mahaukaciyar dariya har da masu kwanciya a cikinsu saboda ƙeta. Sai da suka yi mai isar su sannan suka dube su cike da izgilanci suna faɗin, "Waye zai kuma cewa zai sha ruwa a cikinku?" Wurin ne ya yi tsit ba tare da wani ya furta koda kalma ɗaya ba, sai da tsohon ya gama galabaita sannan suka ɗauko wani wurtu da ɗan ƙanƙanin ruwa a ciki suka ɗaga kansa suka sheƙa masa. Ruwan da ya shiga bakinsa ko cikin tafin hannu ɗaya ba zai cika ba, ya yin da sauran ya wanke masa fuska gabaɗaya. A na cikin haka ɗaya daga cikin masu matan da ke ɗauke da tsohon cikin ta fara naƙura gadan-gadan, a galabaice take yunƙurin tashi saboda yadda take jin kan jaririn na iya ratsowa ta ƙarƙashinta. Duk yadda ta kai ga ganin ta miƙe ta gagara sakamakon yadda hannuwansu yake ɗaure a jikin itacen kuma a ƙallah sun kai su goma sha biyar a jikin kowanne itace ɗaya. Kururuwa take cikin azaba da neman ɗauki, mijinta da ke ɗaure a wani itacen ya gagara haƙuri duk da zuciyarsa na bugu saboda fargaba ya dubi Dakarun yana faɗin, "Ku taimakawa mai cikin can haihuwa za ta yi." Ɗaya daga cikin su ne ya fara takowa yana sakin murmushin mugunta ɗauke da muguwar manufa, sai da ya ƙarasa

gabansa sannan ya wurga masa tambaya, "Ko dai matarka?" Ƙara matar tashi ta sake ƙwallawa a hargitse ya kalli wurin idanunsa na fidda ƙwallah. Suna haɗa ido ta fakaici idon Badakaren ta girgizawa mijinta kai alamar kada ya nuna mijinta ne, ganin irin kallon da mutumin yake yi wa ɓangaren matar ya sa Badakaren ya kalli wurin, a hankali ya miƙe ya ƙarasa wurin matar ya ɗora hannunsa akan cikinta yana shafawa har zuwa gabanta, jaririn da ke cikinta ya ji yadda yake mutsu-mutsu ya waiga wurin mutumin sannan ya sake kallonta ya ce, "Amma mijinki yana tausaya miki da alama yana ƙaunarki sosai." Cije baki ta yi saboda azabar da take ji gumi na ci gaba da keto mata, cike da ƙarfin hali ta girgiza kai murya na rawa ta ce, "Ba mijina ba ne."

Ta faɗi haka ne don ta lura a lokacin da mijin nata ya yi magana ya taso gadan-gadan don aiwatar masa da mugunta, wannan dalilin ya sa ta yi wannan badarar ko mijinta ya kuɓuta daga azabarsu. Jin abin da ta faɗa ya sa Badakaren bushewa da dariya, ajiyar zuciya mijinta ya sauke ya sunkuyar da kai ƙasa sai dai duk abin da yake faruwa yana kallonsu ta gefen idonsa. Cikin shammata Badakaren ya saka hannu ya bigi tsakiyar cikinta da ƙarfin gaske, azaba ce ta ratsa ilahirin jikinta ta saki razananniyar ƙara. Ganin haka ya sa jikin mijinta ya riƙa karkarwa ransa ya yi mummunan ɓaci, yana shirin yunƙurawa don yin magana Mahaifin Kyauta ya zungure shi a fakaice cikin raɗa ta furta masa, "Ka da ka yi wani yunƙuri don komai zai iya faruwa daga kai har mai ɗakinka." Babu yadda ya iya haka ya koma ya yi laƙwas yana yin hawayen zuci saboda ɓacin rai, Badakaren ne ya miƙe ya koma wurin zamansu don irin dukan da ya yi mata a ciki ya tabbata idan mijinta ne zai magantu, ganin mijin nata bai tanka ba kuma bai yi wani yunƙurin dakatarwa ba ya sa ya yadda ba matarsa ba ce.  Sabon ciwo ne ya taso mata gadan-gadan ganin haka dabara ta faɗowa sauran mutanen da suke ɗaure a jikin itace ɗaya, yunƙurawa suka yi da ƙyar suka tashi suka tsugunna don sun tabbata idan ba haka suka yi ba babu yadda za a yi ta iya haihuwar abin da yake cikinta lafiya ƙalau. A daidai lokacin da suka tsugunna kan jariri ya taho cikin azaba ta ƙwallah wata gigitaciyyar ƙara sai ga jariri ya faɗo, jaririn ne ya fara wutsul-wutsul a cikin ƙasa da gwiwoyin ƙafarta take yunƙurin ɗaukansa amma ta kasa.  Kukan jaririn ne ya cika dokar dajin don haka tausayinsa ya ratsa zuƙatan mutanen wurin, mahaifiyarsa ta kifa kanta a kansa ta rushe da wani irin matsanancin kuka.

Tamkar dirar mikiya haka ta ji maganar babban Badakaren a kanta, tana ɗagowa ta riske shi ya ɗauki jaririnta. Tsugunnawa ya yi ya ciro wata kaifaffiyar aska ya yanke masa cibiya sannan ya saka aka kwanceta. Mamaki ne ya kamata sai kuma take ganin kamar tausayinta ya ji har ya sa aka kwance ta. Jaririn ya miƙa mata sannan ya sa aka ɗaure mata sarƙa a ƙafafuwa biyu, saitin fuskart ya koma suna fuskantar juna sannan ya ce, "Kin samu wannan rangwamen ne domin biyan buƙatar kaina, yau ita ce ta kasance ranar shaƙatawa a Daularmu don haka zan fanshe ranata a kanki." Ƙirjinta ne ya buga sakamakon yadda take jin gabanta yana yi mata wani irin raɗaɗin azaba, uwa-uba ga babu wani gyara da ta samu a matsayinta na mai jego. Kallon jikinta ta yi ta ga yadda jini yake bin ƙafarta kace-kace, kasa tanka masa komai ta yi sai hawaye da ke bin idanunta. Tana ji tana gani haka Badakaren ya sa aka rirrriƙeta ya fara biyan buƙatarsa da ita a gaban mutane, saboda azabar da take ji sai da ta yi suma biyu sannan ta farfaɗo ta dawo hayyacinta. Jikin sauran mutayen wurin ba ƙaramin sanyi ya yi ba, mijinta ban da huci babu abin da yake yi. Fatar da ta rufe ƙirjinta ta ciro ta naɗe jaririnta a ciki ta rungume, tana haɗa ido da mijinta ya sunkuyar da kai cike da tausayawa. Yadda suka ga rana haka suka ƙarasa ganin

daren, gari na yin haske Dakarun suka tashe su suka ci gaba da tafiya, a galabaice suka ci gaba da cira ƙafafuwansu suka ƙara ɗaukan hanya da yin tafiya mai nisa. Sai da suka shafe wuri guda sannan suka ƙarasa babbar ƙofar da za ta sada su da Daular. Dakarun bakin ƙofar ne suka fara yi musu barka da zuwa, domin su ne tawaga ta biyu a cikin Dakarun da sarki ya tura fataucin bayi waɗanda suka dawo. Saura tawaga biyu da ake saka ran ganin ta hanyar da za su ɓullo.

Mun yi tafiya mai nisan gaske kwatankwacin wacce muka yi a baya, ni da Kandala ba ƙaramin galabaita muka yi ba. Har haƙurina yana shirin ƙare wa zan tambayi ɗan fulanin sai muka fara hango bukkokinsu daga can nesa, a bayan gari ya tsayar da mu ya wuce cikin rugarsu don cemin ya yi matuƙar muka shiga da irin shigar jikinmu cikin rugar ba makawa za su yi mana korar kare kuma babu wanda zai taimaka mana, domin shigarmu ta saɓa da irin shigar da suke yi. Ya dakatar da mu ne domin ya je wurin mahaifiyarsa ya sanar mata da komai kuma ya karɓo kayan ƙanwarsa a sirrance  ya kawo mana mu saka ni da Kandala. Ya ɗan jima da tafiya sannan ya dawo, sai da ya ba mu wuri muka kintsa sannan muka wuce cikin rugar hatta Jaririna sai da na naɗe shi da zanin da aka saƙa shi da fari da kalolin zare.  Bayan mun gama shiryawa kafin mu wuce ya dube ni yana faɗin, "Ku saurare ni da kyau ku ji abin da zan gaya muku, bayan ni da mahaifiyata babu wanda ya san su waye ku. Idan muka shiga rugar mu zan ce musu tsintarku na yi a cikin daji ku ba ƴan nahiyar nan ba ne, garinku ne aka ci shi da yaƙi kuke neman wurin matsuguni babu maganar wani addini bayan na Yesu Almasihu, idan ba haka ba za a samu matsala." Yana gama magana na gyaɗa masa kai cike da gamsuwa na fara jera masa godiya sannan muka wuce, kamar yadda ya gaya min haka ya gaya musu kuma ba su nuna ƙyama a gare mu ba. Hasali ma ba ƙaramin tausayinmu suka ji ba, mahaifi da mahaifiyarsa suka shiga hidima da mu ya yin da aka ci gaba da kula da Jaririna, duk wata kyakkyawar kulawa muna samu amma tunanin iyayena da halin da suke ciki ya addabi gangar jiki da ruhina, babu lokacin da zan kwanta bacci ban yi mafarkinsu. Tun su Inno wuro ba su fara fuskantar halin da nake ciki ba har suka fara tambayata, ban ɓoye musu ba na sanar da su damuwata, sun tausaya min matuƙa haɗe da kwantar min da hankali. Kwananmu uku a cikin rugar da wata asuba muka wayi gari da mummunan tashin hankali sakamakon farmakin da masu fataucin bayi suka kawo. Sun cunna wuta a dukkkan bukkokin rugar, ganin su ya tabbatar min da zargina ya tabbata dai gudun gara muka yi muka faɗa gida zago. A zuciyata nake ayyana ina ma ba mu yi wannan guduwar ba duk abin da zai same mu gara ya same mu tare da iyayena, irin baƙaƙen Dakarun da suka farmaki yankinmu sune suka kawo farmaki wannan rugar da muka sauka, babu yadda muka iya muna ji muna gani suka riƙa azabtar da mu suna ɗaure mu a jikin wasu murtuka-murtukan ita ce, jaririna na zura cikin wata jakar fata na saƙalo shi da gefen kafaɗata zuwa cikina, a itace ɗaya aka ɗaure mu da Kandala muna ji muna gani aka tasa ƙeyarmu cike da azabtarwa.

😰 Shafin akwai ban tausayi, wasan yanzu zai fara💃🤣

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰  ku

dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Ƙirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

Free page 8

🥳 in ka ji busa tabbata Sarauniya ce ta ƙaraso, ina kuke matan ƙwarai, mata ba muna mata ba, shin kin jaraba kayan *HONEY-DROPS* me kike jira har yanzu?, Manyan mata, mata masu aji na ta dafifi wajen kwasar kayan gyara, me ya sa za ki kashe kanki da ƙuruciyarki, ko tsohuwar ma na zuwa karɓar nata, kina fama da matsalar bushewar gaba, ɗaukewar sha'awa da ni'ima, ƙaiƙayi ko ƙurajen gaba, jin zafi yayin tarawa da maigida, sanyi ya taɓa miki

mahaifarki?, Kina ta allura da shan magunguna ba su miki aiki ba, wane kalar infection kike fama da shi?, Staphylococcus, Gonorrhea, Syphilis, UTI, STDs ne?, Share hawayenki kukanki ya ƙare je ki nemi *HONEY-DROPS INFECTION FLUSHER* ke da sanyi sai dai ki ba da labari, kin gama cacar kuɗi, cikin kwana uku zaki fitsarar da duk wani sanyi da dattin da ke tattare a mararki, ki gyara zamanki gidan aurenki don sanyi kashe mace yake har buzunta, duk wani magani da za ki sha muddin da sanyi a jikinki iyakar shi cikinki, ba zai sauka ba. Magani ne ingantacce made of herbs, In kin gama da wannan akwai na gyaran other room, akwai Exclusive Gumba ta manyan mata ke nan, ko matar Gwamna ita take sha, ga Gumbar babbar mace mai tada tsohuwar soyayya, akwai fa tsuumi na matan gaske, akwai *HONEY FLOOD TSUUMI* kan ƙiftawar ido ni'ima ta yi ta kwararo miki, akwai BUJENTA JAGAB, da Tsuumin Ɗafau, daga jin sunan kun san akwai zance na bar muku ku ƙarasa, akwai sauran kaya masu zafi🔥

Muna da bridal package

Diamond - 100k
Gold - 50k
Silver - 30k

Ga kuma na postpartum (wanda suka haihu don dawo da martabarsu)

Diamond - 50k
Gold - 30k
Silver - 15k

Kuna iya samun mu ta 08167888934, ko 08067770852

Rukunin bayi suka rinƙa wucewa kala-kala, kowanne wuri suka wuce da irin kallon da suke yi musu wanda hakan ba ƙaramin sanyaya jikinsu ya yi ba. Ɓangare-ɓangare ne a cikin gidan masarautar wanda ya haɗa da ɓangaren bayi masu aikin wahala kala-kala. Ganin irin baƙar wahalar da bayin suke yi ne ya sake sanyaya jikinsu wasu daga cikinsu har suka fara zubda ƙwallah tun kafin a sama musu gurbin zama, a wani katafaren fili aka tsayar da su mutane sai kallonsu suke ƙananan maganganu suna tashi a wurin. Kamar saukar ungula ba su yi aune ba haka suka hangi wani gabjejen mutum zaune akan kujera mai siffar mutum wanda ya duƙar da kai ga kwari da baka saƙale a wuyansa kamar yadda kujerar ta zame masa mazauninsa kodayaushe. A razane suka dube shi ganin a kan abin da yake zaune, da sauri Dogaransa suka ƙaraso suka fara kafa masa tanti tare da sauron fadawansa. Ransu ba ƙaramin ɓaci ya yi ba sakamakon ganin kamar cin zarafi ne ake yi wa al'ummarsu ta maharba, suna girmama duk wani abu da ya shafi maharba da faruta. Don haka kusan lokaci ɗaya suka sunkuyar da kai ƙasa zuciyoyinsu babu daɗi. Cike da izza, ɗagawa da taƙama Sarki Damina ya dube su a wulaƙance yana faɗin, "Ya ku wannan ƙasƙantacciyar al'umma taɓaɓɓu ababen taɓewa. Ku sani ba tun yau ba ina cike da ƙishirwar samunku don haka sai na shayar da ku ruwan azaba

mai raɗaɗi, duk wani mummunan al'amari da yake faruwa da Daular nan ku ne sila don haka za ku ɗanɗana kuɗarku." Ya gama magana ya dubi ɓangarensa na hagu, wani ƙosasshen ƙato ne mai siffar samudawa a tsaye yana jiran umarninsa. Nuna wurin da su Mahaifin Kyauta suke tsaye ya yi sannan ya nuna wani matashin saurayi yana cewa, "A ɗauko min wancen ƙasƙantaccen karen." Dogarin na jin haka ya ƙarasa bakin wani daro ya ciro baƙar sarƙar sasari ya ƙarasa gabansu ya zargo wuyan matashin da sarki Damina ya nuna. Da yake har lokacin a ɗaure suke nan take gabaɗaya suka kife a ƙasa, a wahalce suka fara ihu saboda azabar buguwar da suka yi wasu daga ciki kansu har fashe wa ya yi. Sai da ya tusugunna ya kunto saurayin sannan ya sake zargo wuyansa yana jansa a ƙasa har gaban Sarki Damina, da ƙarfi ya sa ƙafa ya take kan saurayin cikin ƙasa yana sake murza fuskarta a ƙasa. Lokaci ɗaya ya bushe da wata dariya mara daɗin saurare, matashin saboda azaba ban da wutsul-wutsul babu abin da ƙafafuwansa suke yi. A gadarance ya dubi dubbanin al'ummar da ke wurin yana faɗin, "Daga wannan rana da muke ciki wannan ƙasƙantaccan bawan zai kasance haka a kodayaushe a tare da ni, kullin zai kasance yana cin ƙasa daga yau ita ce abincinsa" Cikin haɗin baki gabaɗaya suka furta, "Sarauniya Sha kundum ta ci gaba da jan ragamar mulkinka ya kai wannan adalin sarki mai cikakken iko. Mun fansar da kanmu gare ka duk yadda ka ga dama ka yi da mu, mu masu biyayya ne a gare ka." Kan Sarki Damina ne ya sake fashewa saboda jin daɗin kambabawar da suka yi masa, ya dubi wani dogari da ke gefensa sannan ya sake cewa. "Yau ranar farinciki ce a gare mu don haka a je a fito da Yarima a kai shi ga ƙasƙantattun can da suka fito daga la'ananniyar zuri'a." Mahaifin Kyauta ne ya sunkuyar da kai ƙasa cike da takaici don irin cin zarafin da Sarki Damina yake yi musu tun da suka zo duniya ba su taɓa ganin irinsa ba. Kasancewar sun san yanayim ciwon yarima ya sa Dogarawa huɗu suka tafi don taho da shi, ba a ɗauki lokaci ba suka dawo da shi a rirriƙe yana wawure-wawure alamun yana son ya yago naman ɗaya daga cikinsu. Zuwan da aka yi da Yarima wannan wurin ba ƙaramin sake ɗugunzuwama hankulansu ya yi ba, jikinsu ban da karkarwa babu abin da yake yi. Mahaifiyar Kyauta cikin kuka ta dubi Mahaifin Kyauta da ke ɗaure a wani itacen daban, ta yi ƙasa da murya hawaye na zuba tana faɗin. "Sa'a dai mazaje uban Kyauta amanar shamuwa. Yanzu haka za mu ƙare rayuwarmu cikin wannan ƙasƙancin da azabtarwa? Babu wani taimako da Abar bauta za ta yi mana ta kawo mana mafita."

Jin tambayarta ya sake raunata zuƙatan sauran matan da ke wurin, lokaci ɗaya hawaye ya wanke fuskokinsu suna kallon Mahaifin Kyauta don jin abin da zai faɗa. Muryarsa na rawa dube su ɗaya bayan ɗaya ya ga yadda duk suna lalace lokaci ɗaya suka fita hayyacinsu sannan ya mayar musu da martani, "Dawa da buɗa mana abar bauta ta shiga lamuranmu. Tabbas shigowata wannan Daular ya farkar da ni daga dogon baccin da muke yi, a wannan Daular da muke ciki ƙarfi da ƙarfin sihiri ba zai fusshe mu ba face mu zuba na mujiya mu ga yadda rayuwarmu za ta kasance. Shigowata Daular nan ya tunasar da ni labaran da magabatanmu suka sanar da ni akan mummunan lamarin da ya faru a ɗaruruwan shekarun da suka gabata tsakanin wannan Daular da yankinmu wato al'ummar Maharba." Cikin kuka wani magidanci ya karɓe zancensa da cewar, "Idan suka hallakar da mu kenan sun yi nasara a kanmu? Shi ke nan za a rufe shafin farauta da mafaruta a faɗin duniya?  Kuna nufin nan gaba tarihi zai bayyana Maharba ƙasƙantattu ne kamar yadda wannan azzalumin sarkin nan yake faɗa?" Mahaifin Kyauta ya sauke ajiyar zuciya ya sake dubansu cike da tausayinsu a fuskarsa ya furta, "Tun

shigowata cikin Daular na na hangi mutuwata da ƙwayar idona, na sani kun sani tun da muka shigo daular nan babu mai fidda mu cikin salama, sai dai jikina yana ba ni da sannu nan ba da jimawa ba wani mummunan al'amari zai faru da su domin jinin Maharba ba zai tafi a banza ba, koda za su ƙarar da mu kaf waɗanda muke nan gabansu na tabbata akwai ɓurɓushin zuri'armu kuma sai sun fansar da jininmu..."

Bai ƙarasa magana ba suka riski wata gigitacciyar tsawar da ta sake hautsina ƴaƴan cikinsu, nan take suka sake lura da duniyar da suke ciki. Suka riski muryar Sarki Damina yana cewa Dogarawansa, "Ku ɗauki Yarima ku kai shi tsakiyar wulaƙantattun can na yarje masa ya yi duk yanda yake so da su kafin na san irin hukuncin da zan yanke musu." Da sauri suka fisgi Yarima har za su nufi wurin su Mahaifin Kyauta ko me Sarki Damina ya tuna a gaggauce ya dakatar da su da cewar, "Ku dakata!" Ilahirin mutanen wurin ba ƙaramin mamaki suka yi da jin kalaman Sarki Damina ba, da kansa ya miƙe ya kira wasu zaratan dakaru guda goma ya sa suka fara kwance su ɗaya bayan ɗaya. Wani sanyin dadɗi ne ya ratsa su a tunaninsu wani sassauci za su samu, da kansa ya sa aka fara ware ƴanmatan cikinsu gefe ɗaya sannan ya sa waɗannan Dakarun suka tafi da su sihirtaccen gidansa da ke bayan gari. Ganin haka ya sa suka fashe da kuka don ba su san abin da zai aiwatar musu ba, yana gama zaɓarsu ya sa aka sake mayar da sauran aka ɗaure. Ya janyo hannun Yarima da kansa ya kawo shi tsakiyarsu, gudun kada ya haɗa da shi ya sa shi matsawa da sauri. A haukace Yarima ya kwarmata mahaukacin ihu, zaro idanu yake yana wage baki. Wani tsalle ya buga cikin shammata ya fisgi jaririn da ke hannun mai jegon da suke kira da Lantan, yana fisgarsa ya riƙe ƙafafuwansa da hannuwansa biyu, kan jaririn na ƙasa ƙafafuwansa suna sama. Tsalle ya fara yi a haka daga shi da wani guntun ganyen da ya rufe masa al'aurarsa, tsallen da yake yi sa ganyen ya fadî ya zama babu komai a jikinsa. Cike da azaba jaririn ya fara ƙwalla matsanancin kuka, lokaci ɗaya Sarki Damina ya ƙyaƙyace da dariyar ƙeta yana nuna wurin da yatsansa. Ganin haka ya sa sauran mutanen wurin suma suka fara ƙyaƙyata dariya mugunta, sai da ya ƙara ɗaga jaririn ya yi wani irin gurnani da ƙarfin tsiya ya yaga jaririn gida biyu kowanne hannunsa ɗaya da ƙafar jaririn, take ya sake tsanyarewa da wani irin gigitaccen kuka na fitar hayyaci, Yarima ya riƙa nunawa mutane sannan ya saka baki ya cisge kunnensa na hagu. Ganin haka ya sa nan take mahaifinsa ya fadî a wurin sumamme, Mahafiyarsa tun lokacin da ya karɓe shi ta fara wata irin shaƙuwar baƙin ciki da tashin hankali. Lokaci ɗaya tari ya sarƙe ta; ta fara aman jini ana cikin haka ta sulale a wurin matacciya.

Tafiya muke cikin wahaltacciyar rayuwa wacce ta baƙunci rayuwata ba tare da zato ko tsammani ba, tun da aka wanzar da ruhina ban taɓa ganin azzuluman da babu ɗugon imani a ƙirjinsu tamkar waɗannan Dakarun ba. Ba ma yin taku biyu zuwa uku ba tare da sun tafka mana bulala ko wani dogon ƙarfe a jikinmu ba, ba su ƙyale yara ba balle tsofaffi marasa ƙwarin jiki, tun muna kuka da hawaye har ta kai ga mun koma kukan zuci wanda yake azabtare da tsokar zuciya. Lokacin da muka miƙa wuya gare su mun sallama musu gangar jiki da ruhinmu, jaririn da ke wurina ne azabar rana ta ishe shi don haka ya fara tsala kukan babu ƙaƙƙautawa. Duk yadda na kai ga rarrashinsa sam ya gagara fahimta halin da muke ciki ba zan iya wanzar da komai ba akansa, tun ina iya dakewa har rauni da tausayinsa ya mamaye ni. Na kalle shi cike

da tausayawa saboda har ya yi kukan ya gaji ban da ajiyar zuciya da tsotsar hannu da jakar fatar da yake ciki babu abin da yake yi, hawaye ne yake bin idanuna bibbiyu ina takaicin amsar alƙawarin jaririn da na gagara taimakon rayuwarsa har yana neman rasa ransa. A lokacin da muka yada zango dare ya tsala sosai, hasken farin wata ne ya haske mu muna zaune jigun-jigun. Jaririna ne ya fara mutsu-mutsu lokaci ɗaya ya tsanyare da kuka, gwiwoyin ƙafata na saka ina jijjiga shi koda zan samu ya yi shiru amma fir ya gagara fuskantata. Da ƙyar na tura kaina sautin kunnensa na fara yi masa raɗa a tunanina ko zai fahimci halin da muke ciki ya yi shiru, amma kamar na sake ingiza shi haka ya tsanyare da matsanancin kuka, wata mata da ke gefena ta share ƙwallarta sannan ta furta, "Yesu Almasihu ba zai taɓar da mu ba, salama da jin daɗi na tattare da mu ranar gobe ƙiyama." Lokaci ɗaya na ji sun amsa da, "Amiiin. Mu mabiya muna buƙatar cetonka Yesu." Kallona ta sake yi ta furta, "Da zan iya da na shayar da yaron nan domin..." Bata ƙarasa ba wani Badakare ya yi tsaye a kanmu, tsit muka yi jikinmu na karkarwa. Cikin tsawa ya dube ni yana faɗin:

"Me ya sa ɗan tayin nan zai cika mana kunne da kuka." Wani irin gumi ne ya shiga karyo min ta ko'ina ya yin da tsoro ya mamaye ni ina fargabar kada ya nemi raba ni da shi ko ya salwantar da rayuwarsa. Muryata na rawa na sake saka gwiwoyin ƙafata na rungumo shi jikina na furta masa, "Yunwa yake ji amm... Dama..." Murmushin da na ga ya yi ne ya sa na taune harshena ba tare da na sani ba har sai da raɗaɗin haka ya ratsa ni, sauya fuska ya yi cikin yanayin damuwa wanda haka ya sa na fara tunanin ko tausaya mana yake yi. Ina tsaka da tunanin na ji ya furta, "Wannan da gani bai ci abinci ba ko? Ke ce mamansa ne?" Harshena har rawa yake don na sanar da shi a tsammanina waraka ce ta zo mana sai dai abin da ban sani ba ashe tashin hankali ne zai sake ziyartar mu akan wanda muke ciki. Kallonsa na yi na ce, "Mun rasa mahaifiyarmu ni ce yayarsa." Ina rufe baki ya saka hannu ya ɗauke shi ya ɗaga sama yana kallo, nan take zuciyata ta fara bugawa tamkar za ta hudo ƙirjina. Runtse idona na yi ina ambato duk wani kirari da bege da muke yi wa Abar bauta, ana cikin haka ta amsa roƙona sai ji na yi ya ɗora shi akan cinyata. Ajiyar zuciyar da na yi sai da bayyana a fili har sai da na lura da kallon da yake yi mini, da sauri na kawar da kaina gefe ban yi aune ba na ga ya fidda al'aurarsa a waje ya yi fitsari cikin wani kurtu ya kama bakin jaririn ya fara ɗaɗɗaka masa. Mutuwar zaune na yi mamakin da ban taɓa shiga ba ya mamaye ni, daga gefe na ji wata tsohuwa tana faɗin, "Yesu Almasihu ya yi hani da zalinci don haka zai azabtar da ruhin masu aikata zalinci." Yana jin haka ya ƙarasa ya ciro wuƙa ya fara zagayata da ita, cikin shammata ya ɗaga rigarta ya burma kaifaffiyar wuƙar a cikin mamanta ɗaya, gabaɗayanmu babu wanda bai ƙwallah ihu ba saboda ganin abin da ba mu taɓa gani ba. Ya zaro wuƙar ya sake burmawa ɗayan sannan ya soka mata a tsakiyar ƙirjinta, yana zare wuƙar ya tura hannunsa ciki ba zato muka ga ya zaro zuciyarta waje. Yana ciro wa ya bar gawarta na lilo a jikin itacen, a kan idanunmu ya saƙale zuciyar a jikin wani ƙarfe da suke raɗa mana a duk lokacin da suka ga ba ma sauri, ya haɗa wuta nan take ya gasa ta suka cinye. Kwanciyar hankalina ɗaya da na samu jaririna ya yi shiru, don haka na ci gaba da addu'a akan Abar bauta da ta dafa min har mu ƙarasa wurin da za su kai mu, ina wannan fatan ne ba tare da nasan azabar da suke yi mana shafar mai ce akan wacce za mu tarar a gaba.

Da yake sun fusata da abin da dattijuwar nan ta faɗa, suna gama cinye zuciyarta suka tasa

ƙeyarmu gawarta na lilo muka ci gaba da tafiya. Sai da muka yi tafiya mai nisa sannan muka hango wani ƙasaitaccan gini mai birgewa wanda aka gina shi da alatun more rayuwa, wani abin da ya ɗaure min kai bai wuce yadda nake ganin gumakan maharba na fasalta ƙasƙanci ba. Haka na zurawa lamarin idanu don ganin sabuwar duniyar da za mu riski ruhi da gangar jikinmu a ciki, amma ko ba a faɗa min jikina ya ba ni wannan ita ce Baƙar Daular da waɗannan azzaluman suka fito daga cikinta. Cikin wata babbar ƙofa muka shiga sai dai wata irin hayaniya na riƙa ji ba tare da na ga waɗanda suke waɗannan surutan ba, daga can gefe na riƙa ganin wasu zaratan Dakaru na tsugunnawa har ƙasa suna saka goshinsu a ƙasa suna miƙa min gaisuwa, a yadda na lura sam babu wanda ya lura da abin da nake gani a ƙwayar idona don haka ban tankawa kowa ba na bar abin a raina kamar yadda na saba duk lokacin da wani baƙon yanayi ya riske ni. Wani ingarman farin doki na hango ya ƙaraso wurina yana shafa kansa a jikina yana ɗaga ƙafafuwansa na gaba sama, ya yin da na ji wata muryar da ban san ta waye ba yana faɗin, "Alƙaluma za su daidaita da dawowarki duniyarki ya ke Sarauniya Sha kundum, waɗannan mutanen jininki ne, zuriyarki ne kuma ahalinki ne. Hutawarki lafiya domin ke mai babban matsayi ce tare da su." Ana gama faɗin haka na hango zugar wasu dakarun irin waɗanda suka yi farautarmu, suma sun taso waɗansu mutane kamar yadda namu dakarun suka farauto mu maza da mata. Dakarun cikin Daular ne na ji suna faɗin, "Sauran runduna biyun da ake tsammani sun dawo cikin nasarar Sarauniya Sha kundum." A hankali na furta, "Sarauniya Sha kundum? Wace ce ita?"

Kafin wani lokaci tuni Yarima ya yi fata-fata da naman jaririn ya ci na ci ya wurgar da na wurgarwa, ihu mutanen wurin suke yi da shewa na take aka fara kiɗe-kiɗe da bushe-bushe. Sarki Damina ya sa aka ɗauke gawar mahaifiyar Jaririn, duk da zafin rana ta sa mahaifin jaririn ya fara farfaɗowa ba su bi ta kansa ba aka haɗa da shi aka kai ramin da ake ƙone duk wata gawa da Sarki Damina ya bayar da umarni. Giya aka kawo wa Yarima ya rinƙa ɗaɗɗaka duk wanda ta rayawa sai ya miƙa masa akan dole sai ya sha, sai da Yarima ya gama shagalinsa sannan Sarki Damina ya sa aka tafi da shi ɗakinsa, su kuma iyayen Kyauta ya saka aka tafi da su Gidan duhu na tsawon mako guda. Nan take taron ya watse, ƴan matan da ya ware ya sake zuwa ya duba su ɗaya bayan ɗaya sannan kai tsaye ya wuce tsaunin kogon dutsen Boka Mai zamani domin ya bincika masa ko akwai sarauniyarsu Sha kundum a ciki kafin ya yanke musu hukunci.

Muma bari mu yi wa Saruniya Sha kundum barka da dawowa duniyarta🤣💃

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰 ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
 Wiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Kirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

Free page 9

🥳 in ka ji busa tabbata Sarauniya ce ta ƙaraso, ina kuke matan ƙwarai, mata ba muna mata ba, shin kin jaraba kayan *HONEY-DROPS* me kike jira har yanzu?, Manyan mata, mata masu aji na ta dafifi wajen kwasar kayan gyara, me ya sa za ki kashe kanki da ƙuruciyarki, ko tsohuwar ma na zuwa karɓar nata, kina fama da matsalar bushewar gaba, ɗaukewar sha'awa da ni'ima, ƙaiƙayi ko ƙurajen gaba, jin zafi yayin tarawa da maigida, sanyi ya taɓa miki mahaifarki?, Kina ta allura da shan magunguna ba su miki aiki ba, wane kalar infection kike fama da shi?, Staphylococcus, Gonorrhea, Syphilis, UTI, STDs ne?, Share hawayenki kukanki ya ƙare je ki nemi *HONEY-DROPS INFECTION FLUSHER* ke da sanyi sai dai ki ba da labari, kin gama cacar kuɗi, cikin kwana uku zaki fitsarar da duk wani sanyi da dattin da ke tattare a mararki, ki gyara zamanki gidan aurenki don sanyi kashe mace yake har buzunta, duk wani magani da za ki sha muddin da sanyi a jikinki iyakar shi cikinki, ba zai sauka ba. Magani ne

ingantacce made of herbs, In kin gama da wannan akwai na gyaran other room, akwai Exclusive Gumba ta manyan mata ke nan, ko matar Gwamna ita take sha, ga Gumbar babbar mace mai tada tsohuwar soyayya, akwai fa tsuumi na matan gaske, akwai *HONEY FLOOD TSUUMI* kan ƙiftawar ido ni'ima ta yi ta kwararo miki, akwai BUJENTA JAGAB, da Tsuumin Ɗafau, daga jin sunan kun san akwai zance na bar muku ku ƙarasa, akwai sauran kaya masu zafi🔥

Muna da bridal package

Diamond - 100k
Gold - 50k
Silver - 30k

Ga kuma na postpartum (wanda suka haihu don dawo da martabarsu)

Diamond - 50k
Gold - 30k
Silver - 15k

Kuna iya samun mu ta 08167888934, ko 08067770852

Duk wata al'ada da ake gudanarwa kafin ya shiga tsaunin Boka mai zamani sai da ya aiwatar, daga matsayar da Dogarawansa suka saba tsayawa wannan karon ma a nan suka yi carko-carko. Ko ba a faɗa musu ba sun fahimci sauyi a tattare da Sarkin nasu, sai dai sun ta'allaka hakan ne sanadin baƙin bayin maharban da aka yi wanda su kansu ba su san takamaiman tsattsamar alaƙar da ke tsakaninsu da Maharban ba. Lokacin da Sarki Damina ya shiga cikin Kogon dutsen tsirara ya same shi a tsakiyar kogon, hannunsa ɗaya ɗauke da ƙwarya ya ɗaga ta sama yana biya waɗansu irin ɗalasiman tsafi. Wata jar akuya ce tsaye a gabansa da alama tsaface ta yake yi da baƙaƙen zakaru uku, sai wani gudan abu da ke hannunsa da hagu tamkar gudan jini yana matsa shi a tsakiyar kan akuyar. Jin motsin Sarki Damina ya sa shi  waigawa a hargitse don a wannan ranar ya tabbata babu wani mai kawo masa ziyara, daskare wa Sarki Damina ya yi saboda fargaba, tsoro da tashin hankali. Saboda gabaɗaya ya manta da wannan ranar ba ya ziyartar Boka mai zamani domin ranar ta kasance masa ranar neman biyan buƙatarsa ga Sarauniya Shakundum. Tun boka mai zamani bai yi magana ba bakin Sarki Damina na rawa ya furta, "Ina neman gafarar zunubin da na aikata na kasance mai mantuwa a gafarce ni kada Shakundum ta yanke mummunan hukunci a kaina." A fusace Boka mai zamani ya nuna masa ƙofar kogon a hargitse yana faɗin, "Ɓace wa ganina idan ba haka ba yanzu na roƙar maka a zaba wurin Sarauniya Shakundum ta la'anceka ka ɗaiɗaice." Kamar sabon munafiki haka Sarki Damina ya fice sum sum sum rai a ɓace, cike da hargowa ya rufe Dogarawansa da faɗan babu laifin tsaye balle na zaune.

Lokacin da Sarki Damina ya sa aka kai su Mahaifin Kyauta ɗakin duhu gabaɗaya sun gama galabaita saboda tsananin zafin rana da yunwar da take sasaƙar cikinsu, a can tsakiyar gidan masarautar ɗakunan suke. A ƙarƙashin ƙasa aka samar da wurin saboda waɗanda suka aikata mummunan zunubi ko kuma waɗanda Sarki Damina ya yi mummunan fushi da su, baƙiƙƙirin wurin yake saboda babu ɗigon haske da yake ratsawa da ciki. Duk yadda ka kai ga son ganin tafin hannunka ba za ka iya ganin ba balle waɗanda aka saka ku tare da su, sai dai ku riƙa lalubar juna kuma yin magana a haka. Cikin ɗakunan cike yake da kunamu suna harkokinsu kamar yadda kiyasai suke kai kawo a doron ƙasa. Ana saka su ita ce ta fara yi musu marhabun lale ta rinƙa sakar musu cizo ta ko'ina ban da ihun yara da na iyayen su kansu babu abin da kake ji. Da suka lura ihu ba zai kai musu ba haka suka riƙa lalube da hannuwansu da sun ji ƙatuwar kunawa su saka hannu ko ƙafa su murtsuke ta. Duk da haka ko kaɗan ba su tsira ba haka suka haukace saboda azabar harbin da take yi musu, a yammaci zuwa wayewar gari ƙananan yara huɗu ne suka rasu da manya biyu sanadiyyar mummunan harbin da kunamar take yi musu. Washegari suna nan zaune jigun-jigun cikin baƙar azaba suka ji an buɗe ɗakin da suke ciki, sai a lokacin da hasken rana ya hasko suka fahimci a zaune suka kwana har gari ya waye, cike da ƙarajin ban tausayi suka fashe da kuka suna faɗin, "Ku taimaka ku cece mu duk abin da kuka saka mu na aikin wahala mun amince za mu yi bakin ƙoƙarinmu." Badakaren da fuskarsa babu alamun wasa ya furta, "Ba don Sarki Damina ya so ku da rahama ba da a nan za ku dauwamma har sai kunamun ciki sun hallakar da ruhinku. Ya ba ni umarnin a fito da ku zuwa sararin haraba zai rarraba ku gida-gida domin kowa ya san irin aikin da zai rinƙa yi." Saboda murna har kwanciya suka yi suna gode masa suna cikin godiya suka ji ya buga musu tsawa yana cewa, "Yau kwananku nawa rabonku da abinci?" Bakinsu har rawa yake suka furta, "Yau kwana huɗu." Girgiza kai ya yi sannan ya furta, "Idan kun je za ku ci a cen." Daɗi ne ya mamaye zuciyarsu sannan ya buɗe musu suka riƙa fitowa ɗaya bayan ɗaya. Duk wanda ya san su a baya matuƙar ya gan su a wannan lokacin ba zai taɓa gane su ba, saboda wani irin burɗun-burɗun da jikkunansu ya yi. Da wata irin rama ta ban mamaki da suka yi sun yi wani irin baƙi tamkar waɗanda suka shekara suna matsananciyar jinya.

Sarki Damina na sauka daga tsaunin boka mai zamani kai tsaye gida ya wuce, yana shiga turakarsa ya samu Usaina zaune ta haɗa kai da gwiwa. Duk duniya babu abin da Sarki Damina ya ƙi jini ya ƙi tsana sama da ya ga ran Usaina a ɓace, don haka a rikice ya dube ta yana tambayarta. "Yake faruncikina uwar gida a wurin Damina uwar Yarima bada kanki a sare. Ya ke Hasana shin waye ya taɓa min ke yanzu na sa a sauke min kansa ƙasa ko shi ɗan gidan uban waye, idan kuma bautarwa kike so ki gaya min wanda kike so duk matsayinsa a yankin nan na sa a bautar da shi." Sai da ta goge ƙwallar munafurci sannan ta ce, "A lokacin da Maharban suka shigo Daular nan haka kawai na ji jikina ya ba ni zuwan su babu alheri a ciki, na ji an ce har da wacce ta zo da jariri a ciki ko?" Usaina ta yi tambayar tana ƙura wa Sarki Damina idanu don ta karanci yanayinsa, tun ranar da tawagar farko ta shiga cikin Daular Bawanta mai yi mata leƙen asiri ya ke kai mata ɓoyayyun bayanai, har ta kai ga ya sanar da ita zuwan tawaga ta biyu da jaririn matar nan kafin Yarima ya hallaka shi. Sarki Damina na gama jin bayaninta tsaf ya bushe da wata irin mahaukaciyar dariya sannan ya furta, "Tuni shalelenki ya gama da shi indai wannan jaririn ne." Cikin kissa ta sake tambayarsa nan take ya zayyana mata duk irin kisan rashin imanin da Yarima ya yi masa. Ajiyar zuciya ta sauƙe a fili saboda ko ba komai ta san ta

gama da jaririn da Boka mai zamani ya sanar mata ya wanzu a nahiyar maharba, babban aikin da ke gabanta bai wuce ta gano wane ne tauraro na biyu da na uku da ke cikin masarautarsu ba domin tana gudun kada gaba allura ta tono garma. Ta san ɗayan tauraron cikin maharban shi kansa ba zai yi mata wuyar gani ba domin sannu a hankali za ta saka Sarki Damina ya riƙa salwantar da ruhinsu ɗaya bayan ɗaya. Ganin yadda Usaina ta bashi fuska ya sa shi jin daɗi domin idan bata ga dama ba hatta ɗakin akwai wurin da take yi masa iyakarsa. Don haka a daren ranar Usaina ta bashi haƙƙinsa musamman da ta tabbatar da ta bashi haɗin da Boka mai zamani ya bata ta tashi kuma ko kaɗan bai tambayeta ba balle ya musa mata, tamkar ajiya ya bata haka ya amsa hannu bibbiyu ya kafa kai ya shanye. Washegari sai da yamma ta yi sosai sannan ya saka Dakarunsa su fito da iyayen Kyauta, haka aka sake fito da su jama'a sai kallonsu suke yi. Suna ƙarasawa tsakiyar filin aka saki kiɗe-kiɗe da bushe-bushe, masu giya suka fito da ita suka riƙa sha suna tamɓele a wurin. Abin da ya ɗaure wa su Iyayen Kyauta kai bai wuce yadda suka ga duka al'ummar wurin sun yi ado da zanen fari da baƙi ba. Hatta Sarki Damina da Dogaransa duk sun fante jikinsu da baƙi da fari, sai da suka ƙura ido suka lura da cewa zanen jikin mutanen ba komai ba ne face zanen idanu. Kowannensu babu wanda ba ya zance zuci a cikin zuciyarsa, suna tsaye a tsakiyar rana aka kawo musu dafaffiyar jar dawa babu komai a cikinta. A yunwace suka ɗauka suna na ci kafin wani lokaci tuni sun cinye sakamakon dama ba wata ta kirki aka kawo musu ba, wani irin jan ruwa aka kawo musu kamar turɓaya. Shi ma ba su ɓata lokaci ba suka daka masa wawa, nan take suk shanye shi. Sarki Damina ne ya ɗaga hannu lokaci ɗaya mutunen wurin suka yi tsit, Waziri ya miƙe da wata sanda a hannunsa mai kan zaki ya fara kallon mutane ɗaya bayan ɗaya sannan ya ce, "Musha giya mu ji daɗi don yau ranar ido ce a gare mu babu wanda ya isa ya zura mana ido." A hankali Mahaifin Kyauta ya sake maimaita maganar ta shi don ko kaɗan bai fahimci komai a maganar ba, yana cikin nazari ya riski Wazirin ya ci gaba da cewa. "A yau ba za mu duba tsofaffin Bayi ba za mu ɗauki  sadaukarwar idon babban dodo a wurin waɗannan la'anannun bayin maharban,
." Ya ƙarasa magana yana nuna wurin da su mahaifin Kyauta suke tsaye. Ilahirin jikinsu ban da rawa babu abin da yake yi, Waziri na rufe bakinsa ya ƙarasa wurin ya jango Mahaifin Gogo saurayin Kyauta. Sai da aka kai tsakiyar filin aka zaunar da shi a kan kujerar ƙasa aka ɗora kansa a kan hannun kujerar, wasu garadan Dogarai ne suka ƙarasa suka ɗaure hannuwansa ta baya sannan ya ɗauko kaifaffiyar wuƙa ban da sheƙi babu abin da take yi, saita ramin idonsa ya danna wuƙar da ƙarfi ya ƙwaƙwalo ƙwayar idonsa. Wani irin gurnani yake yi saboda azaba jikinsa na wani irin karkarwa kamar ransa zai fita, a cikin wani ƙoƙon kai ya saka ƙwayar idon sannan ya sake saka wuƙar ya ƙwaƙulo ɗayan idon sai kuma ya ɗebo wani ruwa mai koriyar kala ya zuba masa a ƙwayar idon. Daga haka Dakarun suka ɗauke shi aka wuce da shi ɓangaren makafin cikin gidan, wannan lamarin da suka gani ya sake ɗugunzuma hankulansu. Don haka wasu daga ciki suka riƙa zubda ƙwallah wasu kuma suna roƙon mutuwarsu kafin a ɗanɗana musu wannan ukuɓar. A karo na biyu Waziru ya zaƙulo Mahaifiyar Kyauta, ganin haka ya sa ta fashe da kuka mai tsanani tana ɗaga wa mijinta hannu, ko me Waziri ya tuna sai kuma ya hankaɗata ta koma, ya miƙa hannu ya janyo wata matashiyar yarinya da ba za wuce shekara goma sha uku ba. Tana kuka mahaifiyarta na riƙe ta haka Waziri ya fisgeta ita ma ba a ɗauki lokaci ba aka cire nata idanuwan aka wuce da ita. Bayan ita Wata mai tsohon ciki suka ɗauko ita ma sai da suka ƙwaƙwale nata sannan ya burma wuƙa a cikinta ya zaro jaririn da ke kwance

a cikin cikinta. A daidai wannan lokacin ayarinsu Kyauta suka ƙarasa cikin filin manyansu da ƙanana, ƙura ce ta gauraye wurin saboda yawansu sakamakon tawagar dakaru biyu ce suka shigo. Yawan mutane da tashin hankalin da suka yi tozali da shi ya sa kowannensu ya sha jinin jikinsu, mummunan kamannin da danginta suka sauya ya sa ta gagara bambamce ainihin surarsu, sai dai a lokacin da ta gan su ta fahimci irin suturar yankinta ce. Lokaci ɗaya tunanin iyayenta ya faɗo mata hawaye ya ciko idanunta take tunanin halin da suke ciki, don a tunaninta ƙila tuni an gama da su.

Dum! Na ji kaina ya yi min tamkar an ɗora min dutse, haka kawai na ji hajijiya na neman ɗaukana har sai da na jingina kaina jikin sauran mutanen da ke tare da ni. A hankali na samu damar buɗe idanuna, ban yi aune ba na hango wata ƙasaitacciyar kujerar zinari daga can nesa da ni, Jarumin mazajen da ya saba faɗo wa rayuwata na hango yana kirana da hannunsa. Farin dokin ne ya fara takowa har ya zo gabana yana ci gaba da goga kansa a jikina, karon farko na kalli Kyauta sannan na ce, "Kyauta kina ganin farin doki a kusa sa ni?" A wahalce ta girgiza min kai ta ce, "Sai dai idan gizo idanunki suke yi miki amma yanzu haka muna wani wuri mai iya tsinka zuciya, na shiga tashin hankula kala-kala amma ban taɓa cin karo da makamancin wannan ba." Ina yunƙurin bata amsa na riski sanarwar mutumin da nake tsammanin shi ne mai mulkar wannan yankin bakiɗaya, sai da ya miƙe tsaye sannan na ji fara sanarwar da cewar. "A ware mini al'ummar Maharba ɓangare guda ba na buƙatar a haɗe su da waɗannan bayin da suka shigo wannan Daula tamu mai albarka yanzu." Tun bai rufe baki ba Dogarawan suka zabura da sauri suka fara yi mana iyaka da al'ummar da aka kira da Maharba. Tun da na ji ya ambaci haka na riƙa leƙawa koda zan samu na yi tozali fa mahaifana, duk da na aminta da zuciyata ba ƙaramar yaudarata take yi ba. Kwatsam! Kamar a mafarki na yi kwalli da su, kamaninsu duk sauyin yanayin da suka samu ba zan mance su ba. Iyayena da nake ƙishirwar gani, da su na yi tozali a lokacin da ganinsu ba zai yi mini amfani ba. Hawayene ke bin idanuna bibbiyu ya yin da na sake tabbatar da wanzuwar halitata tana da sanadi da ƙaddara wacce bawa baya taɓa tsallake mata. Ina cikin wannan yanayin na ji ya sake faɗin, "A kunkunce wannan tagawar sannan a zaɓo mini kyawawan ƴanmata daga cikinsu, a wannan ranar ba zan kira Yarima ba domin ya fi ƙarfin gabaɗaya waɗannan ƙasƙantattun don haka a zaɓi nagartattu sha biyar a tura masa su." Babu musu suka aiwatar da abin da ya umarce su, suka shiga kwance mu nan take daɗi ya mamaye zuciyata ko babu komai za mu samu hutun ɗan taƙaitaccen lokaci. Hannun Kyauta na riƙe muka riƙa kutsawa tsakiya don kada su ɗauki ɗaya daga cikinmu domin tun da na ji an ce za a kai ƴanmata wurin Yariman Daular na san ba abin kirki zai aikata mana ba, ina daga lungu ina hango yadda ake fitar da ƴanmata mafi yawa daga cikinsu iyayensu na jansu suna ihun rabuwa da su. Ban yi aune ba na ga wani Gabjejen Badakare ya fisgi hannin Kandala, a hargitse na yi kukan kura na cafko hannunta ya fara fisgarmu tare. Yana ganin ina jan hannunta ya ƙaraso a fusace ya ɗauke ni da wani irin gigitaccen mari wanda zafinsa ya sa na kife a katsa tare da jaririn hannuna, cike da azaba ya tsanyare da matsanancin kuka. Inna wuro ce ta ƙaraso wurina ta karɓe shi ina yunƙurin tashi ban yi zato ba na ji ya dawo ya fisge ni, ya hankaɗa ni da ƙarfin gaske. Kandala na ganina ta rugume ni tana kuka ni ma ban da zaɓi da ya wuce na zubda na wa hawayen, muna cikin wannan yanayin na ji Badakaren nan ya kwarara ihun da ya sa idanunmu suka koma kansa. Zaro idanuwa na yi cike da fargaba abin da na gani, gefen fuskarsa ce ta hau daddarawa haka

kawai kamar ana yaga tsuman zani. Wani abin mamaki ɗaya ɓarin wurin babu abin da ya same shi. Ganin yana neman hautsina wurin ya sa Sarki Damina ya tura wasu daga cikin Dogarawansa suka kai shi turu (Gidan mahaukata.) Da kansa ya ƙaraso wurinmu ya fara zaɓar ƴanmatan da za a kaiwa yarima, ba zato na ga ya sa da ni a ciki wanda za a kaiwa Yarin, hakan ya sake sabbaba mini kaɗawar hanta. Mu goma sha biyar ya wara daga cikin waɗanda aka zaɓa sai ƴanmata biyar da na ga ya lissafa daga ciki har da Kandala. A gaban dubbanin jama'a babu kunya maganaina suka hango min yadda ya fara kai hannuwa jikin su Kandala yana taɓa al'aurarsu. Duka babu wacce bai kai hannu jikinta ba sannan ya bada umarni da akai masa su can gidan shaƙatawarsa da ke bayan gari. Mu kuma ya sa aka tarkata mu aka wuce keɓaɓɓan gidan Yarima da mu, tun daga tsakar gidan Dakarun suka yi ta tsige mana suturar da ke jikinmu. Tamkar dabbobi haka suka tura mu cikin ɗakin da na hangi wani matashin saurayi na zaune ya kifa kansa da gwiwa, jin motsinmu ya shi ɗagowa yana zaro idanu haɗe da kallonmu ɗaya bayan ɗaya. Ban yi mamakin ganinsa ba domin fuskarsa ba baƙuwa ba ce a wurina, sai dai na yi mamaki a tsawon shekarun da ya shafe yana ziyartar duniyata da bai sanar da ni yana da alaƙa da wannan Baƙar Daular ba. Dama shi ƴan biyu ne bai sanar da ni yana da wani ɗan'uwan ba? Idan haka ne kenan yana da alaƙa da zuwanmu wannan azzalumar Daular, ya aka yi na bar shi a filin can na sake riskarsa a wannan ɗakin har na ji ana ambatonsa da sunan Yarima? Ban gama jerawa zuciyata tambayoyi ba balle na bawa kaina amsa na ji ya yi kukan kura ya fisgi ɗaya daga cikinmu ya fara biyan buƙatarsa da ita, kuka nake mai tsuma zuciyar mai sauraro tausayin kaina ya mamaye zuciyata. Yana gama amfani da ita ya rufe ta da duka kamar ya samu jaka har sai da ta daina motsi. Haka ya bi mu ɗaya bayan ɗaya yana amfani da mu, wanda ni ce mace ta ƙarshe da ya keta wa haddi ya raba ni da martabata ta ƴa mace. Tun yana jikina na ji ya fara wani irin munshari mai ban tsoro wanda haka ne ya tabbatar min da bacci ya ɗauke shi, da ƙarfi na ture shi na koma gefe ina ci gaba da hawaye. Dakarun da suka kai mu ba su suka zo suka kwashe mu ba sai da dare ya tsala sannan aka ɗauke mu aka kai mu wani ɓangare wanda na ji suna kira da, ƴantattun bayi. Wani abu da ya tsaye mini a rai bai wuce yadda komai na Yarima yake min kamanceceniya da Jarumin da ke ziyartata ba, sai dai lokaci ɗaya tsanarsa ta mamaye zuciyata na ji danasanin shigowarsa rayuwata. Gari na waye da shi na yi tozali a tsakiyar kaina ina yunƙurin magana na ji ya furta min, "Kada laifin wani ya shafi wani domin kin san kama da wane bata wane." Bai jira cewata ba ya ɓace min da gani, a hankali na miƙe ina zagaya lungu da saƙon wurin tafiyata keda wuya na ji Dogaran Sarki sun zo da shelar kiran gaggawa da Sarki Damina yake yi ga waɗanda aka kai ɗakin yarima.

Wannan shine shafi na biyun ƙarshe na free pages. Hajiyata kada ki bari a yi wannan tafiyar domin wasan yanzu ya fara ɗaukan zafi💃 Wai ko dai Yarima ya warware ne🥵🤣😂

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰 ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala

cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚
[11/25, 7:00 AM] Ameera Adam🌚: *BAƘAR DAULA*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

Tsokaci: Kirƙirarran labari ne bai faru a gaske ba, ban rubuta don cin zarafin kowacce ƙabila ko yanki ba. Daga sunayen garuruwa zuwa na abin bauta duk ƙirƙirarru ne, kuma ban lamunce a sauya min littafi ta kowacce siga ba tare da izinina ba.⚠️

Last free page 10

🥳 in ka ji busa tabbata Sarauniya ce ta ƙaraso, ina kuke matan ƙwarai, mata ba muna mata ba, shin kin jaraba kayan *HONEY-DROPS* me kike jira har yanzu?, Manyan mata, mata masu aji na ta dafifi wajen kwasar kayan gyara, me ya sa za ki kashe kanki da ƙuruciyarki, ko tsohuwar ma na zuwa karɓar nata, kina fama da matsalar bushewar gaba, ɗaukewar sha'awa da ni'ima, ƙaiƙayi ko ƙurajen gaba, jin zafi yayin tarawa da maigida, sanyi ya taɓa miki mahaifarki?, Kina ta allura da shan magunguna ba su miki aiki ba, wane kalar infection kike fama da shi?, Staphylococcus, Gonorrhea, Syphilis, UTI, STDs ne?, Share hawayenki kukanki ya ƙare je ki nemi *HONEY-DROPS INFECTION FLUSHER* ke da sanyi sai dai ki ba da labari, kin gama cacar kuɗi, cikin kwana uku zaki fitsarar da duk wani sanyi da dattin da ke tattare a

mararki, ki gyara zamanki gidan aurenki don sanyi kashe mace yake har buzunta, duk wani magani da za ki sha muddin da sanyi a jikinki iyakar shi cikinki, ba zai sauka ba. Magani ne ingantacce made of herbs, In kin gama da wannan akwai na gyaran other room, akwai Exclusive Gumba ta manyan mata ke nan, ko matar Gwamna ita take sha, ga Gumbar babbar mace mai tada tsohuwar soyayya, akwai fa tsuumi na matan gaske, akwai *HONEY FLOOD TSUUMI* kan ƙiftawar ido ni'ima ta yi ta kwararo miki, akwai BUJENTA JAGAB, da Tsuumin Ɗafau, daga jin sunan kun san akwai zance na bar muku ku ƙarasa, akwai sauran kaya masu zafi🔥

Muna da bridal package

Diamond - 100k
Gold - 50k
Silver - 30k

Ga kuma na postpartum (wanda suka haihu don dawo da martabarsu)

Diamond - 50k
Gold - 30k
Silver - 15k

Kuna iya samun mu ta 08167888934, ko 08067770852

Ba ƙaramin ruɗu da tsananin mamaki ya shiga da faruwar lamarin, a saninsa duk rana kamar wannan matuƙar ya miƙa kuka da buƙatarsa ga Sarauniya Shakundum tana share masa hawaye ta hanyar amsar buƙatunsa. Koda ta daina yin magana amma akwai alamun da yake ji na amsar addu'a da roƙon nashi. Miƙe wa ya yi tsam daga wurin da yake ya fara kai kawo a cikon kogon dutsen cikin mamaki, bakin wani baƙin kasko ya tsugunna ya ɗebo garin sihirtacciyar bishiyar kukar da ya taɓa aika wani ɗan autan aljanu ya ɗebo masa a dajin Buzurul-shusu. Barbaɗawa ya yi da zummar ya ga ainihin abin da yake faruwa da Gunkin Sarauniya Shakundum, kasancewar a ƙa'ida idan har Almuru ya yi babu shi babu ziyartar muhallin Gunkinta. A maimakon komai nata ya bayyanar masa sai gani ya yi wutar ta ɗauke, ya gwada haka ya fi a irga daga haka jikinsa ya ba shi tabbas akwai wani sabon al'amari da yake faruwa. Don haka a gaggauce Boka mai zamani ya ɗauko madubih sihirinsa yana karkatar da shi kusurwar kudu ya fara karanta waɗansu irin ɗalasuman tsafi tun bai ƙarasa ba ya ga jini ya ratsa ta jikin mudubin yana ɗiga. Da sauri a jiye saboda sababbun al'amuran da yake gani masu rikita lissafi, ko tunanin me ya yi sai ya sake ɗauko mudubin yana bincike game sauran al'amuran da ke faruwa a cikin Daular. Tamkar an saka masa hoto a majigi haka ya riƙa ganin duk abin da yake faruwa, yana sake karkata mudubin zuwan binciken Sarauniya Shakundum kamar wancen karon haka ya sake ganin jini na ratsowa ta cikin madubi. Yana nan zaune yana ganin abin da yake faruwa sai ganin wata ƙanƙanuwar wuta ya yi harshenta na ratsowa ta

tsakiyar madubin, ruwan tsafinsa da ke ƙoƙon baƙin ƙarfe mai ɗauke da waɗansu irin zanen baƙaƙen aljanu ya ɗauko ya watsa. Amma abin da ya sake tsinka hanjin cikinsa yadda ya ga wutar ta taso masa gadan-gadan har sai da ta fara lasar naman jikinsa. A firgice ya riƙa ɗaukan abubuwa yana jefawa don ya samu wutar ta mutu amma kamar ƙara mata makamashi yake yi, babu shiri ya ƙarasa bakin wani gajeren kabari ya ɗebi ƙasar saman kabarin a tafin hannunsa. Nan take ya fara kiran sunayen aljanu, sai da kira sama da goma sannan ya rufe idonsa yana kiran Aljanu Gagare,  ya jima yana abu ɗaya sannan Aljani Gagare ya bayyana tare da faɗin, "Me yake tafe da kai a tsohon daren nan ya kai wannan tsoho mai surkulle kala-kala?" Bakin Boka mai zamani na rawa ya furta, "Ka taimaka min Ubangidana Kogon tsafina ya kama da wuta sha'anin Sarauniya yau ya zo da wani irin salo." Yana rufe baki Aljanin ya bushe da dariya mara daɗin saurare sannan ya ce, "Wannan wajibi ne a gare ta domin matuƙar kiɗa ya canja dole rawa ma ta canza. Sarauniyar da ka sani a baya ta bambamta da ta wannan, don haka ka yi takatsantsan wurin tsaurara bincike a kanta idan ba haka ba watarana za ka nemi rayuwarka ka rasata gabaɗaya." Ganin wutar na sake ruruwa ya sa Boka ya ce, "Na ga alama amma ka taimaka min da abin da zan kashe wutar nan ina cikin tashin hankali." Aljanin na jin haka ya ɗiga masa wani yelon ruwa akan ƙasar kabarin tafin hannunsa yana cewa, "Ka murje ta da ƙasar hannunka sosai sannan ka je ka watsa wa wutar, wannan ruwan da ka gani fitsarin ɗan autana ne na lakuta maka shi da ƙasar kabarin can su za su kashe wutar." Da sauri Boka mai zamani ya ƙarasa wurin da wutar take ci, yana watsawa kamar ɗaukewar ruwan sama haka wutar ta ɗauke sai wani irin hayaƙi mai wari da yake tashi a wurin. Daga can gefe Boka mai zama ya zauna yana sauke ajiyar zuciya ya dubi Aljanin yana faɗin, "Lamarin nan ya matuƙar gigita tunanina." Aljanin ya yi dariya mai kama da haniniyar doki sannan ya ce, "Na gaya maka wannan kaɗan ne ka gani matuƙar za ka tsaurara bincike a kan Sarauniya Shakundum." Yana rufe baki ya ɓace daga wurin. Yadda boka mai zamani ya ga rana haka ya ƙarasa ganin darensa idanunsa biyu yana saƙa da warwarar abin da yake daminsa, yau kaɗai ya sake tabbatar da zarginsa na baya. Ajiyar zuciya ya sauke yana gyaɗa kai sannan ya saki wani shu'umin murmushi ya ce, "Tabbas sai yanzu na fahimci kuskurena. Da alama Shakundum ta bayyana a cikin daular nan kamar yadda bincikena na baya ya nuna min tana gabda ƙarasowa Daular nan. Yanzu zamana a cikin kogon tsafin ba shi da wani amfani domin wacce nake zaune domin ita ta bayyana har ta bar cikin kogon nan, amma kuma zan zuba ido na ga abin da zai ci gaba da wakana a cikin Daular. Matuƙar na ga manyan alamomin da nake zargi tabbas kashina da na Usaina ya kusa bushewa. A zabure boka mai zamani ya miƙe kamar wanda aka tsirawa allura a cikin ido, gaban ƙoramar sihiri ya koma ya tsugunna ya hau binkice game da abin da ya shafi Sarki Damina da ƴaƴan cikinsa.

Ras! Ya ji gabansa ya yi mummunan faɗuwa bisa abin da idanunsa suka yi masa tozali da su, Sarki Damina ya gani ya bayyana sai waɗansu haske huɗu da ke zagaye da su. Daga bangaren gabas ya hangi wani ƙaton haske wanda ya shafe sauran gabaɗaya, hannu ya saka da niyyar shiga halararsa ya bincika alaƙarsa da Sarki Damina amma sai ya ga duhu ya mamaye wurin, duk iya bakin ƙoƙarinsa ya gagara gane abin da yake son gani. Cike da mamaki ya furta, "Kar dai wannan hasken ma yana daga cikin zuri'ar Damina? Kai an ya kuwa haka ba zai taɓa yiwu ba. Ya zame min wajibi na nemi Usaina mu tattauna domin mu samu mafita."

Kafin Sarki Damina ya ƙarasa gidan shaƙatawarsa tuni aka tuɓe su kandala kowacce sai kare jikinta take yi cikin jin kunya kasancewar haka bata taɓa faruwa da su ba, lokacin da ya ƙarasa yana shiga ya hau ƙare musu kallo ɗaya bayan ɗaya yana lashe baki domin ya jima bai haɗu da kyawawan ƴanmata kamar su ba. Kowacc ya je gabanta sai ya saka hannu ya ɗago haɓarta ya ƙare mata kallo tun daga sama har ƙasa sannan ya wuce wurin ta gaba da ita. Nan take ya ji zuciyarsa ta yi matsanciyar kamuwa da ƴanmata biyu daga cikinsu, kamar dabbobi haka ya saka su a gaba yana mu'amala da su, idan ya gama da wannan sai ya koma kan waccen. Ban da kuka da roƙo babu abin da suke yi masa, kallon Kandala ya yi wacce yake kwance share-share a jikinta ya furta, "Yan mata kukan me kike yi bayan a yadda na jiki kin saba, ba ni na fara sarrafa linzaminki ba?" Kuka ta fashe da shi a hankali ta furta, "Abar bauta ta shiga lamarinka amma ka taimaka ka ƙyale mu ya shugaba nagari." Duk da ya ji daɗin lafazinta duba da ƙanƙantar shekarunta ya sa ya dube sosai yana cewa, "Ba ma buƙatar jin wani abin bauta bayan Sarauniya Shakundum." Gyaɗa masa kai ta yi cike da gamsu, a yadda ta ji muryaraa ta yi tsammanin zai rabu da su kamar yadda ta roƙa amma sai ta ji ya sake lalubarsu yana ƙoƙarin biyan buƙatarsa. Babu yadda suka iya suna ji suna gani ya yi abin da zai yi da su ya gama sannan ya dube ta ita da Saro ya furta, "Daga yau ke da ita kun zama matan huce zafina." Za a bar ku a nan duk lokacin da na buƙace ku zan zo na same ku, kuma duk wacce ta nemi musamin zan sa a ɗauki mummunan mataki a kanta." Daga haka ya ɗauki wasu manyan ganyaye da yake rufe al'aurarsa ya ɗaura a ƙugunsa ya fice. Dakarun da ke bakin ƙofar turakar ne suka shiga suka fisgi sauran mutum ukun suka fita da su, aka bar daga Kandala sai Saro. Lokaci ɗaya suka rungume juna suna matsanancin kuka, kamar daga sama suka ji shigowar wasu ƴanmata wanda ko ba a faɗa musu ba sun fahimci bayi ne. Sababbin ganye suka kawo musu da abinci mai kyau sannan suka kalli su Kandala suna faɗin, "Tabbas kuna cikin masu daraja tun da a yau haɗuwarku kaɗai da Sarki har ya ƴanta ku. Ku taimaka ku roƙar mini Sarauniya Shakundum ta sassauta min baƙar wahalar da nake sha." Daga Kandala har Saro babu wacce ta tanka mata sai binta suke yi da kallo, don su ko kaɗan wannan ƴantawar bata faranta ransu ba.

Asubar fari a sirrance Boka mai zamani ya rikiɗa zuwa siffar Tsuntsun kai tsaye ya tashi ya nufi cikin gidan Sarki Damina, daga kan katangar ɗakin Usaina ya tsaya yana wani irin kuka da ba kowa zai fahimci inda kukan ya dosa ba. Cikin bacci Usaina ta yi mafarki da Boka mai zamani yana tsala matsanancin gudu ga wata baƙar guguwa na biye da shi, tana daga nesa har suka tunkarota gadan-gadan. Duk yadda ta kai ga yin gudu abin ya gagara ko ƙafarta ta gagara motsawa, don haka ta fara karara ihun neman ceton sai dai bata yi aune ba baƙar guguwar ta turnuƙe su gabaɗaya. A zabure ta tashi zaune jikinta na rawa, sai da ta buɗe idanunta ta riski kukan tsuntsun kamar yadda ya saba zuwar mata a duk lokacin da yake da wata muhimmiyar magana da ita. A hankali ta miƙe ta fice ta bar Sarki Damina buɗe da baki yana sakin munshari. Tana fita ta buɗe wani ɗan ƙanƙanin ɗaki da je can nesa da ɗakinsa tsuntsun na ganin haka ya rufa mata baya. Sai da ya yi girgiza ya dawo suffarsa ta ainihi Usaina ta dube shi ta ce, "Mai zamani akwai matsala." Boka ya dube cikin damuwa ya ce, "Ita ce take tafe da ni. Ni na ga masifa yau ganin idona." Nan take ya bata labarin duk abin da ya faru a kogon Tsafinsa, tana gama jin jawabinsa ita ma ta zayyana masa abin da ta gani a mafarkinta sannan ta ɗora da cewar, "Sirrantaccen bawana ya sanar da ni abin da ya hana ni bacci, wannan baccin ma da ya

ɗauke ni ɓarawo ne kuma rabon zan ga wannan mafarkin ne. Ya sanar da ni an kawai Yarima yanmata shabiyar kuma tun da ya gama mu'amala da su yake wani irin bacci da bai taɓa yin irinsa ba. Yana farfaɗowa ya fara wani irin tarkacen amai, kasan aman me aka ce min ya yi?" Boka ya girgiza mata. Usaina cike da damuwa ta ci gaba cewa, "Ina laƙaninnikan da ka ba ni na bashi yana yaro?" Boka ya gyaɗa kai.Ta sauke ajiyar zuciya ta ce, "Su ya amayar an ce har da baƙar allura da kan maciji. Kai ba za su lisaafu ba kuma wai yana dawowa hayyacinsa ya fara cewa me yake yi a wannan gidan. Mai zamani in taƙaice maka labari alamu sun nuna Yarima ya dawo hayyacinsa don har ni da Damina mun je mun gano halin da yake ciki." Boka mai zamani ya yi taku biyu jiki a sanyaye ya ce, "Ta faru ta ƙare... Amma duk da haka ba za mu tozarta ba zan kira Manyan baƙaƙen aljanun ƙarƙashin ƙasa na nemi agajinsu. Abu ɗaya nake so da ke." Usaina ta zuba masa ido tana jiran jin ta bakinsa, boka mai zamani ya ci gaba da cewa. "Ko da wasa kada ki yadda Damina ya lura da halin da kike ciki. Ki sani har yanzu yana kallonki da sunan Hasana, ki nuna masa kin fi kowa farinciki da samun lafiyar Yarima haka zai sa mu sake samun yadda za mu murƙushe rayuwarsa." Usaina ta saki dariyar ƙeta tana faɗin, "Kada ka manta ni ce fa Usaina. Bari ka ji ko ni ina tsoron shu'umancina ba don komai ba sai don sanin makircina. Waɗannan ƴanmata sha biyar da aka kai wa Yarima dole su baƙunci lahira ko ta tsiya ko ta arziƙi. Kuma samun lafiyar Yarima ba shi zai sanyayar da ni ko ya ba shi damar ɗarewa karagar mulki ba, na yi rantsuwa da tsantar makircina ko da Hasana za ta dawo Daular nan Damina ba zai taɓa aminta da ita ba balle Yarima da nake kallo a tafin hannuna nake iya sarrafa linzamin rayuwarsa yadda nake so." Cike da jin daɗi Boka ya ruƙo ƙugun Usaina ya ce, "Ba don ni nake haɗa miki kayan mallaka ba da sai na ce an ya ba maƙale mata kika yi min ba Usaina? Ba na gajiya da ke da duk wani abu na jikinki, a yanzu da za ki ba ni dama da na huce tulun zafin da ɗauko daga cikin kogona. Amma yanzun ma ba zan ce komai don kin wuce tunanin duk wani mai tunani shalelena, ina fatan dai watarana ba za ki harba min ƙarinki ba dom ba zan iya jurar budulcinki ba." Usaina ta ci gaba da hillatar boka mai zamani tuni suka faɗa duniyar masha'arsu cikin kissa ta furta, "Ka bar min komai a hannuna sauran bayanin za ka ji daga baya. Mai zamani idan na yi maka butulci ai sai na ɗaiɗaice wa nake da shi da zan jingina na ji daɗi. Wancen lusarin mijin nawa kowa?" Boka mai zamani ya taɓe baki ya ce, "Haba Usaina ko kin manta na san kuna ƙulla irin wannan alaƙar da wannan sirrantaccen bawan na ki." Sai da gaban Usaina ya faɗi amma da yake ta ita bariki sai ta wayance ta ce, "Hmm idan wannan bawan ne kar ma ya dame ka domin ina nuna masa kulawa ne domin biyan buƙatar kaina ya ci gaba da yi min biyayya yana kawo min saƙƙonni. " Tana gama maganar ta ci gaba da rikita mai zamani da salo kala-kala.

Lokacin da Sarki Damina ya tashi daga bacci tuni Boka mai zamani ya gama abin da zai yi ya yi gaba, da tarairaiya ta tarbe shi sannan ta furta, "Na yi mamakin yadda ka iya yin bacci a daren yau." Murmushi ya yi yana shirin magana ta ci gaba da cewa, "Farincikin samun lafiyar Yarima ya fi min komai don haka yau ko kaɗan ban runtsa ba. Idan ban manta ba rabona da farinciki irin wannan tun kafin samun ciwon Yarima yau sama da shekara ashirin da wani abu. Kai gaskiya mun gode wa Shakundum ta dubi roƙon da muke yi na tsawon shakaru."Sarki Damina ya faɗaɗa fara'arsa yana faɗin, "Hasana ban da bacci ɓarawo ne babu abin da zai hana ni kwana idanu biyu, kin ga maganar boka mai zamani ta fito fili da ya ce min Yarimana zai warke. Sai dai wani hanzari ba gudu ba, ya ce min yarinyar da zai kusanta ita ce silar samun

lafiyarsa kuma har da albarka Ɗa ko Ƴa a tsakaninsu." Ras! Gaban Usaina ya faɗi, a zabure ta furta wannan saduwar da ya yi da su ko kuma wata nan gaba?" Kai tsaye Sarki Damina ya ce, "Wannan dai kin ga ya zaman wajibi na sa a binciki yarinyar don dole Yarima ya aureta tun da na lura alheri ne tattare da ita kuma ƴar baiwa ce." Usaina ta fara sosa kai wani abu na taso mata mai ɗaci a maƙogaro sai kuma ta wayance da cewar, "To mai zai hana ka sa a tara ƴaƴan nawa a bincike su idan aka gagara ganewa ka ga ba sai ka saka a killace su ba, idan aka killace a wani gidan ana kula da su da sannu za a ga wacce take da juna biyu a cikinsu. Idan kuma haka bai yi ba sai ka saka Boka mai zamani ya yi maka bincike a kansu." Cike da jin daɗin shawararta ya rungumeta yana buga bayanta ya ce, "Shi ya sa nake ƙaunarki Hasana, ke wallahi kin ga dai ƴar uwarki Usaina ta mutu ko amma ko ita da kuka kasance ƴan biyu ba za ta nuna miki kaifin basira da tunani ba domin sam hali da tunaninku ba ɗaya ba." Wani abu ne ta ji ya soki ƙirjinta har sai da fushinta ya baiyyana a fili, ganin haka ya sa Sarki Damina ya yi tsammanin ko don ya faɗi wannan maganar game da ƴar uwarta ne ta ji haushi, cikin lallashi ya furta. "Ki yi haƙura ban faɗa don na ɓata miki ba sai dai yabon gwani ya zama dole." Usaina ta wayance tana murmushi ta furta, "Wannan haka ne. Yanzu dai idan an jima zan leƙa na ga sauƙin jikin Yarima, idan ya so sai ka yi yadda na bada shawarar ina ganin zai fi." Sarki Damina ya amsa mata. Daɗi ne ya kamata don ta san duk shawara ɗaya da ta bayar idan aka ɗauketa dole za ta samu mafitar da za ta hallaka su lokaci ɗaya ba tare da wani ya zarge ta ba.

Shiru na yi lokacin da na ji shela da sanarwar da aka bayar daga wurin Sarki, a tunanina zan iya ɓaddabami na saje da sauran bayin cikin wurin da muka samu a wurin, ina gani wasu daga cikin tsirarun ƴanmatan da aka tafi da mu suka fita wurin mai shelar. Ni da sauran mutum huɗu muka yi shiru kamar ba ma daga cikin waɗanda ake yi wa sanarwar, wani abin mamaki sai ga Dakarun na zaluƙo mu ɗaya bayan ɗaya duk da babu wani abu da za ka kalla wanda ya bambamta mu da waɗancen, idanu ne ya dawo kanmu nan take tsoro da fargaba suka mamaye zuciyata musamman da na tuna irin halin da muka baro yarima a ciki yana wani irin bacci da ban taɓa ganin irin munsharinsa ba. Hawaye ne ya zubo min na fara ayyana irin gashin-kumar da za a yi mana domin har lokacin matar da muka samu an farkewa ciki ta gagara ɓace min daga idanuna ba, kuka nake sosai saboda tausayin hukuncin da za mu fuskanta. Ganin haka ya sa ƴan uwana da aka tafi da mu tare suma suka mara min baya kowacce na zubar da ƙwalla, a gaban dubban jama'a aka sake jere mu sarki da muƙarrabansa suna cikin tanti a zaune. Karaf idanuna suka hango min shi a zaune kusa da Mahaifinsa, a wannan karon tsaf na gan shi cikin kyakkayawar shiga duk da ba wata sutura ce a jikinsa face ganye. Amma kana ganinsa za ka bambamce yanayin nutsuwarsa saɓanin jiya da muka same shi a hargitse, a hankali na furta, "Ko kaɗan ba zaci cutarwar da kake min a baya ta kai haka ba, sai ga shi ka raba ni da ƙimata da mutumcina da na jima ina yi wa Goga tanadi..." Maganar da Sarki Damina ya yi ce ta katse min kalamaina, ya miƙe tsaye yana kallon al'ummar da ke wurin yana faɗin, "Ya ku al'ummar cikin wannan Daula, ku yi sani Yarima Ɗana ɗaya jal tilo ya samu lafiya. Ya samu lafiya ne kamar yadda boka ya faɗa min a baya sanadiyar waɗannan ƴanmatan, don haka ya zama wajibi a gare mu; mu killace su domin suna daga cikin masu daraja." Yana rufe baki na ji duka sun ɗauki sowa da tafi cikin farinciki suka shiga raye-raye da bushe-bushe, sai da suka ɗan jima sannan Sarki ya ruƙo hannun Yarima ya fara takowa har gabanmu, tun da na ga haka gabana ya ci gaba da faɗuwa ina tsoron kada ya nuna ya sanni domin na san babu tantama shi ne

mutumin da ke fitowa daga cikin tawagar da ke baƙuntar rayuwata. A hankali ya fara nuna masa mu ɗaya bayan ɗaya sannan ya bashi labarin zuwanmu da kai mu wurinsa da aka yi, bai tanka wa mahaifinsa ba illa gyaɗa kai kawai da na ga ya yi sannan suka koma suka zauna. Wurin zama aka nuna mana sannan aka kawo mana kayan ciye-ciye da lashe-lashe. Ina kai loma ɗaya bakina na ji ta min ɗaci sakamakon tuno iyayena da ƴan amanata da na yi, hawaye na goge a fakaice sannan na ci gaba da turawa ba don ina jin daɗinsa ba. An jima ana shagali sannan daga baya aka ɗauke mu daga wurin aka kai mu cikin gidan Sarki Damina, a wani ɗan ƙaramin gida aka sauke mu aka ba mu duk wani kayan buƙata tamkar waɗansu ɓangare daga jinin Sarki Damina.

Daga wurin taron kai tsaye Sarki Damina wurin Boka Mai zamani ya wuce, duk abin da yake faruwa ya zayyane masa da neman taimakonsa. Boka mai zamani yana son yin bincike a gaban Sarki mai zamani amma yana gudun kada wani abu ya faru marar daɗi har Damina ya ga gazawarsa. Don haka ya ƙarfafa masa gwiwa akan hukuncin da ya yanke na killace ƴanmatan a wuri ɗaya kafin cikin da ake tsammani ya bayyana. Cike da murna Sarki Damina ya miƙe har zai je bakin ƙofa Boka ya ce, "Damina ina fatan baka manta al'adar Daular nan ba ko?" A hargitse  Sarki Damina ya juya yana faɗin, "Ta me fa?" Cikin rashin damuwa Boka ya ce, "Har ka manta sadaukarwar da ka yi wa Babban dodo abin da ka haifa na fari? Sanin kanka ne duk wani Sarki ko mai jiran gado dole ne abin da za a haifa masa na fari a sallama wa Babban dodo, idan kuma ba haka ba ka san abin da ya wakana ga mahaifinka kafin baƙuntarsa lahira." Dariya ya bushe da ita mai ƙarfi sai da ya yi mai isarsa ya kalli Boka ya ce, "A halin nake ciki ko uwarsa ka ce na sallamawa Babban Dodo zan bayar da ita balle abin da za a haifa masa, na yi alƙawarin a lokacin da yarinyar da ke ɗauke da cikin Yarima ta haihu ko mahaifa ba za ta kai ga faɗowa ba Jaririn zai dangana ga Babban dodo. Buri da fatana dama Yarima ya samu lafiya yadda zan samu magaji kuma ya samu ban damu ba, don haka idan ka cire Yarima da ni zan iya fansar da gangar jiki da ruhin kowa." Yana gama maganar ya fice daga kogon dutsen. Jinjina kai Boka mai zamani ya yi ya ce, "Tabbas kuwa ka yi shuka a idon makwarwa waɗannan kalamai naka tamkar a kunnen Usaina ka yi su."

Zamanmu a cikin gidan Sarki Damina babu yabo babu fallasa domin duk wani abin buƙata babu wanda muke nema mu rasa, sai dai tuni kwanciyar hankali ta yi ƙaura a gare saboda kullin tunani ɗaya a wane hali iyayena da ƴan amanata suke. Ga ƙarin takaici ɗan gidan da aka kai mu a ciki muke rayuwa ko soro ba a bari mu je, sa dai kusan kullin Mahaifiyar Yarima takan kawo mana ziyara, a yadda na lura macece mai mutumci da sakin fuska. Kullin cikin jammu a ciki take tana kawo mana hira masu daɗi da kwantar da hankali, don haka ya sa a duk lokacin da ta shigo wurinmu take tambayarmu matsalolin da ke damummu. Kwananmu goma sha biyu a cikin gidan na fara ciwon kai mai zafi ga yawan kasala da tashin zuciya, sautari a duk lokacin da na ci abinci sai dai na fakaici idanun sauran ƴanmatan da muke tare na tafi banɗaki na kyalaya amaina a can, wannan sauyin da na gani ba ƙaramin ɗaga hankalina ya yi ba domin duk wasu alamin ciki ya bayyana a jikina, ranar da mahaifiyarsa ta shigo wurin mu da yamma haka kawai na ji turaren jikinta na tayar min da zuciya. Na tsugunna ina gaishe na ji na gagara daurewa sakamakon aman da nake jin ya taso min, da gudu na nufi bakin rariya na fara amai kamar zan amayo da ƴaƴan cikina. A wahalce na dawo ina shirin zama mahaifiyar Yarima ta

ruƙo hannuna tana duba tafin hannuna, tana gama duba hannuna ta gwala idona tana ƙarewa ƙwayar idona kallo. Sunkuyar da kai ƙasa na yi na ji ta ce, "Tun yaushe kika fara yin aman nan?" A hankali na furta, "Yau kwana uku."

Tirƙashi! Tabbas yanzu wasan ya fara, kurunkus dai tun da Usaina ta fahimci Kyauta na da ɗan bayani a jikinta🤣🤣🤣 Sai dai akwai ƙura fa wai za a sadaukar da abin da ke cikin Kyauta😰😰😰 Me kuke harsashe shin za su nasara ko yaya? Ina labarin iyayen Kyauta? Shin Kandala ta hallata ta zama matar Sarki Damina kar fa aje allura ta tono garma? Wane ne mai kama da Yarima da yake baƙuntar Kyauta shin wane katon haske Boka ya gani a gefen Sarki Damina? Meye alaƙar Kyauta da Sarauniya Shakundum, kuma me ya sa boka ya gagara gano bincike a kanta? AKWAI TAMBAYOYI DA YAWA DA CI GABAN LABARINE ZAI FAYUACE MUKU💃 Wollah na gaya muku salon labarin nan na daban ne kada ku bari a yi babu.🤭

*KU MATSO KU TAHO*💃

Wannan labarin salonsa na daban ne💃 cike yake da sarƙaƙiya da tsananin ban tausayi😰 ku dai kar ku bari a yi babu ku.🏂

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 400 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Idan kati ne MTN. Idan kika bari na kammala cmplt 700 ne.

Idan kin san kin sayi ɗaya daga cikin litattafan nan *AN YA BAIWA? KO DUBU JIKAR MAI CARBI KO ZAUJATU JINNUL-ASHIQ* za ki biya 300 wannan ragin na waɗanda suka sayi wannan littafan nan ne kaɗai.💃

Na ɗaga hannuwa riƙe da takobi da kwari da baka na salaƙe na sunkuyar da kai ina miƙa gaisuwa da kirari cau cau cau cau, sai ni Ameera 'yar Alhaji Adamu Amiriyan Mamanta, uwar Aslam da Ayman Amanar Oganta turmi sha daka 🥰
Wiiiiiihuuuuuuhuuuu mace mai kamar maza ko cikin maza sai an duba domin wuya ake yi wa lissafi daɗi sai an jinkirta. Allah dai ya biya wuya a ƙofar Na'isa, wuya a ƙofar Kabuga wuya a ƙofar Nasarawa wuya a doka wuya, wuya a ƙofar kansakali mun buga a dajin Jemagu mun buga a dajin Falgore ko dajin Sambisa albarka. Sai ni ƴar Kanawan dabo amanar mutanen Rigana, idan ka ga matsoraci ko rago a Rugana baƙo ne domin jarumi ba'a nuna masa hanya, sa'a dai 'yar gaban goshin *FIRST CLASS WRITER'S* Amanar Marubuta La'ilaha'illahu. Sai ni ta hannun Matar Habibu ni ce dai ƙawar Mum Amnash amanar Masoyanta, cau cau cau cau makaranta ku matso ku ji wannan kafcan don idan kika bari aka yi babu ke an barki a baya. Domin duk wacce ta bari aka yi wannan tafiyar babu ita ta fita daga cikin jaruman mata masu aji.🌚

*Ummou Aslam Bint Adam*🌚

[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

© *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 2

https://chat.whatsapp.com/J0qrgC0rXNQ57u50VzeewR

A hankali Jabun Raihan ta fara bin ɗakin da kallon, miƙewa ta yi ta fara buɗe drowers ɗin kayan Raihan sai kuma ta bi hotunan ɗakin Raihan da ke maƙale a jikin bango tana kallo ɗaya bayan ɗaya, tana jin motsi ta koma wurin kayan abincin ta zauna. Kallon abincin take don sam bai burgeta ba cikin zuciyarta take mamakin irin abincin bil'adam don ita bata ga abin daɗi a ciki ba. Goggo ce ta turo ƙofar tana faɗin, "Rehanu! Ke Rehanu wai ina kika shiga ne tun jiya ban ji wulgawarki ba, yarinya sai iya shege don kin ga na damu da ke." Turus ta yi tana kallon Jabun Raihan da ke cin abinci tana yamutsa fuska, daƙuwa ta yi mata da hannu tana faɗin, "Kin ci ƙaniyarki Rehanu dama kina jina kika yi shiru to kin wulaƙanta uwarki Abu. Meye wannan ɗin kike ci kina yamutsa fuska kamar abinci?" Jabun Raihan a daƙile ta ce, "Gashi kuwa kin gani."

Goggo ta shiga ɗakin ta yi tsaye a kan Raihan tana faɗin, "Oho dai kowa ya raina uwar wani tashi ya raina, wallahi duk maganar da kika gaya min uwarki da Ubanki kika gayawa." A fusace ta ɗago tana duban Goggo da ke tsaye tana zazzaga ruwan masifa, farantan gabanta ta kalla tana motsa baki lokaci ɗaya ta cinye abincin ciki sai kwanukan, tana kallon Goggo kamar wacce ta basu umarni sai farantan suka yi tsalle zuwa gaban Goggo, wuƙar da Mama Uwani ta haɗowa Raihan don ta riƙa yankar farfesun ƙafar sa ce ta yi tsaye a daidai fuskar Goggo saitin idonta tana wani juyi, kamar za ta tsokane mata ido. Jabun Raihan ta kalli Goggo fuska ba walwala tana cewa, "Kika sake zagar mini iyaye sai na tsokane idonki, ke da sake gani har abada. Wannan kwanukan kuwa sai na basu umarni su yi ta ranƙwale miki kai har sai sun illataki." Goggo daskarewa ta yi a wurin, tuni fitsari ya jiƙe mata zani gumi sai yanko mata yake ta ko'ina. Tun Jabun Raihan bata gama magana ba, Goggo ta juya da gudu tana ƙawalawa Mahaifiyar Raihan kira, sai dai yadda ƙafafuwanta suka yi mata nauyi ya sa ta fice da rarrafe zanin jikinta kuwa tuni ya samu mutsuguni a bakin ƙofa.

Tana fita Jabun Raihan ta miƙe tana kaiwa da kawowa don gabaɗaya zaman wurin ya gundureta, abin da ya sa ta bi umarnin Huzaifa don biyan tata buƙatar amma ba don haka ba babu yadda za a yi ta amince da rayuwa cikin siffar bil'adam.

Huzaifa bai tsaya ko'ina ba sai cikin wani ƙasurgumin daji mai ɗauke da jajayen furanni, da

jajayen ƙoramu. Komai na wurin ja ne hatta ciyayin da suke wurin, sai waɗansu korayen kifaye da su kaɗai ne suka bambamta da jajayen abubuwan da ke wurin. Kan wani jan dutse ya kaita ya kwantar da ita nan take ya fara gyara mata jikinta, kafin wani lokaci tuni ya gyara mata jikinta ya ɗauko wani ƙaramin jariri da ke kwance cikin wata ƙorama mai ɗauke da siffar kunkuru, sai dai kansa ɗauke yake da kawuna huɗu kowanne da surarsa. Akwai kai mai siffar jaki, agwagwa, mage da mai siffar kifi, a kowanne kai akwai manya kahunhuna guda biyu, daga jelar hallitar ɗauke take da tafkeken kan maciji. Yana zuwa ya ɗora shi a gefenta sannan ya ɗaga hannunta ya tura shi ƙarƙashin jikinta kamar yadda uwa take rungume jaririnta. Nesa da su ya koma yana sakin murmushin farinciki a fili ya fara faɗin, "Na jima ina burin haka ban samu dama ba domin gudin abin da zai ɓata miki rai, sai dai a wannan karon dole na ɗau wannan matakin domin haka ne kaɗai sai tseratar da ke daga kaidin Mugaza, idan ba haka ba duk yadda za ta yi sai ta halaka min ku. Ni kuma ba zan juri rabuwa da ke ba wanda ya nemi raba ni da ku zan iya hallaka shi ko wanene, ko da kuwa Mahaifina ne Jingas." Yana gama magana ya ɗaga dutsen da Raihan take kwance da jaririnta, naɗe su ya yi cikin wani kogon dutse sannan ya hura wani kogi da korayen kifayen nan suke ciki, nan take ruwan ya dare Huzaifa ya jefa su ciki ya sake hura ruwan ya haɗe gabaɗaya.

Mommy na daga falo ta fara jiyo muryar Goggo na ƙwala mata kira, da sauri ta nufi wurin da ta ji muryar Goggo tana zuwa ta yi turus ganin Goggo na rarrafe daga ita sai ɗan fatari. Da sauri ta sunkuya tana faɗin, "Goggo lafiya kuwa ko ƙafar ce ta motsa?" Tun bata rufe baki ba Goggo ta ci gaba da faɗin, "Abu ki dubi Allah da ma'aiki ka mayar da ni Albasu wallahi na yafe zaman gidanki, ki maida ni Albasu na mutu cikin aminci tun bata tsaface ni a gidan nan ba." Goggo na maganar hawaye da majina na zuba, a gefe ɗaya fitsari ne ke zuba don Goggo ta yi fitsari daga ɗakin Raihan zuwa babban falo ya kai sau uku.

A ɗan tsorace Mommy ta waiga tana faɗin, "Goggo lafiya kuwa wace ce ta zama matsafiya?" Goggo ta fyace majina da gefen zaninta ta ce, "Wa kuwa kika sani idan ba Rehanu ba. Wallahi yadda na ga tana tsafi ido biyu na ga Annabi haka..." Tun bata ƙarasa maganar ba Mommy ta fara waige tana katseta da sauri cikin ƙasa-ƙasa da murya.

"Goggo don Allah ki daina faɗin haka wallahi Alhaji yana gida kar ya ji abin da kike faɗa, kin san fa baya kawaici a kan yarinyar nan Raihan." Tana rufe baki Inno ta ƙaraso wurin tana faɗin, "Allah ya tonu asirinku, ashe gulmar Ɗana kuke da jikalleta to ahir ɗinku wallahi ke Zinaru ki yi ta kanki arziƙi kika zo ci ba zan miki baƙin ciki ba, gida dai gidan Ɗana ne ba a isa a sawa jikata ido." Goggo takaici ya sake cikata tana ganin kamar gori Inno take yi mata, don haka a zafafe ta ce, "Allah ya sa ni na haifi Abulle har ɗan naki ya aura, magana ce na gama ta yau za a mayar da ni Albasu don wannan sheɗaniyar jikar taki ba za ta sayar da kaina ina ji ina gani ba." Inno na jin haka ta yi zaman ƴan bori daɓar sai kawai ta fashe da kuka, da sauri Mommy ta koma wurinta tana rarrashinta amma fir taƙi yin shiru. Suna nan zaune Alhaji Abdallah ya sauko cikin dakakkiyar shadda ruwan toka da hula baƙa, kayan ba ƙaramin kyau suka yi masa ba. Tun kafin ya ƙaraso Mommy ta fisge ɗankwalinta ta rufawa Goggo, yana ƙarasowa ya ce, "Lafiya dai Inno mai yake faruwa?" Inno na jin haka ta rushe da kuka tana faɗin, "Audullahi ka dubi irin sitirar da ka yi wa Zinaru ita da ƴarta amma da yake sun samu wuri wai cin naman ka suke da ƴarka ɗaya

tilo a gidan duniya. Don Allah ko don darajar haihuwa Abulle ai da ɗagawa yarinyar nan ƙafa ina dalili tana uwarta tana cin namanta?" Goggo ta ƙanƙance ido cikin masifa ta ce:

"Audullahi wallahi tun wuri ka san halin da kake ciki, kwarankwatsa dubi Rehanu ta shiga ƙungiyar asiri."

Kamar wanda aka zagi iyayensa haka Alhaji ya ɓata fuska sai da ya haɗiyi yawu mai ɗaci ya ce, "Goggo kin san wa kike faɗa kuwa? Raihan ɗina ce ta shiga ƙungiyar asiri?"

"Ƙarya na yi maka kenan Audullahi?" Goggo ta tambaye shi tana ɗage kai gefe. Shiru ya yi don ya san idan ya buɗe baki a kan Raihan za a iya samun matsala shi kuma yana ganin girman Mahaifiyar matarsa, ba zai so wani abu ya haɗa su ta sanadiyyar Raihan ba. Ganin haka ya sa Mommy ta riƙo hannun Goggo tana cewa, "Goggo ta so mu je ɗaki don Allah." Inno na ganin haka ta fashe da kuka tana faɗin:

"Allah ya fini sanin dalilin da ya sa bai bani ƴa mace ba, amma ya yi mini komai da ya bani Audullahi da ban haihu ba sai na rasa mai kaini ɗaki nima." Tana gama maganar ta kalli Alhaji ta ci gaba da cewa, "Audullahi nima ka kaini ɗaki ba sai an goranta min ba, kuma wallahi aure za ka ƙara don ba za ka zauna da macen da bata ganin mutumcina ba."

Daddy na shirin yin magana suka ji Raihan ta turo ƙofa ta fito fuskarta murtuk babu fara'a, da sauri Goggo ta fara ja baya tana leƙenta. Daddy na ganinta ya saki murmushi ya rungumota yana faɗin, "Barka da fitowa habibtyn daddy." ƙarasowa wurin ta yi ta ce, "Daddy ba dai fita za ka yi ba?" riƙo hannunta ya yi ya ce, "Yanzu ma kuwa don na gama komai."

Fisge hannunta ta yi ta koma kan kujera tana faɗin, "Na faɗa maka gaskiya za ka yarda?" Murmushi ya yi ya ƙarasa wurinta ya ce, "Faɗi babyna."

"Ka haƙura da fita da baƙar mota idan ba haka ba za a samu matsala."

Mommy ta kalle ta tana faɗin, "Raihan me ya sa bakinki baya furta alheri ne? Ke kin san gaibu ne da za ki yanke masa wannan hukuncin." Goggo da ke gefe tana son yin magana tsoro ya hanata. Daddy ya gyara zaman agogonsa yana faɗin, "Baby sai abin da kika ce da wacce kike son da ita." Daga wurin da take ta ce, "Kowacce ka yi niyyar fita da ita amma ban da baƙar." Daga haka sallama ya yi musu Mommy ta wuce raka shi, Raihan na ganin haka ta ƙarasa gaban Goggo ta tsugunna a wurinta tana faɗin, "Wallahi na kuma jin kin danganta ni da ƙungiyar asiri Allah za ki yi mamakina, sai na kaiki Daulatul Jinnul nariy na azabtar da ke." Inno da ke gefe ta karɓe zancen da faɗin, "Wallahi kema kya gaya mata ai ni wallahi ban yafe wannan ƙazafin da ta yi miki ba. Ni dai wannan larabcin da kika yi ne ban san me kika faɗa ba, amma idan za ki tafi da ita don Allah ki kaini na ga yadda Zinaru za ta yabawa aya zaƙinta." Raihan bata bi ta kansu ba ta wuce kan dianning table, saboda yadda yunwa take sasaƙar cikinta don abincin da ta ci babu in da yaje mata. Tana zama ta fara buɗe kulolin da ke wurin nan take ta fara tasa kulolin a gaba, ɗaya bayan ɗaya tana cinyewa, kuloli huɗu ne a wurin

amma da zaman ta ko minti biyar bata yi ba ta cinye abincin ciki gabaɗaya, tare da shanye shayin da ke cikin fulas ɗin ta kora da ruwa sannan ta dawo falo ta zauna. Lokacin da ta dawo tuni su Inno sun wuce sashensu don haka basu lura da abin da Jabun Raihan ta aiwatar ba.

Sanyin da yake busawa a wurin ne ya doki gangar jikinta wanda ya sa ta buɗe idanunta a hankali tana ƙarewa wurin kallo, cikin rashin ƙwarin jiki ta miƙe zaune har lokacin kallon wurin take yi da tsananin mamaki. A hankali wannan jaririyar hallitar ta fara matsowa har sai da ta hau cinyar Raihan, zamanta a cinyarta ya sa ta lura da wurin a zabure ta miƙe tana ƙwalla ƙara haɗe da ja da baya zafin buguwar ya sa hallitar yin can gefe wanda yake nuni da jin zafin da ta yi. Waige-waige ta fara yi tana ambatar sunan mahaifiyarta, kamar daga sama ta riski muryar Mommynta tana faɗin, "Ga ni nan zuwa Raihan."

Tafiya ta fara yi daga wurin da ta fara jin sautin muryar, ta wani lungu ta hango Mommynta ta fito cikin doguwar rigar shadda tana sakar mata murmushi, kallo ɗaya ta yi mata ta ji gabanta ya yu mummunan faɗuwa. Dafa Raihan ta yi tana faɗin, "Kin tashi Raihan?"

Kuka Raihan ta fashe da shi tana faɗin, "Mommy ina ne nan menene wancan abin?" Ta ƙarasa maganar tana nuna wurin da wannan hallitar take rarrafowa a hankali, Mommy ta kalli wurin tana murmushi ta ce, "Taho mu je ki rabu da wancen abin." Har sun fara tafiya Mommy ta kalli Raihan ta ce, "Amma duk wanda zai ce miki ki bishi kar kije wurinsa cutar da ke zai yi ni ce mahaifiyarki babu abin da zan yi miki." Har lokacin Raihan a tsorace take don haka ta kalli yanayin wurin ta ce, "Amma mommy ya aka yi muka zo nan?" A ɗan tsawace ta ce mata:

"Za ki taho ko tambaya ta za ki tsaya yi." Ba musu Raihan ta bi bayan wacce take gani da siffar Mommynta, har sun kusa fita sai gani ta yi Daddynta ya diro da ƙarfin gaske yana faɗin, "Raihan." Da sauri ta waiga wurinsa tana shirin yin magana mai ɗauke da siffar Mommynta ta fara fisgar hannunta tana faɗin, "Karki saurare shi wuce mu je." Da sauri ya ƙaraso wurin rai a ɓace ya fisgi hannun Raihan sannan ya dubi Mai ɗauke da siffar Mommy yana faɗin, "Mugaza ki shiga taitayinki fa, na gaya miki ki fita harkar yarinyar nan ba na son na hukuntaki a kanta amma wallahi idan kika illatata sai na baki mamaki." Lokaci ɗaya ta rikiɗa zuwa wata mummunar hallita mai ɗauke da siffar ƙadangare sai dai kawunanta goma kowanne ɗauke yake da wasu irin manyan harsuna masu kama da kaifin takobi. Da gudu Raihan ta rungume mai ɗauke da siffar mahaifinta tana wani irin kuka tare da faɗin, "Daddy tsoro nake ji." Ilahirin jikinta ban da rawa babu abin da yake yi, rumgume ta ya yi tsam a jikinsa yana shafa bayanta cikin wata irin soyayyarta da take fisgarsa, don karta fahimci wani abu ya sa ya iya riƙe kansa ba tare da kusanceta ba. Wannan abin ba ƙaramin ɓata ran Mugaza ya yi ba, a shammace ta kaiwa Raihan cafka da ɗaya daga cikin harshenta a ƙafa, da sauri Huzaifa ya janyeta amma sai da harshen nata ya samu ƙafarta. Wata uwar ƙara ta ƙwalla sannan ta faɗa jikin Huzaifa wanda yake nuna suma ta yi.

Wata irin mahaukaciyar dariya Mugaza ta fara ƙyaƙyatawa lokaci ɗaya ta murtuke fuska tana faɗin, "Ki je ki da wannan damuwar zan baki rata kafin na sake waiwayo ki." Tana gama maganar ta ɓace daga wurin.

Cike da tausayi Huzaifa da ke ɗauke siffar Daddy ya shimfiɗar da Raihan, a daidai wannan lokacin jaririn hallitar nan ya ƙaraso wurin ya kwantar da kansa a jikinta. Hannu biyu Huzaifa ya sa ya ɗago jaririn idanunsa ɗauke da ƙwallah ya ce, "Mahaifiyarka na fuskantar ƙalubalen rayuwa, amma daga yanzu zan tsaya mata tsayin daka don kare martaba da ƙimarta." Yana gama maganar ya sake ɗora mata shi a kanta yana motsa baki, lokaci ɗaya jaririn hallitar ya ɓace.

Yana ganin ɓacewarsa ya kalli Raihan da ke kwance ya ce, "Daga yau za ka kasance tare da Mahaifiyarka ko baby komai za ka riƙa ankarar da ni kamar yadda ka ankarar da ni kafin Mugaza ta cimma ƙuduri a kanta."

Share hilis🌚

Ummou Aslam Bint Adam🌚
[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

© *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

https://chat.whatsapp.com/J0qrgC0rXNQ57u50VzeewR

FREE PAGE 1

Girma da nauyin cikin da ke jikinta kamar an kifa ƙwarya, bai hanata gudun da take yi na ceton rai ba. Gudu take zabgawa saboda miyagun hallitun da ta yi tozali da su, masu kawo mata farmaki da zimmar cafkar tsohon cikin da ya yi tsini tamkar zai fashe.

Zuwanta bakin wata bishiyar kuka mai duhun gaske ya bata damar tsugunnawa cikin haki, saboda ji take kamar bayanta zai ɓalle gida biyu saboda azaba, ajiyar zuciya take saukewa akai-akai kamar wacce ta shekara tana matsanancin gudu a tsakiyar rani. Daƙe bayanta ta yi wani irin azabar ciwon baya da mara ya sarƙeta kamar ana tsaga marar tata da kaifaffiyar aska. Sannu a hankali ta waiga bayanta don ganin mummunar halittar da ke bibiyarta kamar yanda inuwar mutum take bibiyarsa. Kukan jarirai ne ya fara yi mata amsa kuwwa kamar saukar aradu a tsakiyar ka! Ta ko ina take jin sautin kukan na su kamar kunnuwanta za su tawatse.

Kuka haɗe da dariya ne suke ta shi a cikin dajin, zuwa can ta hango inuwar wata hallita na

tunkaro ta, matsananciyar guguwa ce ke tashi bishiyoyi na kaɗawa da ƙarfa yanda kasan za su jijjigo daga jikin jijiyoyinsu.

Cikin wani irin gwamamman yare ta riski muryar inuwar tana cewa, "Sai kin halaka ke da abin da yake cikinki, kin zama halakakkiya keda tsiron da ke cikinki." Ba ta yi aune ba ta fara jin abu na bin ƙafarta zuu!  A daidai lokacin da ta ji wani irin nishi ya taso mata.

Durƙushewa ta yi a wurin tana murƙususu, nan take wani irin kukan Jarirai mai haɗe da kukan Jaki ya fara karaɗe lungu da saƙon da ke cikin dajin tamkar zai tsage gida biyu. Sannu a hankali Jarirai suka fara rarrafowa suna zageta kamar ana zagaye wainar gero. Duk da halin da take ciki bai hanata yunƙurin tashi domin tseratar da rayuwarta ba, amma ina! Haihuwa ta tunkarota gadan-gadan nan take jaririn ya faɗo.

Sannu a hankali ya rinƙa bin duk wurin da jini ya zuba yana lasa shi da sauran 'yan uwansa Jarirai, tamkar waɗanɗa suke da'irar ƙungiyar asiri.  Raihan da ke durƙushe da sauri ta zabura kamar wacce aka ɗanawa ruwan dalma, tana yunƙurin tashi nan take mabiyiya ta faɗo. Kamar yanda Kura take ƙishirwar nama haka suka afkawa Mabiyyar kafin wani lokaci tuni suka gama da ita.

Kamar haɗin baki haka suka waiwayi wurin da take tsaye, tamkar 'ya'yan Birrai haka suka fara tsalle suna ɗane jikinta har Allah ya basu nasarar hawa jikinta. Lokaci ɗaya suka fara lasar jikinta, ihu take kurmawa kamar zautacciya amma babu ɗaya daga cikinsu da ya yi alamun dakatawa. Daga can ƙafarta ta hango Jaririn da ya fito daga jikinta yana bin jinin ƙafarta yana lasa. A haukace ta ƙwalla ƙara tana ambatar sunan Mahaifiyarta kamar wacce ake zare wa rai.

Firgigit ta farka daga bacci tana sauke ajiyar zuciya kamar wacce ta ci gasar tseren gudu, jikinta rawa yake kamar mazari, ta haɗa gumi sharkaf kamar wacce take gaban maƙera.

"Barka da tashi ranki shi daɗe." Ba ta yi aune ba ta ji kalaman Mama Uwani a tsakiyar kanta. Da sauri ta ɗago ta kalle ta har lokacin jikinta rawa yake, sai da ta jingina da bangon gadon ta lumshe ido tana sauke ajiyar zuciya ta ce, "Yauwa Mama Uwani."

"Kina buƙatar wani abu?"

Girgiza mata kai ta yi tana murza idanu, hamma ta yi haɗe da miƙa sannan ta dubi Mama Uwani tana faɗin, "Mama Uwani ki haɗa min Tea kafin na fito." Cike da girmamawa Mama Uwani ya russuna tana faɗin, "An gama shalelen Uwani, gabanki gata bayanki gata. Duk abin da kika faɗa haka za a yi uwar ɗakina." Tana gama maganar ta fice daga ɗakin, Raihan miƙewa ta yi tana ɗan waƙe-waƙenta sannan ta faɗa toilet don ɗaura alwalar sallar asuba. Sai dai rana ta buɗe sosai wacce take nuni da gari ya waye tangararan don ƙarfe tara har da kwata a lokacin.

Sai dai har lokacin mafarkin da ta yi bai gama sakin jikinta, wani abin da ya bata mamaki bai

wuce zuwan period ɗin ta ba alhalin ba lokacin zuwansa ba ne.

Mama Uwani tana fita bayan Raihan ta shiga toilet wata baƙar mage ce ta ratso daga bangon kusurwar ɗakin, idanunta jawur suke kamar gauta ga ƙarshen jelarta wani tafkeken kan maciji ne ban da sheƙi babu abin da yake yi. Kalle-kalle ta fara yi tana shine-shine sannan ta fara girgiza cikin wani irin yanayi, lokaci ɗaya ta fara rikiɗa zuwa kaloli daban-daban. Sai da ta rikiɗa zuwa kaloli sama da goma sannan ta dawo kalarta ta farko, ta buga tsalle zuwa kan gadon da Raihan ta tashi wanda har ya ɗan fara ɓaci da jini. Tana hawa kai ta fara lasa sai da ta siɗe shi tas sannan ta sauko cikin takun ƙasaita tana kalle-kalle, a hankali ta taka zuwa kan mudubin Raihan da ke cike da kayan shafe-shafe da turarruka kala-kala.

Girgiza ta yi lokaci ɗaya ta rike zuwa wata mummunar hallita mai siffar dorinar ruwa da ranƙwalelen ƙaho a goshinta, a hankali ta fara zuƙe mayuka da tururrukan da ke cikin kwalabe da robobinsu, nan take komai ya zama wayam babu komai a ciki. Wani irin ruwa ta shiga ɗurawa mai yauƙi sai da ta gama cika su sannan ta hura iska suka dawo tamkar mayuka da turarrrukan da ke ciki da farko. Mama Uwani ce ta tunkaro ƙofar da sauri wannan hallitar ta sake rikiɗewa zuwa mage wannan karon jelar rabuwa ta yi gida biyu dukkansu ɗauke da kan maciji. Tana jin alamun buɗe ƙofa da sauri ta ratse ta jikin bango ta ɓace daga ɗakin, sai dai takaicinta ɗaya da bata samu ta ƙarasa cimma abin da yake tafe da ita ba.

Mama Uwani jere kayan abincin Raihan ta fara yi, a daidai lokacin Raihan ta fito ɗaure da towel. Da murmushi Mama Uwani ta riƙo hannunta tana faɗin, "Yar gatan Uwani me kike buƙata bayan wannan?" Ɗan yamutsa fuska ta yi ta ce, "Babu." Mama Uwani cikin wani yanayi ta fara bin ɗakin da kallo, Raihan ta ɗan ja guntun tsaki tana faɗin, "Mama Uwani ki bani wuri bana buƙatar hayaniya."

Mama Uwani ba don ta so ba ta juya jiki a sanyaye ta fice daga ɗakin tana waige, fitarta ke da wuya Mommy na kawo kai tana ganin Mama Uwani ta ce, "Uwani yarinyar ta tashi kuwa?" Mama Uwani cikin ladabi ta ce, "Ta tashi hajiya yanzu na kai mata abin kari." Mommy bata tanka mata ba ta tura ƙofar ɗakin ta shiga, Raihan na gaban mudubi za ta fara shafa mai. Mummy ta kira sunanta tana ci gaba da cewa, "Raihan ba dai yanzu kika ta shi kika yi sallaha ba?" Raihan ta ɓata fuska ta ce, "Haba Mommy wai me kika mayar da ni, ni ba sallah ma zan yi ba period ɗina ya dawo." Fuska ɗauke da damuwa Mommy ta ce, "Period kuma, ina ce yau ko sati biyu ba ki da gamawa ba." Cikin rashin damuwa ta gyaɗa kai tana ci gaba da shafa mai, juyawa Mommy ta yi ta fi ce tana faɗin, "Gaskiya idan ya ci gaba da yi miki wasa dole mu je mu ga likita." Raihan ta tura baki gaba ƙasa-ƙasa da murya tana faɗin, "Kawai don period ɗina ya dawo sai ace sai na je wani Hospital ana zaune ƙalau." Turo ƙofar da aka yi ne ya sa Raihan waigawa a lokacin ta fesa turare tana saka wata doguwar rigar bacci, Mama Uwani ce ta sake shiga hannu ɗauke da kunun gyaɗa ta ajiye, Raihan na ganin haka ta saki murmushi mai sauti ta ce, "Mama Uwani dama kin yi kunu shi ne baki kawo min ba, ai kuwa da na cika cikina sai kin kwashe min tass kin ɗura min kunun nan." Ta ƙarasa magana tana zame towel ɗin jikinta don ita Raihan bata kunyar ko a gaban waye ta cire kayanta ko ta sauya wasu.

Mama Uwani na ganin haka ta fice daga ɗakin, Raihan na cikin saka kaya ta ji kanta na sara mara lokaci ɗaya jini ya fara bin ƙafarta ga wani irin raɗaɗi da jikinta yake yi ta ko'ina, nan take ta yanke jiki ta faɗi a wurin. Wani irin hayaƙi ne ya fara zirarowa ta jikin ƙofa har sai da ya zo gaban Raihan da ke kwance jini ya fara malala daga jikinta, lokaci ɗaya  hayaƙin ya rikiɗa zuwa siffar mutum. Kallon kan mudubin Raihan ya yi yana girgiza kai cike da baƙin ciki, ɗaya bayan ɗaya ya fara zuƙewa mayuwan ciki da yake ganinsu da kalar ruwan nan mai yauƙi, kusurwa bangon ɗakin ya kalla ya ce, "Tabbas ba aikin kowa ba ne sai naki Mugaza, na lura kin fara wuce makaɗi da rawa amma ranki sai ya yi mummunan ɓaci." Tun bai rufe baki ba magen nan ta sake ɓullowa ta bango, har sai da ta zo gabansa ta yi girgiza cikin surar wata matashiyar budurwa ta ce, "Ka ga laifina don na nakasta mai shirin tarwatsa farincikina? Ko kana tsammanin zan zura ido ka ɗauko mini kishiya alhalin ka san wannan haramtacciyar al'ada ce a zuri'armu. Wani abin takaici ma ka rasa wacce za ka aura sai bil'adam salon ka ja mini abin kunya cikin ahalina, wallahi ba zan lamunci haka ba kuma wannan somin taɓu ne ka zuba ido ka gani." Tana gama maganar ta sake rikiɗa zuwa mage ta ɓace daga ɗakin, cike da takaici ya kalli gadon Raihan sai kawai ya fara kiran sunan Hidaya. Sai da ya kira sau uku sannan wata matashiyar budurwa ta ratso ta ƙarƙashin ƙasa mai zubin siffar Raihan babu abin da ya bambamta su har kayan jikinta. Wurin abincin Raihan ya nuna mata ya ce, "Ki maye gurbinta kuma bana buƙatar a samu matsala idan ba haka ba har abada ke da biyan buƙatar ƙudurinki."

Idanunta ne suka ciko da ƙwallah ta ce, "Wuskarbat min kalsusbima wakfit karmu linkasbu muzrabatu fisgatmuha warmi Jalkisu Mu'az." (Don Allah karka yi mini haka, ka san duk duniya babu wanda nake ƙauna kamar Yarima Mu'az.)

Ɗaukan Raihan ya yi da ke kwance ya saɓa a kafaɗa sannan ya kalli jabun Raihan da ke tsaye ya ce, "Dole ki ɗauki ɗabi'a irin ta Raihan hatta yare dole ki ci gaba da irin yarenta ba namu da muka saba yi ba. Na gaya miki idan aka samu matsala ke da Yarima Mu'az har abada." Yana gama maganar ya daki tsakar ɗakin nan take ƙasar wurin ta dare ya faɗa ciki hannunsa ɗauke da Raihan suna shigewa ƙasar wurin ta haɗe ta shafe kamar wani abu bai taɓa faruwa a wurin ba.

SHARE HILIS🌚

Daga yau za ki iya turo kuɗinki don karki bari ayi babu ke🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️

Ummou Aslam Bint Adam🌚
*ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

©  *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 3

Mommy na shigowa ta nufi wurin dianning sai da ta zauna sannan ta kalli wurin da Raihan take zaune ta ce, "Mama Uwani ta ce min kin yi breakfast ko?" Jabun Raihan da ke zaune a kan kujera ta ce, "Eh na yi ɗazu." Mommy na juyawa ta buɗe kular abinci sai ta ga wayam, sake buɗe ɗayar kular ita ma babu komai; haka ta riƙa buɗe kulolin abincin amma sai taunannun ƙashi a ɗan tsorace ta tashi tana faɗin, "Waye ya cinye abincin nan Mama Uwani?" Cikin rashin damuwa Raihan ta ce, "Yanzu na cinye su." A ɗan tsorace mommy ta ce, "Gabaɗaya abincin ke kika cinye har fa da abincin rana na ajiye mana." Raihan ta miƙe ta nufi ɗakinta tana faɗin, "Wanda Mama Uwani ta kaimin bai ishe ni ba shi ya sa." Mommy sororo ta yi jikinta a sanyaye tana bin bayan Raihan da kallo.

Jabun Raihan na shiga ɗaki ta ji Huzaifa na ƙwala mata kira, ta kusurwar bango ta wuce cike da ɗoki don zamanta a cikin gidan jin ta take kamar a kabari take.

Huzaifa da ke tsaye a gaban Raihan ya dubi Jabun Raihan ya ce, "Mugaza ta yi mata rauni zan mayar da ita ga mahaifanta amma zan ci gaba da bata kulawa kamar yadda na kwashe dubban shekaru ina tsaye a kanta. Ki je na sallame ki idan da yuwar wani lokacin na buƙace ki za ki ji ni." Cike da farinciki jabun Raihan ta rikiɗe  zuwa siffar wani ƙaton tsuntsu mai ɗauke da manyan fuka-fukai ta ɓace daga wurin, daga wurin da yake ya ɗauki Raihan ya ɗora ta akan gadonta sannan ya ɓace daga wurin.

Bayan shigar jabun Raihan ɗaki ta fara kiran Mama Uwani, cike da girmamawa ta ƙaraso wurin tana faɗin, "Ga ni hajiya."

Mommy ta kalli kulolin kan dianning ta ce, "Mama Uwani yau mun wayi gari da wani abin almara, dubi kulolin nan wai Raihan ta cinye." Da mamaki Mama Uwani ta zaro idanu ta ce, "Hajiya duka ita Uwarɗakin nawa ce ta cinye?" Mommy ta taɓe baki ta ce, "Dama ke ba ta laifi a wurinki ai, yanzu a sake dafa wani abincin bari na haɗa cornflakes." Mama Uwani ta fara tattara kwanukan tana faɗin, "Hajiy ai kowanne laifi kika ɗauko cewa kike ita ce, ni kuma uwarɗakina bata laifi." Tana gama maganar ta kwashe kwanukan ta wuce kitchen da su.

Raihan ba ita ta farka sai bayan azahar, a hankali ta buɗe idonta da suka yi mata nauyi dum! Tana ƙarewa ɗakin nata kallo. Lumshe idonta ta yi saboda yadda ta ji kanta yana sara mata kamar zai tarwatse, yunƙurawa ta yi zata tashi zaune ta ji jikinta ya yi mata wani irin tsami, ƙafarta ta hagu ta ji ta yi mata sanyi kamar ba a jikinta take ba. Da ƙyar ta samu ta fara dafa bango tana jan ƙafar tata da take jin ta yi mata nauyi kamar gungumen icce, tana zuwa falo ta fara yamutsa fuska tana bin ko'ina da kallo, a gefe ɗaya kuma ta fara wani shinshine-shinshine a haukace kamar mahaukaciya sabon kamu, da rarrafe ta fara watsi da kayan fallon cikin wani irin yanayi tana wani irin ƙaraji da gurnani kamar zakanyar da take tsaka da farauta. Karar

fashewar kayan ne ya fito da Mommy daga ɗaki a tsorace tana bin wurin da kallo, tana shirin yin magana su Goggo suma suka turo ƙofa suka fito don ganin abin da yake faruwa. Gilas ɗin center table da ta fasa ta fara ɗauka tana wurga musu tana faɗin, "Waye ya ɗauke min ɗana, ɗana ne wallahi duk wanda ya taɓa min shi sai na kashe shi." Inno da Goggo na ganin haka da rarrafe suka juya cikin ɗaki a tsorace, suna shiga suka bankawa ƙofarsu sakata jiki na rawa.

Mommy jiki na karkarwa ta ce, "Raihan lafiyarki kuwa?" Raihan ta sake wurgawa Mommy wata kwalba da sauri ta sa hannu ta kare, kwalbar ta yanketa a hannu jini ya fara zuba, jin ƙarnin jinin mommy ya sa ta fara wurga mata wani mugun kallo tana lasar baki. Ta ci gaba da surutai ba fasali, Mama uwani ta shigo a tsorace tana kallon abin da yake faruwa.

Hanyar kitchen ta nufa tana zuwa a haukace ta fisgo wata ƙatuwar roba wacce take ciki da ɗanyan kifi, tana zuwa falo ta rungumeta da hannuwa biyu tana sauke ajiyar zuciya.

Mommy na shiga ɗaki hankali a tashe ta ɗau waya ta fara kiran Daddy, ba a jima ba ya ɗauka ko jiran cewarsa bata yi ba ta fara faɗin, "Alhaji muna cikin tashin hankali, da alama ciwon Raihan na shekarun baya ne ya dawo sabo don Allah ka yi maza ka zo." Amsa mata ya yi sannan suka yi sallama ya katse wayar a gaggauce, Mommy na daga wurin da take a ɗaki tana jiyo ƙarara fashe-fashen kayan da Raihan take yi. Bayan wani lokaci shiru ne ya biyo baya, jin shirin ya sa Mommy ta miƙe a hankali ta buɗe ƙofar ɗakin. A falo ta hango Raihan zaune rungume da ɗanyun kifi, gabaɗaya ta ɓata jikinta da falon da ruwan kifi ban da ƙarninsa babu abin da yake tashi. Daddy ne ya turo ƙofa ya shigo yana gaba Dr Hamza na biye da shi, sai dai ganin yanayin falon ya sa ya fahimci wannan ciwon nata har ya ninka na baya. Jin sallamar Daddy ya sa ta ɗago da jajayen idanunta tana yi masa wani irin kallo, a haukace ta zaburo kansu tana faɗin, "Kar wanda ya taɓa mini ɗana jinina ne ba zan laminta a raba ni da shi ba." Tana rufe baki ta wurgowa Daddy wata kwalba saura kaɗan ta same shi a fuska ya kauce, Daddy ne ya fara kiran Yunusa mai gadi yana zuwa suka shiga kiciniyar riƙe Raihan sai da ƙyar suka samu nasarar riƙeta Likita ya yi mata allurar bacci, a take bacci ya ɗauketa ta faɗi gefe.

Kan kujera suka ɗorata Likitan ya fita yana yi wa Daddy bayani.

"Wato Alhaji da alama ciwon yarinyar nan ya dawo sabo, domin idan har abin da mahaifiyarta ta faɗa ne za mu iya cewa ya ninku a kan na da, saboda a da tana surutai kawai idan abin ya tashi, amma a wannan karon tana nuna kifi a matsayin ɗan cikinta. Akwai issue mai girma a game da lamarin ciwonta, za mu yi bincike mai zurfi a kai, sannan kar a rika wasa da magungunanta ta riƙa sha akai-akai." Jikin Daddy a sanyaye ya miƙawa Dr Hamza hannu yana faɗin, "Na gode sosai Dr don Allah a yi wani abu kai, ka san ina matuƙar son Raihan ba zan iya jure rashinta." Dr Hamza ya jinjina kai ya ce, "Insha Allah Alhaji kuma a ci gaba da addu'a everything will be successfully." Daga haka suka yi sallama da Likita. Yana komawa ciki tuni ma'aikatan gidan suka shiga hada-hadar gyaran falon, kusa da ita ya je ya zauna ya zura mata ido, hannu ya ɗora a kan goshinta zuciyarsa babu daɗi ya ce, "Wish you quick recovery dear, me ya sa al'amuranki basa zuwa da sauƙi why? Allah ya baki lafiya my baby." Mommy na

ƙarasowa wurin ta dubi Alhaji cikin damuwa ta ce, "Habibi ni kam wata shawara gare ni." Bai furta mata komai ba ya ɗago yana kallonta ya yi mata alamar yana sauraronta. Jingina ta yi da bango ta ce, "Gani nake yi mai zai hana ciwon yarinyar nan a haɗa shi da na islamic chemist ko akwai shafar aljanu a ciki..." Tun bata dire zancenta ya buga mata tsawa da cewar, "Ba na son na ƙara jin kin danganta min Raihan da wani jinsin bayan bil'adam, idan ba haka ba ranki zai yi mummunan ɓaci. Me ye wani islamic chemist malaman da kaje wurinsu sai dai su fara yi maka turare da hayaƙi, da sun samu wuri za su fara yi maka maula. Idan ba za ki taya ni mu nema mata magani ba don Allah ki cire hannunki daga cikin maganar, ni kaɗai na isa na nema mata lafiya." Ran mommy ba ƙaramin ɓaci ya yi ba, amma babu yadda ta iya haka ta ja bakinta ta tsuke don ta san akan wannan maganar sai su haura sama su faɗo.  Daddy ne ya ciccibi Raihan zai kaita ɗaki da sauri Mommy ta nuna masa ɗakinta tana faɗin, "Ka kaita Toilet ɗina zan gyara mata jikinta a can sai ta kwanta." Bai tanka mata ba ya wuce ya kaita ɗakin Mommy don har lokacin fushi yake yi.

Mommy da kanta ta gyara Raihan ta kwantar da ita a kan gadonta, zama ta yi a gefe tana kallon ƴartata cike da tausayawa. Idanunta ne suka ciko da ƙwalla, ta sharce ƙwallah ta furta, "Wannan ita ce kalar tamu ƙaddarar, Allah ya baki lafiya Raihan."

Raihan ta jima tana bacci sai bayan wani lokaci sannan ta tashi, ɗingisawa ta ci gaba da yi har ta fito zuwa falo. A lokacin an gyara falon sai ƙamshin turare yake. A zaune ta hango Mommy Mama Uwani na zaune a ƙasa tana matsawa Mommy ƙafa, cike da farinciki Mama Uwani ta ce, "Uwar ɗakina kin tashi?" Kafin Raihan ta yi magana Mommy ta furta, "Barka da tashi My Princess." A ɗingishe ta ƙaraso wurin cikin damuwa mommy ta ce, "Me ya samu ƙafar taki?" Raihan ta yamutsa fuska ta ce, "Wallahi haka kawai na ta yi min nauyi. Mommy kamar mun je wani wurin ko? Ko dai mafarki na yi ne?" Mommy a tunaninta lokacin da ciwon Raihan ya tashi take nufi, ita kuma Raihan tana son tuna zuwanta Duniyar su Huzaifa amma kanta ya yi nauyi ta manta. Mama Uwani ta kafeta da ido sannan ta ce, "Uwar ɗakina sannu kin ji, ai ke kin zama ƙadagaren bakin tulu a karki a kar tulu a barki ki ɓata ruwa." Raihan ta ce, "Yauwa Mama Uwani, don Allah haɗo min ruwan tea." Ta yi maganar cikin jin daɗin kanbababawar da Mama Uwani ta yi mata, Nan take Mama Uwani ta tashi ta nufi hanyar kitchen. A hankali Goggo ta turo ƙofa ta fito falo, don tun lokacin da ciwon Raihan ya tashi da suka shige ɗaki babu wacce ta fito a cikinsu, kallo ɗaya za ka yi wa Goggo ka tabbatar da tsoro ya mamaye zuciyarta amma sai ta dake ta fara yashe baki tana faɗin, "Rehanu hutawa ake yi." Raihan ta taɓe baki ta ce, "Ni kam ko karatu ne wallahi Goggo ya ci ki haddace sunana, kullin sai na ce miki ba sunana Rehanu ba amma ina miyar kuka ta toshe ko'ina." Mommy ta ɓata fuska ta ce, "Gidanku Raihan." Goggo da ta lura Raihan ta dawo cikin hayyacinta, ta yi mata daƙuwa ta ce, "Gata a zaune ita kika gayawa haka." Goggo ta nemi wuri ta zauna tana faɗin, "Abu kunna mini wannan shirin da suke na ƙasashen labarawa ko idanuna sa ƙara ƙarfi." Inno ta ƙaraso wurin tana faɗin, "Allah ya sani ba za mu kalli masu jajayen kunne ba, ni dai ki kai mini shirinsu wannan yaron Adamu zango da Ali Nuhu, ki saka mana sangaya mu kallah." Mama Uwani ce ta ƙaraso da kofin shayi ta taimakawa Raihan suka wuce ɗaki, don ƙafarta sosai ta yi mata nauyi ɗingisawa take yi.

Shigar su ɗaki keda wuya, Mama Hasiya ƙanwar Daddy ta yi sallama cikin falon. Fara'a ɗauke a

fuskarta ta shiga cikin falon. Mommy da murmushi ta tarbi Mama Hasiya tana faɗin, "Mai gidan da ba awo ba cefane, ba waya ba labari." Mama Hasiya ta zame mayafin jikinta tana faɗin, "Mutum da gidansa wacce waya zai yi." Mommy ta saki murmushi tana faɗin, "Barka da zuwa wai da yamman nan kike tafe." Mama Hasiya ta ajiye jakar hannunta tana faɗin, "Wallahi dole ce ta kawo ni, kin san Hubbi ya yi tafiya ƙafar Dubai to sun yi waya da DR John wai yau zai shigo gari so kin san matsalar hospital ɗin Dr John idan kana son ganinsa sai dare." Mommy ta sauya fuska cikin yanayin damuwa ta ce, "Allah ya sa a dace wai wancen karon ba ya ce ƙasa da six months komai zai iya faruwa ba? Ya ce za ki iya samu ciki a kowanne lokaci." Mama Hasiya ta jinjina kai ta ce, "To kin ga dai shiru, lamarin rashin haihuwar nan ba ƙaramin damuna yake yi ba. Tun hubbi bai fara damuwa ba yanzu na fuskanci abin ya fara damunsa, shekara sama da goma sha biyar ba haihuwa an ya ina da rabon ganin ƙwaina a duniya kuwa?" Mama Hasiya ta yi maganar idanunta na cikowa da ƙwallah. Cikin sigar lallashi Mommy ta dubi Mama Hasiya tana faɗin, "Komai kika ga ya faru da bawa da sanin Allah, ba a nan take ba. Komai fa lokaci ne mutane da dama akwai waɗanda suka fiki daɗewa kuma Allah ya kawo musu mafita, mu ci gaba da addu'a komai ya yi farko zai yi ƙarshe." Mama Uwani ta ƙaraso cikin falon fuskarta ɗauke da fara'a tana faɗin, "Hajiya barka da zuwa." Bayan sun gaisa ta fara kawo mata kayan ciye-ciye da shaye-shaye bata jima da barin wurin ba su Inno suka fito falo, nan take suka ci gaba da hira.

Mama Hasiya ƙanwar Daddy ce uwarsu ɗaya ubansu ɗaya, tana auren wani hamshaƙin ɗan kasuwa a unguwar Hotoro. Sun shafe shekara goma sha biyar da auren saurayi da budurwa, sai dai Allah bai basu haihuwa ba duk wannan tsahon shekarun, sun yi yawon ƙasashe amma duk ba a dace ba har sai da suka fara ganin wani likita Dr John, ta taɓa samun ciki ta yi ɓari har sau biyu daga haka ko ɓatan wata bata sake yi ba, don haka ta nace wa Dr John lokaci-lokaci take zuwa ganin likita.

DR JOHN SPECIAL HOSPITAL shi ne sunan asibitin da Mama Hasiya take zuwa ganin likita, asibitin a bayan gidan su Mommyn Raihan yake. Duk ranar da Mama Hasiya za ta zo ganin likita a gidan Daddy take kwana saboda asibitin sai goman dare Dr John yake fara ganin patient, wannan dalilin ya sa idan ta ga likita take dawowa gidan ɗan'uwanta ya kwana, yawaici tare suke zuwa da Mommy saboda mai gidanta yana tafiye-tafiye, kuma yawo babu inda ba su je ba don neman haihuwa.

Cikin Dare.

Wata irin guguwa mai ɗauke da amsa kuwwa marar daɗin sauraro ta fara karaɗe lungu da saƙon da ke cikin dodon kunnuwanta, a hankali iskar ta fara kaɗa labulayen ɗakinta. A hankali ta fara ratso bangawayen da gidan tana raɓewa ta jikin ƙananan shukokin da ke harabar gidan, ta jikin bangon ɗakinta ta ratso jikinta ɗauke da jajayen kaya masu ratsin baƙi haɗe da ɗishi-ɗishin busasshen jini a jikinta. Tana shiga ɗakin Raihan ta tsaya cak a bangon gudu, ta fara huro mata iska nan take Raihan ta miƙe zaune hannuwanta toshe a kunnuwanta ta dubi Intisar. Cikin wata irin girgiza ta ƙaraso wurin Raihan ta kama hannuwanta tana shirin yin magana Raihan ta ce, "Intisar me kika zo yi yanzu gidanmu?" Intisar bata bi ta kanta ba ta hura

mata iska a fuska nan take ta fara layi tana shirin faɗuwa, da sauri Intisar ta tarota tana dafe kafaɗarta ta ce, "Za ki bi ni?" Babu musu Raihan ta gyaɗa mata kai, Intisar bata bi ta kanta ba ta riƙe hannunta nan take suka ɓace daga ɗakin.

Gudu suke zabgawa cikin sararin samaniya a can wani ƙasurgumin dajin wani makeken gida suka sauka, Raihan ban da ido babu abin da take bin ƙawarta Intisar da shi. A wani katafarn kogon dutse suka dira mai ɗauke da wasu irin mutane masu mummunar hallita, ɗauke suke da jajayan sitiru sai zanen jini a jikkunansu. Wata mummunar hallita ce a tsugunne mai ɗauke da kan barewa da manyan ƙahunhuna ga wani irin jini da yake ɗiga daga bakinta a cikin wani ƙaton faifai. Zuwansu ke da wuya wani tiƙeƙe da ya kasance babbansu ya dubi Intisar ya ce, "Hatsabibiya Bungulu na maraba da baƙuwa mai daraja." Intisar da dubi Raihan ta ce, "Ki yi gaisuwa ga Habibiya Bungulu ta saka miki albarka." Kamar bawa da uban gidansa haka Raihan ta dubi wannan hallitar ta duƙa kamar yadda ta ga suna yi ta miƙa gaisuwa. Da wani ƙaton sirinji wani ɗan tsamurmuri ya zuƙi jinin da wannan hallitar take ɗigarwa daga bakinta, a shammace ya samu damtsen hannun Raihan ya kafa mata har sai da ya juye jinin jikin sirinjin a jikinta, sannan ya zuƙo nata ya fesa a jikin hallitar. Lokaci ɗaya ta fara rawar ɗari kamar mai jin sanyi, tun tana daga tsaye har ta duƙushe a wurin tana karkarwa.  Tana jima tana abu ɗaya sannan ta tsagaita da rawar ɗarin, a zabure ta miƙe tsaye cikin wani irin ƙarfi ta zurawa mummunar hallitar tana jiran umarninta.

Buɗe bakinsa ya yi nan take wasu baƙaƙen macizai suka fara fitowa daga bakinsa, suna faɗowa suke fasa kai suna zagaye Raihan. Cikin wani irin yanayi hallitar ta miƙe tsaye tana girgiza sannan ta fara magana da wani irin yare har sai da ta yi yare ya fi kala goma, sannan ta yi magana da harshen hausa.

"Tabbas mun yi babban kamun da muka jima muna jiran wannan rana. Domin ƙara tabbatar da abin da muke zargi godiya za ta kawo mana jini mafi muhimmanci wanda zan shayar da mai gidana domin samun lafiyarsa." Tun bai rufe baki ba Raihan ta russuna tana faɗin, "An gama Hatsabibiya Bungulu." Mummunar hallitar ta nunawa Raihan wata ƙatuwar ƙwarya mai cike da tafasasshen jini ta ce, "Babu buƙatar haka domin da alama ke shugaba ce, muna buƙatar jinin wannan matar yanzun nan..." Raihan ta amsa mata tun bata ƙarasa maganar ba da cewar, "Jininta ya halarta a gare ki, duk duniya babu jinin da za ki buƙata ya gagara a wurina." Tana rufe baki Hatsabibuya Bungulu ta miƙa mata wani busasshen ƙashi da alama ƙashin jikin bil'adam ne. Raihan na karɓa ta wuce cikin sararin samaniyar iskar sihiri bata tsaya ko'ina ba sai a katafaran cikin gidan Mahaifinta, sai da ta zaga ɗakunan gidan sannan ta dira a ƙofar ɗakin mahaifiyarta.

🤭🤭🤭 WASAN YANZU YA FARA, MAZA HANZARTA KI BIYA NA KI DON JIN WACECE AINIHIN ZAUJATU JINNUL-ASHIQ ƊIN, SHIN A CIKIN SU WACECE ƳAR GABAN GOSHIN ALJANIN SOYAYYAR? SHIN WACECE WANNAN INTISAR ƊIN KUMA WACECE HATSABIBIYA BUNGULU? 😁 AMSOSHIN NA GABA DON JIN ƘULALLEN ƊAURIN DA KE CIKIN LABARIN.

Share Fisabillah🌚
[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

© *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 4

Raihan na fita Intisar ta ƙarasa gaban Hatsabibiya Bungulu rai a matuƙar ɓace ta ce, "Hatsabibiya uwar hatsabibai, sai kai mai siffar dabba a bayan fage ki koma bil'adama. Babu hallitar da ta gagare ki rikiɗa duk girmanta duk ƙanƙantarta, yaya ina tunanin lokacin share mini hawayena ya zo amma na ga wankin hula yana shirin kaini dare. Na kawo Raihan domin a salwantar mini da rayuwarta amma da alama tana shirin samun fada a wurin nan, yake Hatsabibiya tun farko kin san ba haka muka yi da ke ba."

Hatsabibiya Bungulu ta yi girgiza lokaci ɗaya ta rikiɗa zuwa wata kyakkyawar budurwar, zaune take tsirara sai wasu sassan gaɓɓoɓin jikinta da ke rufe. Wani malalacin murmushi ta saki sannan ta dubi Intisar ta ce, "Da mun san kina da wannan yarinyar da tuni mun jima da umartarki ki kawo mana ita, sai dai kash! Silar saninta na daga gare domin biyan buƙatarki. Kin kawota domin mu kashe ta sai dai ba za ta mutu ba." Da hannuwa biyu Intisar ta sa ta toshe dodon kunnenta saboda yadda ta ji kalmar a kunnenta, a duniya idan da wacce ta tsana to Raihan ce. Lokaci ɗaya ta murtuke fuska tana shirin yin magana Hatsabibiya ta ci gaba da magana.

"Na tabbata baki san wacece Raihan ba, da kin san amfanin da za ta yi mana a cikin ƙungiya da bakinki bai furta kalmar kisa a tattare da ita ba. Shin ko kinsan Muraza?" Da sauri Intisar ta ɗago da kai tana kallon Hatsabibiya tana girgiza kai bakinta na rawa ta ce, "Ina zan santa ya ke Hatsabibiya mu da muke nemanta ido rufe." Matashiyar budurwar da ake kira da Hatsabibiya ta yi girgiza nan take ta rikiɗe zuwa surar wani ƙaton tsuntsu, sai da ya yi tsalle-tsallensa sannan ya koma kan kujerarsa ya zauna ya ci gaba da magana cikin siffar tsuntsu.

"Tabbas Raihan ita ce Muraza, tun shigowarta kogon dutsen nan alaminta da babban matsafi ya sanar da mu suka bayyana. Ƙofar nasarorinmu ta buɗe ƙarfin iko, tsafi da sihiri da ƙarfin ƙungiyar asirinmu za ta sake dawowa da ƙarfin ikonta, domin haske ya bayyana inuwarta ɗauke take tartsakin wuta mai halakar da magautanmu, za mu riƙe hannu bibbiyu domin saminta tamkar samun lu'ulu ne a ƙarƙashin teku, idan muka yi sake ta kubce mana tabbas mun tafka babbar asara." Intisar ta faɗaɗa murmushinta sai da ta yi taku biyu sannan ta waiwayo ta ce,

"Haƙiƙa zan jinkirta buƙatata har tsawon wani lokaci bayan mun cimma matsayarmu, amma tabbas ko ba yanzu ba akwai ranar da Ya za ta ɗakin ƙanwa, lokaci na tafe zan aiwatar da abin da yake ci mini tuwo a ƙwarya. Ni ma lokaci ya dawo mini da zan karɓo sihirtacciyar sandar mahaifiyata Bokanya Shirzan, a lokacin ne duk wani cikar ikona zai dawo." Tana rufe baki suka fara ƙyaƙyata wata irin dariya mara daɗin sauraron mai ɗauke da amsa kuwwar kukan jakuna, suna tsaka da kuka sai ga wani matashin saurayi ya diro cikin ɗakin hannunsa ɗauke wani jariri sabuwar haihuwa. Jaririn sai mutsu-mutsu yake ko jikinsa ba a gyara ba balle a yanke cibiyarsa, a kan tafin hannun wani gunkin tsoho da ke tsaye ya wara hannuwansa. Yana ɗora jaririn a kai nan take wannan Hatsabibiya da ke ɗauke da siffar tsuntsu ta taso ta dira a kan cikin jaririn. Wata ƙara ya ƙwalla saboda wata irin azaba da ke ratsa sassan jikinsa, da ƙafafuwansa tsuntsun ya huda ƙirjin jaririn ya kafa kai yana tsotsar jinin jaririn. Kafin wani lokaci tuni idanun jaririn sun ƙafe jikinsa ya saki numfashinsa ya ɗauke, tana ganin haka ta tashi daga kanta sai Intisar ta ƙarasa ta banƙare ƙirjinsa ta ciro zuciyarsa ta wurga bakinta ta cinye.

Ɗaukan gawar jaririn ta yi ta miƙawa sauran mutanen wurin, da sauri suka caɓe shi suka buɗe wani ƙaramin ɗaki mai ja da baƙin labule suka wurga ciki.

Raihan na zuwa gida a hankali ta fara zaga bangon da ke cikin ɗakunansu, ga mamakinta tana bi ta cikin ɗakinta ta hangi mai siffarta kwance a kan makwancinta a gefe ɗaya ga Mama Uwani tana zaune tana gadinta. Amma ga mamakinta sai gani ta yi ta gifta ta gabanta ba tare da ta lura da ita ba. Hasalima ratsawa take yi ta ko'ina ba tare da gini ko ƙofa sun yi mata shamaki ba, a hankali ta ci gaba da tafiya kamar mai tafiya a sararin samaniya har ta dira a ɗakin Mahaifiyarta sai da ta ƙare mata kallo sannan ta wuce ɗakin da Mama Hasiya take kwance tana bacci. Kamar yadda Hatsabibiya ta umarceta haka ta tsaya a saitin kanta, ƙashin hannunta ta kai saitin fuskar Mama Hasiya lokaci ɗaya ta buɗe idonta firgigit ta sauke su a kan Raihan, sai dai a cikin idanunta gani ta yi Raihan ta siffanta da wata mummunar hallita, cikin rashin tausayi Raihan ta ƙarasa gabanta ta damƙo maƙogaronta, nan take Mama Hasiya ta fara kakari idanunta suka firfito waje.

Da murya mai wahalarwa Mama Hasiya ta fara karanta kalmar shahada, tana yi tana ambaton sunan Maigidanta da duk sunan wanda ya zo bakinta.

Ana cikin haka wasu tafka-tafkan kunamu suka fara ratsowa ta jikin bango girman kowacce ɗaya ya fi girman kan jariri, da gudu suka fara rarrafowa suka haye gadon sun kai kusan goma suka maƙale a jikin Mama Hatsiya kowacce ta kafa bakinta suka fara zuƙar jini.

Cikin tsananin azaba Mama Hasiya ta fara wani irin ƙaraji da gurnani, tun tana cikin hayyacinta har ta fara fita daga haka idanunta suka kafe rai ya yi halinsa. Raihan na ganin haka ta saki wuyan gawar Mama Hasiya ta faɗa kan gado yaraf ta ja mayafi ta rufeta sannan ta miƙawa kunamin nan hannu lokaci ɗaya suka maƙaleta, ta ɗago da su saitin fuskarta. Haƙoranta ne suka fara girma ga wata fiƙa irin ta karnuka da ta fito mata, bakinta ya fara zubda wani baƙin jini mai yauƙi. Ƙwayar idanunta zazzago suna wani irin juyi, a hankali ta fara takawa ta fice daga ɗakin ta koma ta sashen ɗakin Mahaifiyarta, ta jima a bakin window sai da ta yi

ƙwafa sannan ta ratsa ta jikin bango ta fice daga gidan.

Bayan sun wurga Jaririn cikin wannan ɗakin wata irin tsawa aka yi mai haɗe da walƙiya, a hankali hatsabibiya ta shiga ɗakin tuni wata mummunar hallita mai ɗauke da kawuna har guda goma a jikinta, a kowanne baki akwai aikin da yake aiwatarwa. A ɗaya daga cikin kan mummunar hallitar ta cafke jaririn tana laƙumewa, wani kan kuma ya fara amayo da kuɗaɗe kala-kala har da na ƙasashen waje, ya yin da wani kan ya fara tatsar da wani ruwa mai yauƙi yana zuba watsu ƙananan ƙwari suna zuwa suna tsotsa.

Suna nan tsaya Raihan ta diro cikin gidan, hannuwanta biyu saƙale da kunamu tana tafe cikin takun ƙasaita dauke mummunar hallita. Tana zuwa Hatsabibiya ta fito fuskarta ɗauke da murmushi, shigar Raihan wurin ya sa jikin wannan dattijon ya fara ɓamɓarowa daskararran jikinsa ya fara rozayewa a hankali har ya rozaye gabaɗaya. Wata irin girgiza ya yi nan take ya fara kallon mutanen wurin ɗaya bayan ɗaya, Hatsabibiya ta tako a hankali fuskarta ɗauke da annuri ta ce, "Barka da dawowa cikin rayuwarka ta ainihini Ya masoyina." Hannuwanta ya riƙo yana bin ta da kallo lokaci ɗaya ya rungume ta yana shafa bayanta sannan ya ce, "Ina godiya da sadaukarwarki, amma ya aka yi kika samu tsarkakken jini alhalin an ce sai ta silar Muraza shin kun samota ne?" Hannunsa ta ja bakin wata tsohuwar rijiya da ke cikin ɗakin tana faɗin, "Mu je turaka zan baka labari." Tana rufe baki suka faɗa cikin rijiyar shigewarsu keda wuya wurin ya shafe tamkar ba a taɓa hallitar wani abu a wurin ba.

Wani tutturnan mutum da suke kira da Mataimaki shi ya ƙarasa wurin Raihan ya karɓi kunamin hannunta, ya zuba su a cikin wani ƙoƙon kai sannan ya dubi Raihan ya ce, "An gaishe ki Jaruma, Shugaba mai cikakken iko sai ke gagabadau. Za ki iya tafiya sai ranar taro na gaba amma a ranar muna buƙatar tukwicin sabuwar gawar mace mai ƙarancin shekaru kar su yi ƙasa da talati kar kuma ta haura shekara arba'in." Raihan ban da jinjina kai babu abin da take yi, tana gama sauraronsa ta dubi Intisar alamar su tafi. Intisar ta nuna mata wata ƙoriyar ƙwarya mai cike da wani ruwa mai ɗauke da launin jini kamar anwanke nama, sannan ta ce: "Ki kuskure bakinki da ruwan tsarki domin samun albarka." Ba musu Raihan ta ƙarasa ta ɗauki ƙwaryar ta kafa kanta, tana kafa kai ta ji kanta ya sake yin nauyi dumm! A hankali ta iya kai ƙwaryar bakinta ta kuskure wata irin kasala ta mamaye jikinta, ga wani irin addababban bacci da ya lulluɓe idanunta. Tana ajiye ƙwaryar ta tafi luuuu za ta faɗi da sauri Intisar ta taro ta jikinta, sannan ta saɓa ta a kafaɗa ta fice daga cikin kogon dutsen kai tsaye ta wuce gidan su Raihan.

Intisar bata tsaya a ko'ina ba sai a tsakiyar ɗakin Raihan, tana kallon Mama Uwani ta saki wani malalacin murmushi. Kwantar da Raihan ta yi sannan ta fara zagaye ɗakin ba tare da idanun Mama Uwani sun gane mata Intisar ba, lokaci ɗaya ta saki wata mahaukaciyar dariya. Tun tana dariya a tsaye har ta durƙushe a wurin sannan ta ratse ta ƙarƙashin ƙasa ta fice daga ɗakin.

WASHEGARI

Da Asuba bayan su Inno sun gabatar da sallah suna zaune kowacce a sallayarta suna jan

carbi, Goggo ta dubi Inno ta ce: "Wai ni kuwa yarinyar ta tashi sallah kuwa don ko motsinta ban ji ba, saboda Allah neman haihuwa ya fi bautar Ubaniji. Jiya na ga saboda neman haihuwa raba dare suka yi a wurin wancen Kafiriin, gaskiya a tambayi Malamai an ya; ya hallata neman haihuwa wurin kafiri." Inno takaici ya fara rufeta, ta dubi Goggo ta ce, "Zinaru ki yi ta kanki idan kika kafirta min yarinya a yau ba sai gobe wallahi sai Audullahi ya mayar da ke Albasu. Kafira ce da har yanzu za ta zauna babu sallah babu salati?" Goggo cikin nuna rashin damuwa ta wara hannuwa tana faɗin, "Allah shi ne masanin daidai, ba zan amsa ba ki sa na yi wa ƴar mutane ƙazafi akan abin da ban ji ba ban gani ba, ni dai na san da Hasiya ta tashi za ta leƙo wurinmu. Bari ki ga na je na tashe ta ko na samu lada mai tsoka, bar zancen Albasu tun da ko jini baki taɓa zubarwa a cen balle a binne mabiyyarki." Goggo na ƙarasa maganar ta fice daga ɗakin, tana tafe tana mita har ta ƙarasa bakin ƙofa tana ƙoƙarin buɗe ƙofar sai ga Inno ta rufo mata baya ta ƙaraso wurin tana faɗin, "Saboda Allah Zinaru in haifi abartawa a ciki amma ki nemi ki yi mana farraƙu da ita, Allah ya sani idan Hasiya ta ga ban tashe ba na ɓalɓalce don ɗauka za ta yi baƙin cikin shiga aljanna nake yi mata." Goggo bata bi ta kan Inno ba ta tura ƙofar tana rangaɗa sallama, kamar haɗin baki suka shiga ambatar sunan Hasiya amma shiru suka ji kamar an shuka dusa. Inno ce ta yaye zanin rufar jikinta nan take suka yi tozali da gawarta, kusan suman tsaye suka yi aka rasa mai furta koda kalma ɗaya ne. Nan take Inno ta yanke jiki ta faɗi, Goggo jiki na tsuma ta juye hanyar waje tana ƙwalawa Mommy kira. Can sashenta ta wuce saboda fargaba tini ta zubar da carbi don lokaci ɗaya ya tsinke ya tarwatse, da kusan rarrafe Goggo ta hau sama tun bata ƙarasa ba suka ci karo da Mommy shi kansa Daddy kiran Goggo ne ya sa shi fitowa daga ɗakinsa a lokacin yana zaune yana cike-ciken takardu.Hankali a tashe suka shiga jera mata tambayoyi ban da nuna musu ƙofa babu abin da take yi, sai da ƙyar suka samu ta iya furta, "Hasiya babu ta riga mu gidan gaskiya." Cikin rashin fahimta suka ce, "Wace Hasiya?" Saboda ko a kaɗan basu kawo Hasiya a ransu ba. Goggo cike da jin haushi ta ce, "Hasiya dai ƙanwarka Audullahi ko kana da wata Hasiyan ne." Kusan tare suka nufi hanyar sauka don zuwa su ganowa idanunsu.

Kamar masu rige-rige haka suka shiga ɗakin da Hasiya ke yashe a kan gado, Daddy ne ya fara zuwa kan Inno Mommy ta ƙarasa wurin gawar Hasiya ta fara tattaɓata tana ambatar sunanta amma shiru tafiya ta miƙa. Da hanzari Mommy ta wuce firji ta ɗebo ruwa ta fara yayyafawa Inno sannan ta yayyafawa Hasiya, nan take Inno ta fara motsawa saidai da alama bata cikin hayyacinta amma Hasiya ko alamar motsi bata yi. Daddy ne ya rungumo Inno ya fita a guje yana ƙalawa maigadi waya, kusan gware suka yi a hanya Daddy ya nufi wurin motoci yana faɗin, "Maza-maza buɗe min gate." Tun bai rufe baki ba Driver ya fara kiciniyar buɗe ƙofa nan take bawa motarsa wuta ya fice daga gidan, Mommy jiki a sanyaye ta bi bayan motar da kallo fuska ɗauke da hawaye. Ɗakin ta koma ta janyo hannun Goggo ta rufe ɗakin, kan kujera ta zauna ta rafka tagumi ban da hawaye babu abin da take yi, saboda ba ƙaramin shaƙuwa suka yi da Hasiya ba. Goggo ban da sintiri babu abin da take yi tana nan tsaye suka ga Mama Uwani ta fita, cikin rashin sani ta fara tambaya, Goggo da sai a lokacin kuka ya kubce mata cikin shassheka ta ce, "Bari Uwani yau mun wayi gari da tashin hankali Hasiya babu, yarinyar nan jiya-jiya muka gama hira da ita amma yau sai labari." A tsorace Mama Uwani ta nufi ɗakin don ganewa idonta, tana shiga ta samu gawar a kan gado cikin hanzari ta buɗe ta tana ƙarewa gawar kallo.

Ido ta zurawa gawar tana jinjina kai a hankali ya furta, "Tabbas akwai lauje ciki naɗi amma akwai ɓoyayyan al'amari a dangane da gawar nan." Tana gama maganar ta fice daga ɗakin zuwa falo, ba a ɗauki lokaci ba sai ga Daddy ya dawo. Dawowarsa babu wuya mommy ta tashi Raihan ta sanar da ita halin da ake ciki, murtsuke ido ta yi tana yamutsa fuska ta ce, "Mommy waye ya mutu?" Mommy ta sake maimaita mata, "Mamanki Hasiya yanzu haka gawarta na ɗaki mutane sun fara taruwa." Lokaci ɗaya ta ji kanta ya yi mata nauyi dum! Har sai da ta runtse idonta ta buɗe ta dafa kanta da hannu biyu ta ce, "Mommy me ya sameta ta mutu?" Da sauri Mommy ta rufe mata baki tana faɗin, "Raihan wa yace miki sai an yi ciwo ake yin mutuwa?" Jikin Raihan ba ƙaramin mutuwa ya yi ba, a hanakali ta tashi tana haɗa hanya jikinta sanye da rigar bacci shara-shara babu abin da ta ɓoye na surarta. Ɗakin da Mama Hasiya take ta tunkara Mama Uwani na hangota da sauri ta nufi wurinta ta rungomata tsam a jikinta tana faɗin, "Uwar ɗakina sai haƙuri." Wani iri Raihan ta ji a jikinta yarr a lokaci ɗaya kanta ya yi mata yaaaam! Tsigar jikinta ce ta ci gaba da tashi, a hankali ta saki hannunta tana bin Raihan da wani mayatattacen kallo.

Kafin wani lokaci tuni gidan ya cika da mutane ban da koke-koke babu abin da ake yi, Raihan can gefe ta raɓe ta fashe da wani irin matsanancin kuka. Mai gidanta da aka gaya masa da farko ƙaryatawa ya yi sai da ya zo ya ganta, zama ya yi kamar mace ya yi ta kuka sai da ƙyar ya yi shiru. Kimanin ƙarfe goma aka gama wanke gawarta aka shiryata, ana gabda za a fita da ita sai ga Intisar ta turo ƙofa ta shiga gidan tana kallon mutanen gidan ɗaiɗai tana shigowa ana ɗaukan gawar, tana kalle-kalle Mama Uwani ta fisgi hannun Intisar ta ja ta ɗakin baya wanda baƙi suke sauka a ciki. Rai a matuƙar ɓace ta dubi Intisar ta ce, "Me ya kawo ki gidan nan?" Intisar dariya ta yi ta fara takawa a hankali sai da ta yi taku uku sannan ta juya ta kalli Mama Uwani ta ce, "Abin da ka ke yi cikin suffar tsofaffi shi ne ya kawo ni a wannan suffar."

[7/1, 6:00 PM] My Data sim number: *DUBU JIKAR MAI CARBI*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

*Littafin kuɗi ne 200 idan kina buƙata za ki biya ta wannan Account ɗin Aisha Adam 3090957579 First bank ko katin Mtn, ki turo da shedar biya ta wannan lambar 07062062624.*

https://chat.whatsapp.com/KQd6gkViAXfKDTv7iWLJpV

FREE PAGE 1

Babban gida ne mai ɗauke da ɓangare daban-daban har kusan sashen mutum goma sha

biyu. A taƙaice za mu iya cewa gidan gandu ne da ya haɗa Kakanni, 'ya'yaye da jikoki. Garin Ɗangwauro yana ɗaya daga cikin ƙanana ƙauyukan da ke cikin ƙwaryar Kano, Allah ya azurta su da noma, kiwo da kasuwansu. Gidan Malam Muhammadu mai dogon Carbi sanannan gida ne a kaf cikin garin Ɗangwauro. Tun daga titi idan ka tambaya za a kai ka har cikin gidan, sakamakon gida ne gidan yawa don wani lokaci mutane na yi masa laƙabi da gidan 'Ya'ya da yawa.

Gidan Mai dogon Carbi cike yake da mutane sakamakom wayar gari da suka yi da rasuwar rashin wannan Dattijo mai yawan shekaru, ba iya gidan ba hatta garin Ɗangwauro ya girgiza da rashin wannan Dattijon mai dogon zamani. Yaya Babba da Inna Furai sune matan wannan Dattijo da ya rasu mutuwar ba ƙarmin taɓa su ta yi ba.

Bisa ga al'adar Malam bahaushe a ranar da aka yi mutuwa mutane sun fi nuna damuwarsu ta hanyar koke-koke, kukan ma yana taƙaita yawancin bayan ankai mammaci. Hakan ce ta faru a gidan Mai dogon carbi domin an fita da gawarsa a yi mata sallah yara da Manya sai kuka suke yi.

A gefe ɗaya Hali dubu na hango rakuɓe sai muzurai take lokaci-lokaci tana share hawaye, sai dai cikin zuciyarta haushin mutanen gidan take ji saboda ta lura babu wanda yake bi ta kanta don ya rarrasheta, duk kuwa da irin gursheƙen kukan da take yi. Kallonsu ta fara yi tana ayyana irin abin da za ta yi domin ta janyo hankulansu kanta. Tun da ai ita gani take kamar ta fi su jin mutuwar koda suna yawan faɗa da Mai dogon carbi amma kafin ya rasu,  ai ita ma Kakanta ne.

Sumi sumi sumi ta tashi da yaƙunannan hijabinta ta bi hanyar soron gidan tana waiwaye, sai da ta je soron ƙarshe daga shi sai fita Hali dubu ta ɗora hannuwa biyu akanta ta dawo cikin gidan da gudu tana cewa, "Wayyo Allah! Wayyo ni na shiga uku na lalace." Lokaci ɗaya hankulan mutanen gidan ya dawo kanta, da sauri aka yi carko-carko a kanta masu jero tambaya na yi. Zuciyarta ƙal don ko ba komai ita ma za a rarrasheta kamar yanda aka saka su Yaya Babba ana basu haƙuri. A fakaice take satar kallonsu tana sake sharce hawaye amma ta yi biris babu wanda ta tankawa duk irin tambayoyin da mutane suke yi mata. Baba Munkaila ne ya shigo ya hango cincirindon mutane a tsaitsaye da sauri ya ƙarasa wurin, ganin Hali dubu a zaune ya sa ya ja guntun tsaki sannan ya buga mata tsawa, "Ke lafiya kike yi wa mutane ihu?" Kamar sabuwar Marainiya haka ta ɗago shanyayyin idanuwanta ta kalle shi sai kuma ta waiga ta saci kallon ƙofa ta kuma duƙunƙune  kanta cikin alamun tsoro da firgici. Kamar haɗin baki dukansu suka kalli bakin ƙofar suna neman ƙarin bayani, babu abin da ta furta musu sai ma kuka da take yi tana nuna musu ƙofar da ɗan yatsanta. Baba Munkaila tsawa ya sake buga mata ya ce, "Me ye a cen ɗin?" Hali dubu ta kuma kallon ƙofar ta rushe da kuka tana cewa, "Baffa ne!" Cikin haɗin baki duka suka ce, "Baffa kuma? Wane Baffan?"

Bata bi ta kansu ba sai kawai ta baje a wurin ta fara wata irin birgima tana cewa, "Wayyo Baffa ne ya tafi ya barni!" Takaici ne ya rufe Baba Munkaila domin ya san za a rina don ya tabbata ganin Dubulliya tana wannan kukan ba banza ba. Cikin faɗa-faɗa ya fara yi mata magana amma ko gezau ba ta motsa ba. Can gefe ya hango wata igiyar dabbobi ai kuwa bai yi

wata-wata ba ya fara tafka mata, tana jin shigar bulala ta tashi ta yi cikin gida ta gudu.

Can ɗakin Yaya Babba ta shiga ta haye ƙarshen gado tana kuka, ga haushin Baba Munkaila ya tsinkata a cikin mutane. Tambayar duniya Yaya Babba ta yi amma Dubuliyya kanzil! Bata ce da ita ba. Sai ma ta yi zamanta a nan domin duk duniya babu abin da tafi tsana kamar taron jama'a a gidansu. Domin ba ƙaramin takura take yi ba, dalilinta na haka kuwa ta yanda za ta ji mutane na bata ji ko kuma ta cika rashin ji kamar ƴar aljanu. Tana daga kwance dabara ta faɗo mata ta yanda za ta kore jama'ar gidan ta ruwan sanyi domin ta san yanda danginsu suke sai a kusa arba'in da mutuwar da sauran baƙi tsiraru. Saboda haka Baffa mai dogon Carbi ya saba musu tun yana raye, idan suka zo taro baya barin ƴan uwansa su koma a kwana kusa. Wannan dabara tata ba ƙaramin daɗinta ta ji ba don har sai da ta murmusa saboda farin ciki. Kamar wacce aka tsirawa allura haka ta zabura da sauri ta fice daga ɗakin Yaya Babba, ita kanta Yaya Babba ba ƙaramin daɗi ta ji ba kasancewar duk duniya babu Jikarta da take so kamar ita sakamakon Marainiya ce gaba da baya.

Dubu tana fita ta yi garau da ita kamar ba ita ta sharɓi kuka ba, nan fa mutane suka fara yi mata tsiya, har da masu cewa dama ita zuma ce sai da wuta. Wasu kuma su ce gara da ya yi mata haka ga shi ta ware ta fara harkokinta. Shiru ta yi babu wacce ta tankawa sai dai duk wacce ta yi magana tana auna maganar tata a mizani domin ta san irin hukuncin da za ta yi mata.

Tun da Magriba ta doso Dubulliya ta fara haɗa kayan aikinta a fakaice cikin hikima da basira, ba tare da wani ya fahimci halin da take ciki ba. Sakamakon babban gida ne kowa da wurin da yake nema ya kwanta saboda ko ina a wadace yake hakan ne ya sa Yaya Babba bata damu ba da Hali dubu ta ce za ta sashen Baba Munkaila ta kwana a cen.

DA DADDARE

Da daddare gidan ya yi tsit ban da kukan tsintsaye da ƙananan dabbobi babu abin da yake tashi, sai munsharin bacci da yake tashi daga ɗakunan daban-daban. Dubuliyya tana daga sashen Baba Rufa'i cikin ɗaya daga cikin ɗakunan ƴaƴan gidan. Sai da ta ci baccinta ta more sannan ta farka cikin talatainin dare ta ji gidan tsit kowa ya yi bacci sannan ta saci jiki ta zaro kayan marigayi Baffa ta saka rigarsa da babbar riga har da hula ta naɗa rawaninsa ta ɗauki zabgegen carbinsa ta maƙala ta fito, hasken farin wata ne ya haska mata hanyar da za ta rinƙa bi har fice daga sashen gabaɗaya. Can wurin da ya zamewa Marigayi Baffa mai carbi wurin alwala can ta je ta tsugunna, daga nesa idan ka hango Dubu a tsugunne sai ka rantse da Allah Baffa ne, sai da ta waiga hagu da dama sannan ta taƙarƙare ta fara zabgo kaki irin yanda Baffa yake yi, Baba Sule da ke kwance cikin baccinsa ya fara jin alamar kaki tamkar yanda mahaifinsu yake yi duk asuba. Fakare ya yi yana zare idanu, yana cikin wannan yanayin ya sake jin an yi kaki har da irin tarin tsofaffin nan da Baffa yake yi. Janyo wayarsa ya yi yana dubawa ya ga ƙarfe biyun dare, nan take ya hau murza idanu yana sake kasa kunne. Dubu kamar ta san ana sauraronta ta kausashe murya sai ka rantse da Allah Baffa ne yake magana ta fara cewa, "Tabbas rayuwar barzahu daɗi gare ta." Baba Sule ya waro idanu wace cikinsa na

karta masa, don ya tabbata hatta dabbobin gidan da suna magana za su ce sun shaida maganar Baffa ce cikin daren nan.

Dubu na tsugunne ta ji alamun tahowa wata zuciyar ta ce mata ta tashi ta ɓuya, wata kuma ta ce ta zauna ta ci gaba da abin da take yi. Tarin Inna Furai ta ji ta saci kallonta ta hangota da ƴar buta a riƙe za ta je banɗaki. Dubu wani kakin ta sake yi tana daga tsugunne, hasken farin wata ne ya hasko mata mutum durƙushe da fararen kaya da rawani tamkar marigayin mijinsu. Gabanta ne ya yi mummunan faɗuwa ta fara motsa baki cikin addu'a don a zatonta mugun gamo ta yi.

Ɗauke kai ta yi don ma kar ta ci gaba da kallon wurin da Dubu take ta ci gaba da tsoratata, sai da ta kusa da wurin da Dubu take ta ji muryar marigayin mijinsu raɗau a kunnenta yana cewa, "Wato ita dai rayuwar barzahu daɗi gare ta. Babban daɗin idan ka kawo ziyara tsohuwar rayuwarka sai kuma ka tafi da matarka." Inna Furai na jin haka ta dafe ƙirji tana ja da baya jikinta har tsuma yake ta ce, "Yau na haɗu da zazzagar rayuwa ni Furaira. Allah na roƙeka karka jarrabe ni ta wannan fannin." Dubu na jin haka ta miƙe tsaye tana gyara zaman babbar rigar jikinta ta sake kausashe murya ta ce, "Wuni ɗaya har na yi abokai miliyan ɗaya da ɗari biyar a cikin Fatalen har da masu tashi sama. Ƴan sama jannati ku zo ga wani naman mun samu, kuma daga yau mun fara ɗauka kenan a gidan nan. Duk wanda ya wayi gari ya ga likkafani a jikin kayansa shi za mu yi wa ɗaukan amarya." Inna Furai tuni fitsarin da take riƙewa ya samu sukunin tsiyayowa, sakin butar hannunta ta yi jikinta na tsuma donma bongon da ke bayanta ya tokareta.

Dariya ce ta so ƙwacewa Dubu amma ta maze ta ce, "Ƴan uwana ƴan sama Jannati! Ku zo na fara samo muku ƴar uwa." Inna Furai ta saki salati tana cewa, "Yau na haɗu da zazzagar rayuwa shi kenan tawa ta zo ƙarshe." Dubu sunkuyar da kai ƙasa ta yi ta fara takowa gaban Inna Fuarai ta ce, "Idan kina son fansar kanki sai kin sake shayar da ƴaƴanki tamkar yanda kika shayar da su suna jarirai, tun daga kan Larai (Ita ce babbar Ƴar Inna Furai) har zuwa kan Sabi'u (Shi ne autanta) idan kika kuskurewa haka tabbaci haƙiƙa sai mun zo ido biyu mun tafi da ke babu wanda ya isa ya hana."

Baba Sule tuni cikinsa ya ɗuri ruwa yana son fita domin ceton Matar Mahaifinsa tsoro ya cika masa ciki, bai gama tsinkewa da lamarin ba da ya ji an fara kiran yan sama jannati. Dubu don ta ƙara razana Inna Furai ta sake dakushe murya ta ce, "Ki isarwa da mutanen gidan nan saƙona muddin suka ci gaba da kwanaki sai na yi musu ɗauki ɗaiɗai. Shi kuma na ɗaki da yake laɓe yana sauraronmu, shi kuma ɗauke shi za mu yi gabaɗaya." Dubu na cikin magana sai gani ta yi Inna Furai ta zube ƙasa. Gabanta ne ya faɗi ta ji fargabar kar tsohuwar mutane ta mutu a hannunta. Da sauri dubu ta waiga sai kuma ta kurma ihu tana maƙe murya ta zunduma ihu, sannan ta zuba a guje ta yi cikin gida. Ta nufi ma'ajiyar kayan Baffa ta lallaɓa ta shige ta kwanta.

Ihun da Dubu ta yi ba ƙaramin razana Baba Sule ya yi ba da jim kalaman da da aka ce za a ɗauke shi matuƙar ya saki hannun matarsa. Yana daga gefen gado da sauri ya matsa ya kama

hannuwan matarsa ya riƙe ƙam, don kar a neme shi a rasa. Cikin bacci Sahura ta fara masifa da yake Allah ya yi ta masifaffiyar macece. Tana jin ya riƙo mata hannu ta ce, "Don Allah sakarni Uban ƴan naniƙa." Da yake bacci ya hau kanta bata kuma tanka masa komai ba.

Daga ɗaki mai kallon gabas Baba Auwalu ne ya ɗaga labule yana haskowa da fitila zaraf matarsa Yahanasu ta miƙe tana tambayarsa da yake su sabbabun amare ne. Daga can nesa suka hango Inna a yashe tana ko numfashi bata yi. Gabansa ne ya faɗi yace, "Wa nake gani kamar Inna a ƙasa." Sahura ta dafa kafaɗarsa ta ce, "Auwaluna ni ban yarda ita bace kawai magauta ne suka yi maka ture."

Duk duniya babu abin da Auwalu ya tsana sama da a ɓata ran Yahanasu amma tabbas wannan karon ba zai iya haƙura ya bar Mahaifiyarsa a wannan yanayin ba. Kasancewar dare ne amma bai hana sakar mata murmushi ba ya ce, "Allah shi zai kare ni amma bana tunanin wani zai yi mini ture cikin dare." Kafin ta yi magana tuni Auwalu ya yi gaba, ganin haka ya sa ta ja tinga ta tsaya don har ga Allah a tsorace take musamman da ya kasance ranar ne aka yi rasuwa.

Hankali a tashe ya fara yayyafawa Inna ruwa ganin ta fara motsi ya sa ya kamata yana bubbuga ƙofar Baba Sule, Baba Sule na ji ya yi fakare kamar mai bacci don gabaɗaya ya gama rikicewa. Sama-sama Sahura ta fara jin bugun ƙofa firgigit ta miƙe sai ji ta yi Sule ya riƙe hannunta gam, tana shirin yin magana Baba Sule ya janyota cikin raɗa ya fara cewa, "Kada ki yi magana za su yi sama da ke" Waigawa Sahura ta yi tana kallon ƙofa don ita a tunaninta masu buga ƙofar ne za su yi sama da ita. Suka ƙarajin bugun ƙofa Auwalu yana cewa, "Yaya Sule fito ka taimaka mini jikin Inna ya yi tsanani ina jin makewayi za ta ta faɗi." Sahura ta ja guntun tsaki ta ce,

"To! Sai ka tashi tun da ta ka ji muryar Auwalu." Baba sule ya sake ƙasa da murya yanda daga shi sai Sahura ne za su ji abin da yake faɗa ya ce, "Ki koma ki kwanta kawai ina ji a jikina waɗannan ƴan sama jannati ne suka rikiɗa. Takaici ya kama Sahura yanda ta ga Maigidanta yana rawar ɗari ga shi ba lokacin zafi ba, ta miƙe tana fusgar hannu ta ce, "Sakarni ko ƴan ƙasa jannati ne babu abin da zai hanani fita."Tana jan hannu Baba sule yana ja don a tunaninsa muddin ta saki hannunsa shi kenan za su yi sama da shi.

Sororo Sahura ta yi tana kallon ikon Allah, don ita a iya saninta da Sule ba su taɓa irin wannan wasan da shi, don haka ta sake ɓata fusaka ta ce, "Sule wai wani abu ne yake damunka ko gamo ka yi cikin dare n sani ba?" Baba Sule ya yi wura-wura yana kallon hagu da dama ya sake ƙanƙance murya ya ce, "Sahura a kowanne lokaci za a iya yin sama da ni." Wani takaicin ne ya sake rufe ta, ta miƙe tana ƙoƙarin fisge hanunta amma abin ya ci tura don ƙarfin mace dana namiji ba ɗaya.

Auwalu da ke jin ƙusur-ƙusur a ɗaki sai ya sungumi Inna don a ganinsa bai kamata ya sake buga ƙofar ɗakin ma'aurata cikin dare ba. Can sashen su Inna Furai ya nufa Yahanasu ta ƙwalla masa kira tana cewa, "Auwaluna ina za ka ni dai tsoro nake ji." Auwalu ya waigo ya ce, "Shiga

ɗaki Inna zan kai na dawo."

Dubu na daga ɗaki tana jin duk abin da yake faruwa, tana jin Baba Auwalu ya tafi ta yi zaraf ta fito cikin sanɗa sai da ta zo daga bakin ƙofar Yahanasu ta yi gyaran murya ta sake kausashe murya irin ta Marigayi mai carbi ta ce, "Wato ita rayuwar barzahu daɗi gare ta ni Mamman. Yanzu tun da na zagayo rayuwata ta baya dole na ɗauki mai ɗakin nan." Cikin Yahanasu ne ya kaɗa nan take jikinta ya hau karkarawa kamar mazari. Dubu ta yi irin tarin tsofaffin ta sake cewa, "Amma ita Yahanasu za mu ɗaga mata ƙafa sai dole ta bi sharaɗinmu ko ba haka ba ƴan sama jannati?" Dubu ta sake sauya murya ta ce, "Ai dole ma ta bi umarninmu ko yanzu mu faɗa ɗakin." Yahanasu bata san lokacin da ta yi farat ta ce, "Wallahi ku faɗa ko meye zan bi."

Dubu ta maƙale murya ta ce, "Dole ki zama makauniyar ƙarfi da ya ji muddin kika buɗe idonki sai dai ki wayi gari a ƙiyama." Tun Dubu bata rufe baki ba Yahanasu ta runtse ido biyu ta ce, "Wallahi na rufe har abada ba zan sake buɗe su ba amma don Allah karku cutar da ni."

Dubu har da ƴar tsawarta ta ce, "Kin tabbata kin rufe ko na aiko da Ƴan sama jannati su shigo?" Yahanasu ta sake runtse idonta tana cewa, "Na rufe wallahi na rufe." Dubu ta saki murmushin mugunta a ƙasan zuciyarta tana cewa, "Yau zan ga ƙaryar soyayya kullin a ishe mu da Auwaluna." A fili Dubu ta ce mata, "Maza tashi tsaye ki rungume bango." Da sauri Yahanasu ta fara lalaube-lalube har ta taɓo bango.

A hankali Dubu ta zura kai ta leƙa ta hango Yahanasu na rungumar bango, zuruf ta faɗa ɗakin cikin sanɗa. Sai da ta je daidai wurin Yahanasu sannan ta ɗaga zabgegen Carbin Marigayi ta zabgawa Yahanasu a ƙeya, sai ta fara wani gunji tana cewa, "Gargaɗin yan sama jannati kenan." Tana faɗar haka har ta fice daga cikin ɗakin.

Yahanasu tun da ta gantsare take hawaye a tsaye sai dai ta kasa buɗe idonta saboda tsoron abin da kaje ya zo.

Duk abin da yake faruwa a kunnen Sahura da Baba Sule, cikin Baba sule ne ya sake ɗurar ruwa. Sahura ita kanta jikinta ya fara sanyi musamman da ta jiyo Ihun Yahanasu, shiru ta yi kamar ruwa ya cinye ta duk masifar da take yi ta daina. Domin da alama zancen Sule ya tabbata.

Lokacin da Auwalu ya ƙarasa ɗakin Inna Furai, har lokacin bata dawo hayyacinta ba. Yana shiga ya kwantar da ita akan ƙaramin gado, sannan ya fara tashin ƙanwar Mahaifinsu Lantan da ta zo daga garin Zariya. Ganin halin da Inna Furai take ciki ba ƙaramin ɗaga hankulan mutanen ɗakin ya yi ba. Auwalu ya juya zai fita Inna Furai ta riƙo hannunsa ta ce, "Auwalu! Yau na haɗu da zazzagar rayuwa. Don haka ka haɗo mini kawunan ƴan uwanka mazan su da matan su a yanzun nan. Idan ba haka ba wallahi sai na zazzagar da albarkasu kowa ya lalace."

Auwalu da sauran mutanen ɗakin sun yi tsammanin zafin ciwo ne ya sa Inna Furai take sumbatu. Lantan ta ƙara matsawa kusa da Inna Furai ta ce, "Furaira sanu kin ji Allah sa dai ba

akan makarai kika faɗi ba." Wannan magana ba ƙaramin fusata Inna Furai ta yi ba, a zafafe ta ɗago ta ce, "A kan bulikiya na faɗi! Lantan bana son zazzagar wulaƙanci. Kai Auwalu ka tara mini ƴan uwanka a daren wallahi tun ban zazzage albarkar da ke kanka ba." Kamar sabon munafiki haka Auwalu ya fice sum sum sum daga ɗakin. Haka ya rinƙa bi ɗaya bayan ɗaya yana taso su. Wannan tashin da Auwalu yake yi wa ƴan uwansa ne ya sa kusan rabin mutanen gidan suka tashi daɗin daɗawa idan kowa ya ji ance Inna Furai ta faɗi a hanyar banɗaki sai ya wartsake masu tafiya ɗakinta na yi masu jaje suma suna yi.

Kafin wani lokaci tuni ɗakin Inna Furai ya cika da ƴaƴanta su rai takwas maza biyar mata uku. Sai da ta kalle su ɗaya bayan ɗaya sai kawai suka ga ta ɗaga riga ta ce, "Larai bisimillah" Larai zuciyar ta ɗaya ta ɗauka Inna Furai so take a ƙarasa cire mata riga, nan take ta fara cikiniyar tuɓe mata riga. Cikin ƙaraji Inna Furai ta fisge tana cewa, "Larai yanzu bijirewa umarnina za ki yi? Ni za ki zazzagewa albarka a ka" Sai ji suka yi Inna Furai ta fashe da matsanancin kuka. Lokaci ɗaya suka kalli juna domin ba su ga abin da zai sa Inna Furai kuka ba. Auwalu ya sunkuyo ya ce, "Inna ki yi hakuri me kike so?"

Inna Furai ta ɗago mamanta ɗaya ta ce, "Mahaifinku ya zazzage mini albarka ɗazu nan domin daga zuwansa lahira har ya haɗa kai da ƴan sama jannati. Ba zan zazzage maka bayani gabaɗaya ba amma Auwalu ungo sha ka ji."
[7/1, 6:02 PM] My Data sim number: *DUBU JIKAR MAI CARBI*

©AMEERA ADAM

FIRST CLASS WRITER'S ASSO...

*Littafin kuɗi ne 200 idan kina buƙata za ki biya ta wannan Account ɗin Aisha Adam 3090957579 First bank ko katin Mtn, ki turo da shedar biya ta wannan lambar 07062062624.*

https://chat.whatsapp.com/KQd6gkViAXfKDTv7iWLJpV

FREE PAGE 2

Auwalu sam bai fahimci inda maganar Inna Furai ta dosa ba, don tun da ya ji ta ambaci Mahaifinsu ya tabbatar da zafin ciwo ne yake damunta da kiɗimewar rashin da aka yi musu. Saboda gudun faɗanta ya sa ya wayance da cewa, "Inna ban fahimci abin da kike faɗa ba. Amma kuma duk wanda ya mutu kin san sai dai mu bishi da addu'a ita ce mafita." Inna ta yi ƙuri tana kallonsa sai zuwan can kawai ta fashe da kuka. Lantan da ke gefe takaici da baƙin ciki gabaɗaya suka turniƙe ta, don gani take kamar har da biyu Inna Furai take lanjarewa. Kasa haƙuri ta yi ta ce: "Furaira don Allah ki shafa mana lafiya ki bar mu, mu ji da abin da yake damunmu. Haka kawai ki tayar mana da balli a tsakiyar dare akanki aka fara mutuwar miji? Ko kuma ke kaɗai kika san zafin miji muna zaune ki ishe mu da zancen fatalwa. Ki barni na kwanta na yi baccin da ban samu na yi shi jiya ba."

Inna Furai ta fyace majina da gefen zaninta ta waiga ta ce, "Wallahi babu ƙatuwar Matar da za ta zo mini ɗaki ta nemi kawo mini zazzagar albarka ido biyu. Idan ba za ki iya ba ki tashi ki fice dama ni bana gayyar tsintsinya da bulugari, bare kuma mafici abin banza." Lantan jin maganar Inna Furai ta yi kamar ta watsa mata ruwan zafi, don haka ta zaburo a hasaale ta ce, "Ban da ƙaddara da rashin ɗan'uwana da na yi, me zai kawo ni ɗakinki kaico Allah ya jiƙanka Yaya Mamman. Wai yau jininka ake wulaƙantawa saboda ƙasa ta rufe mata ido, kai jama'a ɗan'adam butulu. Wanne irin karamci ne Ɗan'uwana bai yi miki ba?"

Inna Furai ta jingina da ƙarfen gado sai kawai ta fashe da matsanancin kuka, tana yi tana fatar majina. Abin duniya goma da ashirin ne damu su Auwalu, don haka kowa ya yi jim! Babu wanda ya iya tofa magana ɗaya sai gani suka yi Inna Furai ta fara haɗa ƴan kayayyakinta na sawa da ke kan gado. Sabi'u ya ce: "Inna lafiya kuwa wai me yake faruwa ne kike haɗa kaya?"

Inna Furai ta juyo a fusace ta ce, "Zaman ku a nan bai amfane ni da komai ba. Kuna gani ta gama zazzage mini rashin mutumci a ka babu wanda ya tanka mata. Wallahi ko ku bi mini haƙƙin zazzagar albarkar da ta yi mini a ka ko kuma yanzu na fice na baku wuri ku yi yanda kuke so. Gara ni tawagar Malam da ƴan sama jannati ta zo ta ɗauke ni ko kowa ya huta, dama na kiraku ne domin mu kashe mu binne amma da alama ku dai ba ƴan goyo ba ne, don na lura za ku iya zazzage mini sauran albarka da ta rage mini a kaina.

Gabaɗaya shiru suka yi suna nazarin abin da yake damun Mahaifiyarsu, don rikici sun san Mahaifiyarsu mace ce mai matuƙar rikici amma wannan karon gani suke har da mutuwar mahaifinsu da ta taɓa ta.

Lantan na gama sauraron Inna Furai ta miƙe tsaye tana shartar ƙwalla, ɗan ƙullin kayanta da ke ƙarƙarashin gado ta janyo ta fara kiciniyar ɗorawa a ka tana matsalar hawaye. Da sauri Auwalu ya miƙe ya riƙe kayan yana cewa, "Inna Lantana don Allah ina za ki a tsohon daren nan?" Lantan ta kunto mayafinta ta yafa a kanta ta ce, "Auwalu don Allah karka kawo mini maganar da za ta tunzurani har ta kai ga na nemi shaƙe wannan tsohuwar har lahira. Duk irin cin mutumcin da ta yi mini a gabanku baku gani ba za ka taso tsalo-tsalo kana tambayata ka bar ni yau ko ƙasa da sama za ta haɗe ba zan kwana a gidan nan ba."

Nan fa hayaniya ta fara ta shi a cikin gidan, Inna Furai na gama saurarar maganar Lantan ta sa hannu bibbiyu ta dafe ƙirji a razane tana zare idanu kamar wacce ta yi tozali da kumurcin maciji. Bata tanka musu komai ba sai gani suka yi ta sauko ƙasa daidai wurin da Lantan take tsaye ta fashe da kuka haɗe ta rungumo ƙafafuwan Lantan tsam a jikinta. Tana cikin kuka ta ɗaga kai ta dubi Lantan tana cewa, "Wallahi ba za ki bar ɗaƙin nan ba sai kin zazzage ragowar numfashin da nake shaƙa, Lantan yau ni kike muradin kashewa a gaban ƴaƴana. Ai kuwa ko ba yanzu na mutu ba na rataya a wuyanki Kai Auwalu ku shaida haka."

Inna Furai ta juya ga su Auwalu tana musu mugun kallo ta ce, "Allah na tuba wacce uwar na haɗa da su bayan alaƙar haihuwa? Da su Auwalu da Sabi'u kuma ni kam gara ma a ce ban da

kowa tun da babu mai tare mini faɗa a gidan nan. Har ana niyyar halakani da sauran rayuwa kai jama'a Lantan an ya kina tsoron Allah kuwa? Duk wanda ya kashe wani dai wuta za shi."

Lantan ta yi tsalle can gefe abin ka da da marar jiki, can gefen babban gado ta matsa tana cewa, "Laƙadi ja'akum... Tuf! Aniyarki ta faɗa kanki karki ja mini masifa ki maƙala mini sharrin kisan kai ina zaune ƙalau." A wannan karon Inna Furai bata tanka mata ba sai gani suka yi zaraf ta fice daga ɗakin, da sauri iyalanta suka bi bayanta suna roƙon ta dawo ɗaki saboda dare.

Tana fita ita ma Lantan ta sa ƙafa ta fito ganin haka ba ƙaramin ɗaga hankalin su Auwalu ya yi ba, musamman shi da yana tsaye a nan ne amma zuciyarsa na wurin Yahanasu yana tunanin halin da take ciki. Inna Furai na ganin Lantan ta fito ta bita jiki a sanyaye kamar kazar da ake jefa da gishiri ta ruƙo hannunta sannan ta fashe da kuka. Ita ma Lantan zuciyarta ce ta karye sai kawai ta fashe da kuka, sai da suka yi mai isarsu sannan Inna Furai ta ce, "Yanzu Lantan da na barki tafiya za ki yi a daren nan?" Lantan ta fyace majina a haɓar zaninta ta ce, "Ina zan iya tafiya na barki Furai kina cikin jimamin rashin miji, Furaira rashin miji tashin hankali ne har kin tuno mini da rasuwar Mahaifinsu Ɗan'iya kai rayuwa babu tabbas Allah ya jiƙanka Malam Mudassiru." Lantan ta rushe da matsanancin kuka. Rabe ya matso da niyyar rarrashinsu Inna Furai ta doke hannunsa tana cewa, "Allah wadaran naka ya lalace. Wallahi kaf gidan nan banga wanda zai hanani zazzage muku albarka ba. Wai kamar yanda Lantan take a wurina ta tashi za ta tafi cikin dare amma babu mutum ɗaya da zai hanata tafiya kaico! Wallahi kun ji jiki ƴan bakinciki bantaɓa sanin bakwa ƙaunar aminiyata ba kuma ƙanwar Mahaifinku ba sai yau."Inna Furai na gama maganar ta ja hannun Lantan suka bar su Auwalu a tsaye sake da baki.

Ba su da zaɓi haka suma suka bi su Inna Furai ciki, cikin ƙaguwa Auwalu ya ce, "Inna za mu iya tafiya yanzu?"

Inna Furai ta saki salati ta na kallon Auwalu da wani yanayi har sai da ya tsargu ya ɗan fara sosa ƙeya sannan Inna Furai ta ce, "Wallahi kai dai Auwalu na riga da na san matsayina a wurinka. Tun mahaifinka na raye har ya mutu ban taɓa musa wa maganarsa ba, sai yau don ƙasa ta rufe masa ido?" Ta fashe da kuka tana ci-gaba da cewa, "Ban shirya mutuwa da shiga jahanna ba. Sharaɗi fatalwar mahaifinku ta bani sai na shayar da ku mama kamar yanda na shayar da ku kuna yara, kuma ban ga wanda zai hanani bin umarninsa ba."

Lokaci ɗaya suka ɗauki salati gabaɗaya saboda ta'ajibin jin maganar Mahaifiyarsu, Larai cikin matsananciyar damuwa ta ce, "Inna kin san me kike faɗa kuwa? Yanzu kina nufin Baba ne ya yi miki fatalwa? Inna don Allah kar wani abu ya ruɗe ki ko ya tsorata ki saboda wanda ya mutu ya mutu kenan ba zai ƙara dawowa ba. Sai dai idan shaiɗan ne yake son razanar..."

A hassale Inna Furai ta katse Larai da cewar, "A'uzubillahi minasshaɗanirrajim. Ba zan ga shaiɗan da idona ba Larai kafirta ni kike son yi da za ki haɗa ni da Shaiɗan la'anannan Allah?" Larai rasa hanyar da za ta ɓullowa Mahaifiyarta ta yi don gabaɗaya sun rasa gane kanta. Lantan da ke gefe ta kalli Larai ta ce, "Wallahi ki tubar wa Allah idan ba haka ba, azabar Allah tuni za ta yi fata-fata da ke. Kuma ni gani nake maganar Furaira tana kan hanya don ni kaina

lokacin da Malam Mudassiru ya rasu har gizo ya riƙa yi mini a tsakar ɗaki. Don haka ku yi biyayya idan ba haka ba duk cikinku babu mai kaucewa azabar Ubangiji, musamman kai Rabe da ka fi tsoka wallahi tuni wuta za ta tsotse namanka ka lalace a jahannama."

Ganin wannan lamarin yana ƙoƙarin zama babba ya sa Auwalu ya zame jikinsa ya je Shagon Soro ya taso Yayan mahaifinsu ya sanar da shi halin da ake ciki. Har ɗakin Inna Furai ya shiga yana shiga ya same ta, ta yashe riga a sama tana kumfar bakin Larai ta tsugunna ta fara karɓa tun da sauran mazan taurin kai za su nuna mata. Da sauri ya ɗauke kansa gefe don bai yi tsammanin abin da suka faɗa da gaske ba ne. Nan take ya shiga yi mata nasiha amma duk da haka Inna Furai ta shafawa idonta toka ganin haka ya sa ya fara lallashin ta bari zuwa safiya sai a san abin yi. Da ƙyar da suɗin goshi aka samu shawo kan Inna Furai ta haƙura zuwa safiya sannan kowa ya kama gabansa. Bayan tafiyarsu Lantan ta zabga uban tagumi sannan ta ce, "Yanzu Furaira da idanunki biyu kika yi tozali da Yaya Mamman ni fa ɗazu ƙarya na kirfo da na ce ina ganin Fatalwar Mudassiru, saboda yaran nan sai su raina mu ni kuma a duniya babu abin da na ƙi jini irin raini."

Inna Furai ta miƙawa Lantan hannu ta ce, "Lantan taɓa ni na ji." Da sauri Lantan ta kai hannu tana shafa hannunta. Inna Furai ta mirtsika ido ta ce, "Billahilazi idan har wannan taɓawar da kika yi mini mafarki ce to a mafarki na ga Malam. Wallahi da idanuna na ganshi a wurin zaman alwalarsa amma tun da baku yadda ba nan gaba na kuma ganinsa nasa ya fitowa kowa a zahiri." Kamar wacce aka tsamo daga ruwan sanyi haka jikin Lantan ya yi sanyi ta rasa abin faɗa don hantar cikinta ta fara kaɗawa musamman da ta san Inna Furai ba ta yin rantsuwa sai da ƙwaƙƙwaran dalili. Kwanciya suka yi sai dai kowa da abin da yake wassafawa a cikin zuciyarsa.

Duk cikin ƴaƴan Inna Furai babu wanda ya fi farinciki da tafiyarsu irin Auwalu saboda zuciyarsa gabaɗaya hankalinsa yana wurin Yahanasu don ya san a wannan lokacin tuni ta yi fushi sai ya yi aikin rarrashi. Yana tafe yana haska fitila har ya ƙarasa ɗakin, sai dai turus ya yi a ɗan tsorace yana karewa ɗakin da Yahanasu kallo. Fitsarin da ya ƙarasa gangarawa ƙafarsa ne ya dawo da shi daga duniyar tunani, matsawa ya yi gefe yana leƙa fuskar Yahanasu da ke manne da bango ya ce,

"Yahanasu lafiya kuwa?" Yahanasu na jin muryar Auwalu ta rushe da kuka tana cewa, "Auwalu fatalwar Baba na gani wallahi shi ne har cewa ya yi za su tafi da ni." Cikinsa ne ya bada wani sautin ƙulululu! Da sauri ya ja baya yana dafe ƙirji ya ce, "Kina nufin da gaske kema kin ga fatalwar Baba?" Yahanasu ta nuna masa gadon bayanta ta ce, "Duba ka ga shatin carbinsa a bayana har dukana ya yi da shi kuma ya ce daga yau kar sake buɗe idona." Tsoro ne ya mamaye zuciyar Auwalu musamman da idanunsa suka yi tozali da shatin carbin Mahaifinsu ruɗu-ruɗu a jikinta. Hankalinsa bai ƙara tashi ba sai da ya hango wani guntun likkani a gefen ƙafar Yahanasu. Da sauri ya fisgota suka faɗa gado jikinsa na rawa ya ce, "Yahanasu wallahi maganarki haka take kin ga Likkafani can a ƙasa." Yahansu na jin haka ta ƙara rintse ido tana kuka kamar hawayenta za su ƙare. Auwalu ne ya yi ta maza ta miƙe cikin sanɗa ya banko musu ƙofa da ƙarfi ya sa sakata.

Duk abin da yake faruwa a kunnen Baba Sule da Sahura har zancen Likkafani, wannan maganar ba ƙaramin ɗaga musu hankali ta sake yi ba. Don da har bacci ya fara yunƙurin awon gaba da su kukan da Yahanasu ta rushe da shi ne ya wartsakar da su tare da sa su yin carko-carko kamar masu shirin ko ta kwana.

Dubu tun da ta koma ta yi luf sakamakon motsinta ya so tashin Hasiya Matar Rabe, don haka ta yi kasaƙe daga haka ba a jima ba bacci ya yi gaba da ita don hatta sallar Asuba sai da aka yi da gaske sannan Dubulliya ta samu gabatar da ita.

Washegari.

Jama'ar gidan gabaɗaya kowa ya tashi an ci gaba da harkoki kamar ba taron mutuwa ba. Sai dai gabaɗaya labari ya watsu a ko'ina Inna Furai ta yi ido huɗu da fatalwar Maigaidansu, labarin da wasu suka riƙa ganin kamar tsufa da rikici ne yayin da wasu suke ganin tsabar dukan da mutuwar ta yi mata ne. Sai dai babban abin da ya ja hankulan mutane ganin ɗakin Baba Sule da Auwalu ya rufe. Ko motsinsu babu wanda ya ji bare a sa ran za a ga fitowarsu.

Ɗakin Baba Sule aka fara zuwa ana bugawa, Sahura ta zabura za ta miƙe saboda ta ji muryar mutane don ta yanda ta ayyanawa zuciyarta muddin ta samu ta fice daga ɗakin to ba za ta ƙara kwana a gidan ba sai gidan Mahaifinta. Sai dai tana miƙewa caraf Baba Sule ya damƙi hanunta yana cewa, "Ina za ki tafi ki bar ni?" Sahura ta ƙirƙiro murmushin yaƙe ta ce, "Ai mutanen gida sun tashi ka ga muma sai mu fita zaman ɗaki ba zai kai mu ba." Baba Sule ya yi fakare yana nazari sannan ya ce mata, "Sahura yau ko bayan gida za ki shiga wallahi sai dai mu tafi tare, don ba zan bari matattu su tafi da ni da kwana na a gaba ba." Bugun ƙofar ne ya tsananta don haka suka taso riƙe da hannun juna suka zare sakata, sai dai suna buɗe ƙofa kyallen likafanin da Dubu ta soka musu ya faɗo. Daga waɗanda suke tsaye a ƙofar ɗakin har su na cikin ɗakin bazama suka yi a guje, suka yi cikin gida. A cen ɗakin Yaya Babba suka yada zango sai dai har lokacin Baba Sule yana riƙe da hannun Sahura. Yaya babba sakin baki ta yi tana kallon Baba Sule da ya yi tsamo-tsamo a cikin mata ta ce, "Sule me kake yi a kan cinyar Uwani?" (Uwani ƙanwar Mahaifiyar Sahura ce.) Baba Sule gabaɗaya zuciyarsa a dagule take saboda gani yake rayuwarsa  ta zo ƙarshe.

Ba baka sai kunne. Baba sule ban da hawaye babu abin da yake yi. Wannan shirun da Baba Sule ya yi ba ƙaramin ɓata ran Yaya Babba ya yi ba, don haka ta dube shi ta ce, "Bana son iya shege kai Sule idan ba za ka yi magana ba, ka fice mini daga ɗaki ko na kwashe maka albarkar da ta yi saura a kanka." Baba Sule ya sake matsar ƙwalla ya ce, "Inna wallahi Fatalwar Baba ce za ta tafi da ni matukar na saki hannun Sahuwa ƴan sama jannati ne za su tafi da ni."  Ku san mutuwar zaune Yaya Babba ta yi saboda labari ya risketa daga wurin kishiyarta ga shi Ɗan cikinta ma ya sanar da ita.

Nan fa gida ya hautsine hantar cikin kowa ta kaɗa saboda fargaba, Sai da Yaya babba ta yi da gaske sannan  Baba Sule ya saki hannun sahura. Ai kuwa yana sakin hannunta ta ranta ana

kare. Baba Sule na ganin haka ya rufa mata baya. Sai da ƙyar aka samu aka tsayar da su a soron gidan tare da tura Baba sule cikin ɗaki don Yayan Mahaifinsu gani yake kamar gamo ne suka yi. Dubu ban da dariyar mugunta ƙasa-ƙasa babu abin da take yi.

Sai daga baya aka farga da su Auwalu da suke ɗaki don haka da sauri Yayan Mahaifinsu ya je ya sa suka buɗe ƙofar da ƙyar, Auwalu yana maƙale da Yahanasu don gani yake idan ya sake ta kamar Fatalwar Mahaifinsa za ta yi awon gaba da ita.

Malam Idi shi ne yayan Mai Carbi, tara mutane gidan ya yi gabaɗaya yana yi musu nasiha da nusar da su illar yarda da amincewa abin da suka yi tozali da shi. Sai da ya gama wa'azin sannan ya bawa Inna Furai damar ta yi magana.

Inna Fuarai ta karkace ta ce, "Yaya Idi yadda na ga Fatalwar Malam na ga Annabi. Ganin idona na ganshi kuma har umarnin shayar da su Auwalu ya yi." Sai da suka gama jin jawabinta tsaf sannan aka ce Yahanasu ta yi faɗi abin da ta sani, Yahanasu da ta buɗe ido da kyar tana sunne kai ƙasa don duk yanda hankalinta ya ɗan kwanta har Yaya Idi ya sa ta buɗe ido bata gama sakewa ba. Ta fara yi musu bayani dalla-dalla sanna ta ɗora da cewa, "Kuma da bakinsa ya sanar da ni duk wanda ya wayi gari da likkafani a ɗakinsa to gaba shi za su ɗauka. Shi ya sa na ce tawa ta ƙare." Auwalu ya rumgumota yana cewa, "Ba za ki mutu ba Yahanasuna" Yaya Idi ya yi jim sannan ya ce, "Idan na fahimta wani ne kawai yake son razanar da mutanen gidan amma babu damuwa ku bar mini komai a hannuna zan san yanda zan ɓullowa lamarin.

Dubu tana gefe tana jin duk wainar da ake toyawa don haka ta saci jiki babu wanda ya lura da ita, kuma babu wanda ya taɓa kawo ita za ta aikata wannan abin. Dubu na tafiya ta wuce ɗakin Marigayi ta zaro wasu kayansa da yake zuwa sallar juma'a da su. A wanke suke a goge fari ƙal da su, sai da ta bubbuɗa su ta je bakin katangar banɗaki wacce mutum zai iya haurawa ta wurin ta ajiye, hularsa ta saƙale a jikin wata itaciyar tunfafiya sai kuwa ta kwaso a guje ta shiga wurin taron da suke gabda kammalawa. Ihu take kwarawa kamar wacce ake ɗanawa wuta tana cewa, "Wayyo Allah na ga Fatalwar Baffa na gani zai tafi da ni. Kafin ka ce wani abu tuni wurin ya watse sai takalma da ɗankwalaye da aka barsu suna cin karen su babu babbaka. Yaya Idi sai da ya yi kusan adungure biyu sannan ya samu ya shige ɗakin Inna Furaira. Hularsa kuwa ta yi tsalle ya fi sau biyar kafin ta samu sukuni faɗuwa can bakin ƙofa.
[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

© *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 5

Fuskar Mama Uwani ce ta rune saboda ɓacin rai nan take ta fara fesar da numfashi mai ɗauke da turirin hayaƙi mai zafi, sannu a hankali Hannuwanta suka fara fidda wasu irin baƙaƙen farata masu matuƙar kaifin gaske, harshenta ne ya fara zazzagowa haɗe da fidda waɗansu irin jeluna masu tsawo da santsi tamkar ƴaƴan maciji, fatar jikinta ce ta fara sauya launi zuwa kalar ja haɗe da wani gashi da ya fara tsattsafo mata. Cikin wata irin murya mara daɗin sauraro ta fara magana.

"Wace ce ke?" Intisar ta saki malalacin murmushi ta fara zagaye ɗakin tana ƙarewa Mama Uwani da ke ɗauke da mummunar siffa ta ce, "Menene damuwarka har kake son sanin ni wacece? Dama ka yi abin da yake gabanka don sanin wacece ni ba zai amfane ka da komai ba." A haukace Mama Uwani ta buga uban tsalle da waɗansu manyan fuka-fukai da suka fito daga ƙasan hammarta, ta dira a gaban Intisar haɗe da karta mata faratanta bisa tsautsayi farcen ɗan yatsanta ɗaya ya karci gefen fuskarta. A zafafe ta matsa baya cikin huci, nan take fatar jikinta ta fara darewa tsokar namanta ta fara bayyana  a fili, kanta ya fara rabewa gida biyu wani dogon ƙaho ta fara tsorowa daga tsakiyar kanta. Tana shirin mayar da martani daga can bakin ƙofa suka ji maganar Mommy na ƙwalawa Mama Uwani kira, kamar ƙiftawar ido tuni suka koma hallitarsu ta ainihi. Mama Uwani ta zubawa Intisar wani mugun kallo cike da takaici ta furta, "Idan kere na yawo zabo na yawo watarana za a haɗu."

Intisar ta ɗaga kafaɗa cikin rashin nuna damuwa ta ce, "Kamar yadda Ungozoma ke jiran mai naƙuda haka koyaushe nake dakon haɗuwarmu domin nasan ba a dauwama da kashi a ciki." Dire zancen Intisar ya yi daidai da shigowar Mommy cikin ɗakin wasu baƙin mata na biye da ita, kallon Mama Uwani ta yi a ɗan faɗace ta fara faɗin, "Mama Uwani kina ji ina ta magana lafiyarki kuwa?" Kamar yadda ta saba ladabi a gaban su Mommy haka Mama Uwani ta dausashe murya ta ce, "Hajiya a yi haƙuri yanzu na zo wuce wa na hangi wannan baƙuwar ta shigo ɗakin nan shi ne na shigo don na sanar mata cikin gida ake zaman makokin, wallahi na sha'afa ban ji ki ba." Mommy ta faɗaɗa murmushi tana kallon Intisar ta ce, "Yanmata sannu da zuwa." A kunyace Intisar ta sunne kai haɗe da tsugunnawa har ƙasa tana faɗin, "Mommy ina kwana?" Mommy ta dafa kafaɗarta tana ɗago ta, ta c: "Lafita ƙalau 'yata tashi tsaye." Intisar ta amsa da, "Mommy ina Raihan?" A firgice Mama Uwani ta ɗago cikin suɓutar baki ta furta, "Me Raihan za ta yi miki?"

Da sauri Mommy ta kalli Mama Uwani fuska babu walwala ta ce, "Mama Uwani ya haka ne?" Mama Uwani ranta ya sake ɓaci, ta russunar da kai tana faɗin, "Ayi haƙuri Hajiya." Mommy bata tanka mata ba, ta juya wurin baƙin da take tafe da su ta ce, "Ga baƙi nan ki wuce da su sashenku." Ta juya wurin Intisar ta ce, "Ni kamar Intisar nake gani." Intisar ta sosa kai a kunyace ta ce, "Ni ce Mommy, dama na ji abin da ya faru ne na zo in yi mata gaisuwa." Mommy ta sake goge hawayen fuskarta da yake zuba, don mutuwar Mama Hasiya ba ƙaramin dukanta ta yi ba, ta riƙo hannun Intisar don dama tun da ta ganta take yi mata kallon sani, abin da ya hanata gane ta sau ɗaya ta taɓa ganin wani zuwa da suka yi da Raihan. Intisar ta sake lafewa a jikin Mommy suka nufi hanyar fita, Mommy tana faɗin, "Allah sarki Intisar, ya su mommynku." Intisar

ta ce, "Duk lafiya ƙalau ta ce a yi muku gaisuwa kafin ta shigo." Mama Uwani jiki a saluɓe ta ja baƙin suka nufi sashensu, Intisar tana tafe tana sakin wani shu'umin murmushi haɗe da bankawa Mommy harara a fakaice.

Wuce mutane suka rinƙa yi duk in da ta keta sai gaisuwa ake yi mata, mommy har lokacin hawaye ne ɗauke a fuskarta. Suna zuwa ta wuce da ita sashen Raihan, Raihan na zaune da su Batula ƴaƴan ƙanne da yayyan mommy, suma ƴan mata ne kuma ta su ta zo ɗaya da Raihan.

Intisar na shiga Raihan ta faɗaɗa fara'arta tana miƙa mata hannu daga zaune, da sauri Intisar ta rungumeta tana faɗin; "Besti ya ƙarin haƙuri." Idanun Raihan ya ciko da ƙwallah, sai da ta sa hannu ta goge hawaye cikin shassheƙar kuka ta ce, "Besti wai Mama Hasiya ce ta mutu, idan kin tuna hirarmu da ke last ba nace miki ni na ɗauki alƙawarin Baby shower ba idan ta samu Ciki?" Intisar ta matso hawaye cikin sigar tausayi ta furta, "Kayya Besti ya za a yi na manta da hirar Mama Hasiya." Raihan ta ci gaba da kuka tana faɗin, "Intisar Mama Hasiya na sona kamar ita ta haife ni, wai ita ce ta mutu shi kenan mun rasata." Kamar haɗin baki lokaci ɗaya suka fashe da kuka mai ban tausayi, sai da ƙyar aka lallashe su musamman Raihan.

Bayan wani lokaci suna zaune tuni an sallaci Mama Hasiya an kaita makancinta, Mama Uwani ce ta turo ƙofar ta shiga saboda gabaɗaya zuciyarta ba ta aminta da Intisar ba, don tun ranar da ta fara ɗora ido a kanta ta fahimci ita ba alheri bace a rayuwar Raihan. Sai dai duk yadda ta so bin diddigin gano wacece ita abin ya faskara, don haka ko da ta shiga ɗakin sai ta hau goge-goge don ganin abin da yake faruwa. Intisar na ganin haka ta saki murmushi a fakaice don ta san tsiyar da za ta shukawa Mama Uwani, yamutsa fuska Intisar ta yi ta ce, "Besti pls ki ce Mama Uwani ba ni ruwa and takalmana suna waje ta kwasominsu." A hargitse Mama Uwani ta wurgawa Intisar mugun kallo saboda ɓacin rai har sai da ta so bayyana fushinta a fili, kai tsaye Raihan ta dubi Mama Uwani ta ce, "Mama Uwani ki ɗaukowa Intisar ruwa a falo na firij ɗina ya ƙare." Ganin rainin hankalin Intisar ya yi wa Mama Uwani yawa ya sa bata tanka wa Raihan ba ta kalli Intisar, ta fara wani huci idanunta suka fara sauya lauyi ba tare da Raihan da sauran mutanen ɗakin sun lura ba.

Kofar toilet ɗin Raihan ta kalla lokaci ɗaya kofar ta buɗe da ƙarfi, wani tafkeken maciji ne ya fara silalowa bakinsa na fidda baƙin hayaƙi. Wata uwar ƙara suka ƙwalla a firgice kowa ya fara neman hanyar fita, kafin wani lokaci tuni duk sun fice daga ɗakin har Intisar don ko kaɗan bata yinƙurin yin wani abu a gaban Raihan da zai bayyana ita ainihin wacece.

Mama Uwani nan take ta ɓace a wurin, macijin ra rabu gida biyu ɗaya ya rikiɗa zuwa siffar Raihan ɗaya kuma yana nan a siffarsa ta farko, ita kuma Mama Uwani ta ɓace tare da Raihan ɗin ainihi. Kamar ƙiftawar ido haka Mama Uwani ta ɗira a wani tsibiri mai ɗauke da dogayen bishiyu masu duhun gaske, sai wasu korayen tsuntsaye masu yawan da wasu hallitu masu siffar ƙadangaru sai dai jelunar su gashi gare ta kamar jelar tunkiya. Raihan da take sume ta shimfiɗar, Mama Uwani ta zauna ta zura mata ido, nan take ta rikiɗa zuwa surarta ta ainihi wato HUZAIFA. Miƙewa ya yi da surar wata ƙatuwar hallita mai matuƙar tsawo, fatar jikinsa kamar bayan kada ga wata zabgegiyar jela a bayansa mai ɗauke da kawunan macizai masu fidda

aman wuta. Hannuwansa ɗauke suke da manyan farata sai harshensa da suke dalalar da wani baƙin ruwa mai yauƙi.

Kamar wancen karan da ya kaita daularsa ta ƙarƙashin ƙasa, a yanzu ma zuwa ya yi daidai wurin da take kwance ya zuba mata ido wata matsananciyar sha'awar Raihan na sake fisgarsa. A hankali Raihan ta sauke ajiyar zuciya sanyin shukokin wurin ya fara dukan gangar jikinta, motsi ta fara yi alamar za ta farfaɗo. Ruwan bakinsa ya ɗiga mata a saitin goshinta, a cen gefe ya je ya ɗauko wannan ƙaramar hallitar mai siffar kunkuru ya ɗagata da hannuwa biyu yana kallo yana jin daɗi, domin babu abin da ya fi saurin faranta ransa sama da ya ga ya haɗa Raihan da abin da ta haifa masa. Mayar da jaririn hallitar ya yi sannan ya dawo kan Raihan da ke kwance, a hankali ya fara mu'amala da ita yana sarrafa sassan jikinta ga wata irin kewarta da ya yi don ya jima bai kusance ta ba, tun ranar da ta haifi wannan mumummunar hallitar tun da ba ya iya ɗaukan kwana biyu cir ba tare da ya kusance ta har ya yi mu'amala da sassan jikinta ba.

Yana tsaka da mu'amala da ita ya ji wata iska ta fara, kaɗawa mai tafe da sarewa. A hankali ya ɗago kansa yana  kallon abin da yake faruwa don ko ba a faɗa ba, ya san Mugaza ce za ta dira a wurinsu. Tun bai gama tunaninta ba ya ji kecewar dariyarta a tsakar kansa, miƙewa ya yi daga kan Raihan a lokacin ya bayan ya samu nutsuwa da ita, ya taka wurin Mugaza fuska a haɗe cikin wata irin murya ya furta, "Me ya kawo ki Turakata bayan kinsan hutawa nake yi?" Haushi ne ya sake rufe Mugaza da ke ɗauke da surar wani ƙaton tsuntsu mai kan angulu. Sai da ta yi tsalle-tsallenta sannan ta dira a gabansa rai a ɓace ta mayar masa da martani, "Akwai wani hutu da ya dace ka yi bayan bana kusa da kai?" Huzaifa ya ƙare mata kallo yana shirin magana ta ci gaba da cewa, "Sau nawa zan gaya maka ka fita daga rayuwar yarinyar nan, idan ba haka ba wallahi sai na halakata ta hanyar kisa mai muni." Wani uban tsalle ya buga haɗe da girgiza sannan ya rikiɗa zuwa surar matashin saurayin bil'adam, ya kalli matarsa Mugaza tare da sakin wani shu'umin murmushi ya ce, "Wannan yarinyar da kike gani na fansar da raina a gareta idan kin ga ban tsayawa rayuwarta ba sai dai bana numfashi, ita ɗin ta zama jinin jikina ko iyayen da suka haifeta idan suka nemi raba ni da ita sai na tarwatsa rayuwarsu." Jinjina kai Mugaza ta yi haɗe da sakin wata irin shu'umar dariya sannan ta ce, "Wannan shi ne gargaɗi na ƙarshe da na yi maka a kanta, tun da baka ji ba za ka ga ni a gaba kuma idan kwaɓarka ta yi ruwa karka yi kuka da ni. Sai dai zan ci gaba da baka kulawa a matsayina na matarka mai ƙaunarka, amma a kan wannan yarinyar babu wata kalma da za ta sake shiga tsakaninmu. Sai na ladaftar da ruhinta ta yadda za ta yi danasani, sai na azabtar da gangar jikinta domin sai na shayar da ita azaba mai raɗadi" Tana gama maganar ta tashi daga cikin tsibirin ta fice, ko a jikin Huzaifa ya ƙarasa wurin da Raihan take kwance ya sake rikiɗa zuwa siffar marigayya Mama Hasiya haɗe da sauya fasalin wurin, a hankali ya sa hannu ya fara tashinta tare da faɗin sunanta. Ahankali ta buɗe idonta tana kallon wurin da take da Mama Hasiya da take kanta a tsaye.

Bayan fitowar su Intisar a kan idonta Mama Uwani ta sauya Raihan da wata Raihan ɗin, murmushi ta yi don ta fahimci manufarta na yin haka kuma ita ma ta shiga nazartar yadda za ta ɓullo mata. Nan take gida ya ruɗe da maganar macijin da aka gani a ɗakin Raihan, hankulan

mutane ba ƙaramin tashi ya yi ba. Lokacin da Mommy ta samu wannan labarin da sauri ta aika aka kira Kabiru (Matashin bafulatani Maigadin gidansu Raihan.) Saboda Kabir bai da tsoro sam, bai fi sati biyu da fara aiki a gidansu Raihan ba. Tsayayyen namiji ne mara tsoro don akwai ranar da aka samun kulɓa a kitchen ɗin Mommy, Kabiru na zuwa ya fitar da shi. Kafin Kabiru ya zo Sulaiman ɗan ƙawar Mommy ya miƙe yana faɗin, "Daga wurin ina yake yanzu na fice da shi, ba wani shege kura ma mun kara da ita mun kaita ƙasa." Babu wanda ya hana shi don jikinsa na rawa ya nufi cikin gidan, saboda yana mutuwar ƙaunar Raihan don haka yake son ya yi wani abin bajinta ko ya samu ya ƙara samun masauki a zuciyar Raihan.

Yana zuwa duk matan da ke zagaye da ɗakin suka dare, ya tura ɗakin da ƙarfinsa. Yana shiga ya samu macijin a tsakiyar ɗakin ya naɗe wuri ɗaya kamar gammo ya fasa kai, bakinsa yana fitar da feshin wuta, a hankali ya waiga yana faɗin: "Wani ya miƙo min katako." Har rige-rigen tafiya mutane suke yi babu jimawa aka ɗauko masa wani ƙaton katako, kansa tsaye ya tunkari macijin cikin dakiya ya ɗaga ya buga masa a tsakiyar ka. Tsalle macijin ya yi, Sulaiman ya gantsare duniyar na juya masa. Sannu a hankali macijin ya rarrafo ya fara nannaɗe shi har sai da ya naɗe masa jiki, nan take Sulaiman ya hau kakari ƙwayar idonsa duka biyun ta faɗo ƙasa, jini ya fara zuba ta hancinsa da bakinsa. Tun Sulaiman yana iya kakari har ƙarfinsa ya ƙare, tsokar jikinsa ta fara burtsowa daga jikin fatarsa nan take hallitar Sulaiman ta sauya tamkar ba bil'adam ba. Mutane na ganin haka suka fita da gudu cikin kururuwar neman taimako.

************

Raihan ta shi ta yi zaune jikinta ba ƙaramin tsami ya yi mata ba, ta dubi Huzaifa da ke cikin siffar Mama Hasiya ta ce, "Mama Hasiya kece? Dama baki mutu ba?" Huzaifa ya gyaɗa wa Raihan kai yana furta, "Ban mutu ba amma na dawo nan wurin da zama za ki zauna da ni?" Raihan ta yi shiru tana nazartar maganarsa jiki a sanyaye ta ɗago tana cewa, "Gaskiya ban yarda ba ina su Mommy?" Huzaifa ya riƙo hannunta lokaci ɗaya ta ji wani yaarrr a cikin jikinta, tana kiciniyar ƙwacewa sai gani ta yi ta fisgo da ƴan yatsu biyu na jikin hannun Huzaifa, a tsorace ta wurgar da su ta fara ja da baya jikinta na karkarwa. Cikin rawar murya ta ce, "Don Allah ki yi haƙuri karki cutar da ni." Ganin haka ya sa Huzaifa ya fara ƙyaƙyacewa da wata irin dariya har sai da ta sa hannuwa biyu ta toshe kunnuwanta, kakin yawu ya yi ya tofar nan take ƙasar wurin ta fara rozayewa ya sa ɗan yatsa ya nuna mata wurin yana faɗin, "Ki bar wahalar da kanki domin ba za ki taɓa guje min ba, ki zo ki shiga wurin nan idan ba haka ba za ki dauwama a wurin nan."

*********

Al'ummar da ke zaman makoki kusan rabi da kwata kowa ya cika wandonsa da isa, don ceton rayuwarsa. Hatta Inno da Goggo cikin ayarin ƴan ceton rai suke ba tare da su mommy sun farga ba. Hankalin Daddy ba ƙaramin tashi ya yi ba da ganin abin da ya faru, a hankali Kabiru ya fara takawa cikin gidan dukda yana ta cin karo da mutane masu guduwa hakan bai hana shi sake kutsawa cikin falon gidan da zai sadaka da ɗakin Raihan ba, a bakin wata ƙofa ya ci karo da Intisar da ke tsaye ƙyam babu alamar tsoro a tattare da ita. Suna haɗa ido ya ji

kansa ya sara juwa ta fara ɗibansa, sama-sama ya fara jin wata irin hayaniya har sai da ya dafa kansa da hannuwansa, a hankali ya fara karanto addu'o'in tsari yana karantawa duk wacce ta zo bakinsa. Lokaci ɗaya ya ji komai ya ɗauke masa, ya dawo cikin hankalinsa sai dai tuni jikinsa ya jiƙe da gumi sharkaf. Idanu ya kafe Intisar da su har ya gagara sarrafa kansa, ya fara takawa zuwa gabanta cikin hausar da bata gama zama a bakinsa ba ya ce, "Washeshe kai?" Intisar ta saki murmushi ta ƙarasa gaban Kabiru ta ce, "Kai bafulatanin ƙauye, karka shiga abin da babu ruwanka." Yana shirin sake magana Daddy ya ƙaraso wurin hankali a tashe yana faɗin, "Kabiru mu je ka ga abin da yake faruwa meye abin yi?"  Kabiru ya yi gaba yana waiwayen Intisar haɗe da ɗora mata zarge-zarge a kanta.

Da ƙarfin gaske Kabiru ya tura ƙofar ɗakin cikin zuciyarsa yana ci gaba da karanta ayoyin tsari dana kariya, Jabun Raihan ce ta ƙaraso ƙofar ɗakin. Abin da ya ji da farko a lokacin da yake tare da Intisar haka ya ƙara ji a wannan karon a haukace ya juya, ya shaƙi wuyan Raihan cikin wani irin ƙaraji ya furta.

"Washeshe kai? Me kake yi a wurin nan?"

DA ALAMA KABIRU YA YANKI TIKITIN BARIN AIKIN GADIN DA YAKE YI A GIDANSU RAIHAN😂 TO WAI SHI MA KO YANA DA ALAƘA DA SU NE😂  SHIN DADDY ZAI ZURA IDO YA GA AN MAƘURE GUDAN JININSA? SHIN SU DADDY ZA SU FARGA DA MAMA UWANI BA MUTUM BACE SHI NE AINIHIN ALJANIN DA KE RAYUWA DA ƳAR'SU? KO KUMA HUZAIFA ZAI ƘYALE KABIRU HAR YA TONA MUSU ASIRI🤭🤭🤭

TAFIYAR FA HAR YANZU BA A FARA BA DOMIN LABARIN TAFE YAKE DA SARƘAKIYA🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️  KARKU MANTA HAR YANZU RAIHAN BATA SAN MAMA UWANI CE TA KAWO WANNAN TSIBIRIN BA, ITA DAI TA BUƊI IDO DA MARIGAYYA MAMA HASIYA. WAI INA LABARIN INNO DA GOGGO NE INA SUKA BAZAMA WAYE ZAI TARO SU? 😂😂

Share Fisabillah🌚
[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

©  *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 7

Daddy yana tafe Raihan na riƙe a hannunsa har suka shiga cikin gidan  ayyane-ayyane yake yi, yana mamakin wane irin macijine da nan take zai naɗe mutum ya kashe shi, kuma a ce ya fito daga ɗakin Raihan ɗin sa. Kwafa ya yi yana tunanin irin matakan tsaron da zai ƙara akan na da, har suka shiga ciki. Mommy jikinta ba ƙaramin sanyi ya yi ba don tun lokacin da abin ya faru ta fahimci macijin ɗakin Raihan ba ainihin dabba ba ne. Sai dai a wannan karon ta ci alwashin faɗawa Daddy gaskiya duk irin ɓacin ran da zai yi, don haka suna zuwa ta nemi ganawa da shi a sabon ɗakinsa dama gidan ya gina shi ne da sunan bayan wasu watanni su tare, amma kasancewar ba a gama masa ƙaƙale-ƙaƙale ba ya sa suka dakata da komawar, amma dole ta sa suka tashi a rana tsaka suka koma. A gaggauce Daddy ya dubi mommy ya ce, "Faɗi ina jin ki, kin san yanzu aka yi mini waya wai ankai su Inno da Goggo Hisba dole sai na zo, wani tashin hankali wai an tsinci su Inno a cikin masallacin Malam Isa na ƙarshen layi." Sai a lokacin Mommy ta zaro ido don bata san abin da yake faruwa ba, ganin ta shiga tashin hankali ya sa ya dube ta fuska ba walwala ya ce, "Ba fa wani abu ne na ɗaga hankali ba, komai ya zo da sauƙi yanzu dai ina zuwa." Yana gama maganar ko jiran cewarta bai yi ba ya fice daga ɗakin, jigum Mommy ta yi abu goma da ashirin ya haɗe mata.

Wani irin zafi Kabiru ya fara ji a jikinsa kamar wanda yake gaban wuta, hajijiya ya ji ta fara ɗaukansa ga wata irin matsa da macijin yake yi masa, tun yana daga tsaye har ya durƙushe a wurin yana son furta ayar Allah, amma macijin ya matse masa maƙogaronsa. Kakari ya fara yi kamar wanda ransa zai fita, a zuciyarsa yana son biya ko da ayatulkursiyyu ce amma wani abu mai nauyi ya ji ya tokare masa ƙirji kamar dutse. Yana cikin wannan halin ya ga ɗaya daga cikin macizan ya miƙe tsaye cak ya fasa kai, a hankali fatar jikin macijin ta fara saɓewa tana fita daga jikinsa sai kuma ya fara rikiɗa daga siffar maciji zuwa siffar bil'adam. A hankali wata matashiyar mace ta bayyana ilahirin jikinta gashi ne tun daga kanta har zuwa ƙugunta, ya yin da ƙugunta yake a nannaɗe cikin surar maciji. Harshe ta fara zaro masa nan take wani jaririn maciji ya faɗo, ta damƙe shi a hannunta ta kalli Kabiru da yake cikin mummunan hali ta fara magana, "Kai matashin bafulatani, wa yace maka takun saƙa da ni sauƙi gare shi? Ka san wa ka illata kuwa? Ka san wa ka kashe min kuwa? Ko kana tsammanin ka ci bulus ne?" Kabiru ya ɗago yana sauke numfashi da ƙyar idanunsa jawur ga gumi na ci gaba da tsiyaya daga jikinsa. Baki yake son buɗewa amma ya kasa, ganin haka ya sa ta sake bushewa da wata mahaukaciyar dariya sai da ta yi mai isarta sannan ta fashe da matsanancin kuka, ta jima tana yi sai ta tsagaita da kuka ta sake kallonsa ta ce, "Ba kai kana taƙama da addu'a ba ka yi ta mu gani, har za ka kashe min miji kana tunanin za ka zauna lafiya?" Macijiyar na gama maganar ta fara rarrafowa zuwa gaban Kabiru, ganin ta nufoshi gadan-gadan ya sa Kabiru ya ƙara yunƙura yana ja da baya, ya fara bude baki yana ƙoƙarin karanta addu'a haɗe da motsa baki sai dai ko kaɗan muryarsa bata fitowa, tana tunkararsa hushin numfashinsa ya doki gangar jikinta ba shiri ta ja da baya saboda wani irin zafi da ta ji yana fita daga bakinsa. Kallon-kallon suka fara yi a tsakaninsu, bata daddara ba ta sake yunƙurowa a kashi na biyu da niyyar hallakashi. Duk yadda Kabiru ya kai ga buɗe muryarsa ya yi addu'a abin ya gagara. Dabara ce ta faɗo masa ya fara biya ayatulkursiyyu a zuciyarsa, tana tunkaro shi ya fara tofa masa. Ganin tana niyyar hallaka ya sa ta sake yin baya, nan take macizan da ke gewaye da shi suka ɓace. Katon da ya

naɗe shi tuni jikinsa ya saki da ƙyar ya rarrafa ya bi ta jikin bangon ɗakin ya ɓace. Ɗakin Kabiru ya rage daga Macijiyar sai Kabiru, ya yin da ta sake kafe shi da ido tana ƙare masa kallo don ta fahimci makasar da za ta samu a jikinsa ta yi masa illa. A wahalce Kabiru ya faɗi can gefe yana mayar da numfashi, jikinsa gabaɗaya ya yi ja saboda irin tsananin matsar da macijin ya yi masa. A hankali jikinsa ya fara raɗaɗi, yana kai idanunsa kan fatarsa ya lura da yadda ta fara sauya launi zuwa fatar maciji. Macijiyar kallon Kabiru ta yi ta fara ƙyaƙyacewa da wata irin shu'umar dariyar ƙeta, hankalin Kabiru ba ƙaramin tashi ya yi da ganin abin da yake faruwa da fatar jikinsa ba. Yana tsaka da tunani ya riski muryar macijiyar tana faɗin, "Ka kashe min mijina ba tare da wani dalili ba, Huzaifa ya nemi tallafin mijina akan ya zo taimakonsa ka kashe shi, zafin mutuwarsa ta sa na ji tamkar na kashe ka amma ba zan kashe ka yanzu ba sai na gama wahalar da ruhina da gangar jikinka sannan na hallaka da hannuna. Ka je ko da wannan hallitar fatar macijin na barka ƙuncin rayuwar duniya ya ishe ka." Tana gama maganar ta sake naɗewa ta koma murtukekiyar macijiya, juyi ta fara yi daga wurin da take nan take ta baje a ƙasa ta fara nutsawa cikin ƙasa har ta ɓace ɓat. Ilahirin jikin Kabiru ban da rawa babu abin da yake yi, babban tashin hankalinsa yadda ya ga fatar jikinsa ta koma ta maciji illa iya fuskarsa, hannu da ƙafarsa ne kaɗai basu rikiɗa ba da yake macijin bai taɓa masa nan ba.

A fusace Hatsabibiya ta ɗago da ta sake kallon Intisar ta ce, "Idan ba mu kashe shi ba kina da hanyar da za mu ɓullo masa? Ko kuma kina da shawara akan yadda za mu kawar da tunaninsa akan Raihan?" Intisar ta yi shiru tana nazari don ita kanta ta san wanene Huzaifa da tsananin bincike irin nasa, ta san tun da ya kafa mata ƙahon zuƙa dole zai bi diddigin wacece ita da asalinta. Ta san muddin ya gano ta ba ƙaramar ƙura ce za ta tashi a tsakaninsu ba, a baƙar zuciya irin tashi yana iya hallakata. Don ma tana amfani da sirrin tsafi da sihiri ko a yanzu yadda ya ɗora ransa akan Raihan da tuni ya gama da ita. Tana cikin tunani ta sake riskar muryar Hataabibiya ta ci gaba da cewa, "Idan har baki da wata dabarar ga tawa shawarar." Intisar ta dubi Hatsabibiya tana sauke ajiyar zuciya ta ce, "Ina jin ki Uwargidana maganin kukana, da ke da Abar bauta ku kaɗai na dogara da ku duniya da lahira (Wa'iyazubillah) ke kika saba ɗauke min duk wata damuwata a yanzu ma ina biye da ke don jin mafitar da za ki kawo mana kafin abar bauta ta bayyana."

Hatsabibiya kanta ya sake girma, ta miƙe daga wurin da take ta ɗauki wani dogon ƙaho mai faɗi da tsawo ta kafa shi a bakinta sannan ta durƙushe a gurin. Ta kafa tsinin ƙahon a doron ƙasa sannan ta busa shi da ƙarfinta, lokaci ɗaya tsibirin ya ɗauka tsananin ƙararsa kamar zai tsaga dajin gida biyu. Tun bata rufe baki ba aljanu masu ɗauke da munanan hallitu suka fara fitowa wasu daga ƙarƙashin ƙasa wasu daga cikin duwatsu ya yin da wasu suka fara fitowa daga ɗakin tsafi. Kafin wani lokaci tuni sun taru suna masu sujjada a gabanta, tare da yi mata kirari kamar yadda suka saba sannan suka ƙame wuri ɗaya suna jiran umarninta.

Wani irin kuka haɗe da dariya ne ya fara tashi, lokaci ɗaya tsibirin ya fara girgiza suna nan tsaye wannan mummunar hallitar mai ɗauke da kawuna (Abar bauta.) Ta ziro kawunanta zuwa harabar wurin da take. Suna yin tozali da ita suka kwanta a wurin har hatsabibiya suna masu yi

mata sujjada, haɗe da kirari.  Kafin ƙiftawar ido Wani baƙin aljani ya dira a gabanta cikin girmamawa yana tambayarta.

"Ya ke uwargijiyata shin jariri kike buƙata, uwar jariri tsoho ko tsohuwa kike buƙata." Ɗago da kawunanta ta yi, sai ta saki kuka kamar na bujimin sa. Jin kukan San ya sa aljanin sake rissunawa yana faɗin, "Kin samu kin gama." Yana gama maganar ya ɓace daga wurin.

Kallonsu ta yi ɗaya bayan ɗaya sannan ta fara magana da murya mara daɗin sauraro, "Duk abin da kuka tattauna mun saurara don haka babu amfanin maimaitawa sai zartar da hukunci." Jikin Intisar tuni ya fara tsuma nan take gumi ya rufe ta, don bata san irin hukuncin da Abar bauta za ta yanke a kan Huzaifa ba. Tana tsaka da nazari ta riski muryarta tana ci gaba da cewa, "Ba za mu kashe Huzaifa ba sai dai dole a sauyawa taku salo, sanin kanku ne a da ɗanyan kifi yana haukatata. Sakamakon ɗan da ta haifawa Huzaifa yana da haɗin jinsi da hallitar kifi. A yanzu za mu sake haukatata fiye da lokacin baya, a cikinku waye zai iya aiwatar da abin da muke buƙata?" Wata aljana da ta miƙe tsaye tana faɗin, "Abar bauta zan riƙa haukatata da surar mahaifiyarta..." Tun bata rife baki ba Abar bauta ta katse ta cikin tsawa tana cewa, "Kina tunanin wannan mafita ce? Idan kika yi haka dole za su nema mata lafiya, mu kuma duk wanda zai nuna hanyar lafiyarta sai mun tsotse jininsa." Haka aljanun da ke wurin kowa ya riƙa ɗaga hannu yana faɗin abin da zai aiwatarwa Raihan. Duk acikinsu shawarar guda biyu aka ɗauka, ɗaya daga ciki ya ce zai riƙa shiga jikin maguna yana haukatata, sai wacce ta ce za ta riƙa shiga jikin ƙadangaru sai dai kowanne da abin da zai aiwatar.

Abar bautarsu ta ji daɗin abin da suka yi, don haka ta yi na'am da wannan shawarar. Suna nan zaune aljanin da ya tafi ɗauko mata jinin da za ta sha ya dawo hannunsa ɗauke da wani Dattijon tsoho, suna shigowa tun ba su ƙarasa gaban abar bauta ba, ta miƙa hannunta guda ɗaya ya warto Dattijan haɗe da ƙwaƙule masa ido tun bai ƙarasa gabanta ba ya yi fata-fata da shi, sauran kawunan da ke jikinta suka kafa kawunansu nan take suka gama da Tsohon. Aljanin ya sake russunawa yana faɗin, "Abar bauta ya isa ko a ƙaro wani." Gyatsa ta yi, tana lashe jinin bakinta, sai da ta tsotse ƙashin ƙoƙon kan tsohon sannan ta ɗago ta ce, "A ina ka samu wannan hallitar mai daɗi?" Aljanin ya washe bakinsa yana murmushi bakinsa ya yi girman rijiya saboda wannan ne karona na farko da abar bauta ta yabi naman ɗan'adam. Ya russuna yana faɗin, "Fansar iyayena na mallaka miki abar bauta, ki fanshi wanda kike so. Ke kika hallakawa kike tseratarwa kike kashewa kike rayawa, na samu hallitar bil'adam a cen bakin wata ƙatuwar bola fitowarsa kenan daga wurin Boka Harisu, yana shirin saka laƙanin asirin da aka bashi a ƙarƙashin shara na ɗauko maka shi." Hatsabibiya ta sake kallon wurin da ƙoƙon kan Dattijon yake tana hura masa iska nan take ƙoƙon kan ya fara mirginawa, har sai da ya yi sau uku sannan hallitar tsohon ta sake dawowa kamar yadda take har da kayan jikinsa. Abar bauta ta kalli Aljanin da ya kawo Dattijon ta ce, "A ɗauke shi a mayar da shi wurin da yake rana ita yau a sake dawo min da shi jinin jikinsa bai ishe ni ba." A firgice tsohon ya kalle su nan take jikinsa ya hau tsuma, ya tsugunna yana roƙo da magiyarsu, yana cikin haka ya ga anɓace da shi daga wurin.

Abar bauta ta dube su ɗaya bayan ta ce, "Na wakilta guda ɗaya daga cikinku da ƙadangare

da mage, kuma ya zama wajibi a yau ba sai gobe Raihan ta kawo mana ziyara, shi kuma Huzaifa ku bar min lamarinsa a hannuna amma ba zan cutar da shi ba ko halaka shi alfarmar Mugaza da take kawowa ƙungiya ci gaba." Wata gwauruwar ajiyar zuciya Intisar/Mugaza ta saki tana lumshe ido, ɗaya bayan ɗaya suka fara darewa daga wurin, Hatsabibiya ta yi wa abar bauta rakiya zuwa turakarta sannan ita ma ta ɓace daga wurin.

Daddy shi da abokinsa Alhaji Mustafa suka ƙarasa ofishin Hisbar da su Inno suke, yana zuwa ya samu su Inno a zaune duk sun yi zuru-zuru kamar waɗanda suka wuni suka kwana basu ci ba, musamman Inno da take tsaka da jin mutuwar Hasiya. Suna ganinsa Inno ta fashe da kuka ta kalli ɗan hisbar da ke gefe tana faɗin, "Amma dai kai ƙaramin ɗan sanda Allah ya watsa maka albarka, wallahi ku bar ni a ofishinku amma ni da gidan Audullah sai a lahira ma sadu da juna." Daddy yana shirin yin magana Goggo ta tsugunna a gaban ɗan hisban ta ce, "Yaro ka dubi Allah ka dubi Ma'aiki  ko tasha ne ka kaini na wuce albasu." Daddy ya sauke ajiyar zuciya yana faɗin, "Inno me yake faruwa zuwa na yi mu tafi fa." Inno sunne kai ƙasa ta yi kamar ba ta ji me yake faɗa ba, ta kalli Goggo ta ce, "Don Allah ki duba min hallitar jikin Audullahi ta cika ko akwai nasaka, ada na ƙaryata ki amma Allah ya sani gidan Audullahi Makarai ne suke cin karensu babu babbaka a ciki." Daddy zai yi magana ɗan hisbar ya dakatar da shi, don labarin abin da ya faru tuni ya karaɗe ko'ina musamman da ƴan jarida suka samu zancen yaɗawa, Likitoci suka shiga binciken gawar Sulaiman a ya yin da suke neman Kabiru babu inda ba a duba ba amma basu ganshi ba.

Ɗan hisban da kanshi ya yi wa su Inno nasiha, ya sake faɗarkar da su da cewar duk wani abu yana faruwa ne da izinin Ubangiji kuma addu'a takobin mumini ce. Da ƙyar da suɗin goshi aka samu su Inno suka bi Daddy gidan har sai da ya tabbatar musu da cewar ya sauya musu wurin zama.
Lokacin da su Inno suka koma gida tuni gidan ya yi shara-shara babu mutane sosai, don tun a tsohon gidansu ganin abin da ya faru ya sa mutane da dama kowa ya yi ta kansa. Su Goggo a ɗaɗɗare suka shiga sabon gidan, suna tafe bakinsu na motsi da alama addu'a suke yi don ba ƙaramin tsorata suka yi ba. Mommy da kanta ta kaisu ɗakinsu, kowacce ta zauna shiru don ƙawayensu da suka zo gaisuwa tuni kowacce ta cika wandonta da iska.

BAYAN MAGRIBA.

Raihan na kwance a ɗakin mommy lamo kamar mara lafiya, don gabaɗaya wani sukuku take jin ta kamar ba ita ba tun da ta dawo daga duniyar aljanu. Tana daga zaune ta ga wurgawar abu, da sauri ta tashi zaune tsigar jikinta na tashi. Wani ƙadangare ta gani yana buɗe mata baki alamar dariya, sai kuma ya fara ƙada mata jela yana yi yana tunkarota. Ƙura masa ido ta yi lokaci ɗaya ta miƙe tsaye, ta fisge ɗankwalin kanta nan take gashin kanta ya hargitse, ƙananan kifaye ne suka fara fita daga bakin ƙadangare. Lokaci ɗaya ta yi kukan kura ta fisgoshi haɗe da ƙwalla uwar ƙara, tana ɗaukansa ta tura kansa cikin bakinta nan take ta fisge masa kai ta wurgar a wurin gangar jikin ƙadangaren yana hannunta. Mommy da wata ƙanwarta har rige-rigen shiga ɗakin suke saboda duk wanda yake gidan babu wanda bai ji ihunta ba. Suna

tura ƙofar suka ganta a tsaye tana riƙe da gawar jangwalagwada jini yana ɗiga, ga kansa can gefe sai zare ido take tana faɗin, "Duk wanda ya ce zai hallaka mini Ɗana wallahi sai na fidda masa kai.

🤭🤭🤭🤭 WUYAR AIKI BA'A FARA BA, HAR YANZU FA ASHAFI NA BAKWAI AKE😎😎 KUN GA KUWA AKWAI SAURAN TAFIYA, AKWAI ƘURA A GABA.🤸‍♀️💃

Share Hilis🌚
[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

© *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 6

Raihan kallon ramin ta yi da yake ci gaba da rozayewa ƙasar wurin na ruftawa, ya yin da ramin yake ci gaba da ƙara girma yana tunkaro wurin da take. A hankali ta riƙa ja da baya cikin rawar jiki, firgici da tashin hankali. Tuni hawaye ya wanke fuskarta ta ci gaba da yin baya ba tare da ta fahimci wurin da take jefa ƙafarta ba, bata yi aune ba ta ji wani dutse ya tokareta ƙasar da ke zaftarewa ta ƙaraso har wurinta har sai da ya rage bai fi taku ɗaya ba ta dakata bisa bin umarnin Huzaifa da ke cikin surar Mama Hasiya. Cikin kuka Raihan ta dubi shi tana faɗin, "Don Allah ki yi haƙuri karki cutar da ni, ban san abin da na yi miki ba kika kawo ni wurin nan alhalin mommy ta ce mini kin mutu." Huzaifa ya ƙyaƙyace da wata mahaukaciyar dariya ya fara takowa wurinta yana tafe yana zare sauran ƴan yatsun hannunsa yana zubarwa, kafin ya ƙarasa wurinta tuni ya tsinke yatsun hannunsa sai iya dungulmin kaɗai ya rage, daga guraben ƴan yatsun wasu baƙaƙen farata ne suka fara tsirowa a hankali har sai da suka fito zaƙwa-zaƙwa da su, ta cikin ramin ya shiga kamar ƙiftawar ido ya dira a gabanta cikin wata irin murya mai amsa kuwwa ya sake ce mata. "Ki biyo ni cikin ramin nan idan ba haka ba za ki dauwama a nan." Raihan ta sake girgiza masa kai tana cewa, "Don Allah ki mayar da ni wurin su Mommy." Baki ya buɗe zai fara dariya wasu dogayen fiƙoƙi suka fara fitowa, da sauri Raihan ta runtse ido tana ƙwallah wata razananniyar ƙara. Wata iska ta ji mai sanyi na ratsa jikinta a hankali ta buɗe idonta, ga mamakinta sai na yi ta yi wurin ya sauya mata ta ganta wani kogon dutse mai ɗauke da ƙananan bishiyu, a hankali ta fara takawa har zuwa bakin kogon dutsen don ta hango hasken rana daga bakin dutsen. Tana fita daga cikin dutsen ta fara gudu da iya ƙarfinta don

ganin ta ceci rayuwarta.

Daga nesa-nesa ta fara jiyo kukan jarirai haɗe da haniniyar doki, a hankali ta fara rage gudunta don yadda ta lura hanyar da take tunkara a nan take jin sautin kukan jaririn na sake karaɗe kunnuwanta. Tana tafe tana waiwaye ta bata yi aune ba ta ji ta yi karo da wata murgujejejiyar hallita, hallitar riƙe take da wasu ƙananan jarirai masu surarta, tsayin hallitarta ya ninka ta sau biyu, tana da ƙiba sosai don kaurin cinyar hallitar ya yi kaurin Raihan sau huɗu. Tana ɗauke ƙafa da hannuwa irin na birrai sai ƙaton kai irin na dorinar ruwa. Bakinta tsayi gare shi idanunta kwala-kwala masu ɗauke da launin ja, Raihan na shirin ja da baya Hallitar ta ƙurawa Raihan Ido tana miƙa mata hannu alamar ta zo gare ta. Da gudu Raihan ta juya don ta koma cikin kogon dutsen, karaf ta ji ta yi karo da Hazaifa da ke ɗauke da surar Mama Hasiya sai dai kammanina sun sake munana.

Ajiyar zuciya ta sauke don ko ba komai ta ji daɗin ganinsa, hankalinta ya fi kawanciya da shi a kan na wannan mummunar hallitar. Hallitar na ganin Huzaifa ya ɗauke Raihan sun koma zuwa kogon dutsen ta juya ta koma daga wurin da ta fita, Huzaifa ya saki malalacin murmushi bayan sun koma ciki ya zaunar da Raihan akan wani faffaɗan dutse, ya zauna a gabanta yana kallonta. Tana shirin yin magana ya katseta da cewar, "Kina son komawa gida?" Da sauri Raihan ta gyaɗa masa kai. Jinjina kai ya yi sannan ya ce, "Zan mayar da ke gida amma da sharaɗin..." Da sauri ta katse shi da cewar, "Na amince da kowanne sharaɗinki indai za ki mayar da ni gida."

Wannan jaririn hallitar ya ɗauko mata mai shige da siffar kunkuru ya ce, "Ya zama wajibi ki shayar da wannan domin shi ɗin jininki ne." Idanunta ne suka firfito waje ta ƙarewa hallitar kallo tana yamutsa fuska, bai saurari abin da za ta faɗa ba ya ci gaba da cewa. "Ya zama wajibi ki yanke alaƙarki da wannan yarinyar Intisar." A hargitse Raihan ta sake ɗagowa ta yi tana kallonsa don a duniya bata da aminiya sama da Intisar, bata da wacce tasu ta zo ɗaya sama da ita amma lokaci ɗaya ya ce dole ta rabu da ita.

*********

A haukace Daddy ya yi kan Kabiru ya rufe shi da wani mahaukacin duka, sai da ya gaji don kansa sannan ya janye Jabun Raihan ya rungumeta yana sauke ajiyar zuciya. A cen gafe Kabiru ya faɗi yana sauke ajiyar zuciya yana sauke numfashi cikin wahala, ɗagowa ya yi suka haɗa ido da Jabun Raihan a fakaice ta sakar masa wani malalacin murmushi ta fara motsa baki tana magana ba tare da ta wani ya ji abin da take faɗa ba. Duk maganganun da Jabun Raihan take yi a kannen Kabiru, ransa ne ya sake ɓaci ya dubi Daddy da yake jifansa da mugun kallo, cikin bagwariyar hausarsa  ya ce, "Alhagi shi wannan yaron ba mutumin kirki ba ne, azzalumi ne so yake ya shushe ki." Daddy ya sake dunƙule hannu ya kaiwa Kabiru naushi a baki ya ce, "Don uwarka a gabana kake ce min ƴata ba mutuniyar kirki ba ce, ina maka kallon mai hankalin ashe kaima ɗan iska ne, wallahi a yau ba sai gobe ba sai an rufe min kai na ga gatanka mahaukacin banza mahaukacin wofi." Raihan da ke maƙale da Daddy ta sake langwaɓewa tana ɗangale ƙafa. Alhaji Mustafa Indabawa ne ya dubi Daddy yana faɗin, "Abokina don Allah ka yi haƙuri,

yanzu mu ƙarasa wurin da gawar yaron nan take." Kabiru ya yunƙura da kyar bakinsa na ɗigar da jini. Daddy na leƙa cikin ɗakin ya yi tozali da gawar Sulaiman, da sauri Daddy ya ja da baya jikinsa na tsuma don ba ƙaramin tsorata ya yi ba. Alhaji Mustafa shi ma yana leƙawa a zabure ya ja da baya har suna gware da Daddy. Lokaci ɗaya Daddy ya yi zuru-zuru hankali a tashe ya furta, "Wannan tashin hankalin ne ya faru a ɗakin Raihan?" Intisar da ƙarasowarta kenan ta amshe maganar da cewar,  "Daddy tun da nake ban taɓa ganin maciji mai muni irin wannan ba." Daddy da jikinsa ya gama sanyaya ya fara jinjina kai, suna nan tsaye macijin nan ya fara warware kansa daga jikin Sulaima. Ganin haka ya sa mutanen wurin suka fara darewa, Kabiru ne ya dafa ƙofar a hankali ya zura ƙafarsa ɗaya cikin ɗakin.

Kallon-kallo aka fara yi tsakanin kumurcin macijin nan da Kabiru, a hankali Kabiru ya fara karanta duk wata addu'ar tsari da ta zo bakinsa. A zabure macijin ya fara ja da baya Kabiru na sake tunkararsa, wani kofi Kabiru ya hango da ruwa a jarka da sauri ya ɗauka ya zuba ruwa a kofi ya fara  karanta ayoyin tsari yana tofawa. Daddy ban da leƙe babu abin da yake yi. Kasancewar Jabun Raihan ta san irin soyayyar da Mahaifin Raihan yake yi mata ya sa ta kwaɓe baki a lokacin da ta ga Kabiru ya tasamman halaka Macijin da ubangidanta ya turo, ta ƙwalla wata ƙara tana faɗin, "Daddy wuyana." Kabiru ya waiwayo yana kallonta, Daddy ya kai hannu kan wuyanta yana faɗin, "Mu je asibiti a duba ki, wallahi duk abin da ya samu ƴata ka kuka da kanka." Daddy ya ƙarasa maganar yana watsawa Kabiru mugun kallo. Raihan ta sake langwaɓewa ta ce, "Daddy don Allah a bar korar macijin nan kar wani ya ƙara mutuwa kawai ka kira fire service." Daddy ya kalli wurin da Kabiru yake ya ce, "Kai maza fito daga ɗakin nan kar kaima ka yi mana mushe." Intisar ta kalli jabun Raihan ta watsa mata harara, sannan ta mayar da kallonta wurin Daddy ta ce, "Daddy amma naga kamar macijin ya fara ja da baya mai zai hana a bari a ga ƙoƙarinsa..." Alhaji Mustafa ya katse ta da cewar, "Tabbas ni ma haka na gama ayyanawa don yaron nan kamar akwai wani taimako da zai yi mana." Kabiru bai bi ta kansu ba ya sake tunkarar wurin macijin, lokaci ɗaya ya watsa masa ruwan tofin hannunsa bakinsa na ci gaba da ambaton Allah. Nan take macijin ya faɗi gefe yana wani iri  gurnani, zaburowa ya sake yi da niyyar kai wa Kabiru sara da sauri Kabiru ya watsa masa sauran ruwan da ke hannunsa. Wata dariyar farinciki Intisar ta saki don ko ba komai ta san an yi wa Mama Uwani illa,  jikinsu Daddy ba ƙaramin sanyi ya yi ba da ganin gwagwarmayar da suka yi tsakanin Kabiru da macijin.

Jabun Raihan ta sake kallon Intisar ta saki ƙwafa a takaice, ta so ace Huzaifa ya bata umarni da tuni ta nunawa Intisar iyakarta. A wahalce Kabiru ya sa hannu ya hanyo macijin, ya fito daga ɗakin fuskarsa ɗauke da gumi lokaci ɗaya Daddy ya ji Kabiru ya birge shi saboda jarumtar da ya nuna, wannan ne karo na farko da ya ji ba zai iya ɗaukan mataki a kan wanda ya taɓa gudan jininsa ba, saboda yana matuƙar son mutum mai dakakkiyar zuciya. Sai dai har lokacin yana jin haushin Kabiru saboda abin da ya yi wa Raihan a idonsa.

Kusan tare suka tarkata suka fito daga sashen, kowa da abin da yake faɗa. Kabiru fita ya yi da macijin can bayan gidan Daddy ya kai ya wurgar da shi, Daddy da kansa ya sa aka rufe sashen Raihan tare da cewar sai ya kira ma'aikata sun yi wa ɗakin feshin magani, a ɓangare ɗaya yana tunanin barinsu daga gidan gabaɗaya.

*************

Raihan bata da zaɓi don haka ta gyaɗa masa kai tare da faɗin, "Duk abin da kika faɗa na amince don Allah ki mayar da ni." Huzaifa ya yi murmushi jindaɗi don shi kansa ya lura da yadda Raihan ta gama tsorata da shi. Lokaci ɗaya ya ji ta bashi tausayi, ya sa hannu ya zaro fiƙoƙin bakinsa waɗanda suka tsiro ya wara hannuwansa da niyyar Raihan ta rungume shi amma fir ta ƙi. Ya kalli fuskarta ya ce, "Kina ƙaunata." Raihan bata da zaɓi duk abin da ya faɗa sai dai ta amsa masa da amincewarsa. Tana tsaka da tunani ta ji ya ce, "Rufe idonki." Kallon hagu da dama ta fara yi a hankali ta furta, "Don Allah kar ki yi min komai." Huzaifa ya yi murmushi ya ce, "Kina rufe ido za ki ganki a gida." Tun bai rufe baki ba Raihan ta rufe idonta da ƙarfi, bata jima da rufewa ba ta ji tashin hayaniya na tashi sama-sama. Tana buɗe ido ta ganta zaune a falon Daddynsu, a hankali ta fara bin wurin da kallo, ta hango Intisar da sauran ƴanmatan da suke tare da su a ɗakinta. Suna haɗa ido da Intisar ta ji gabanta ya faɗi rass musamman da ta tuna irin gargaɗin da Mai siffar Mama Hasiya ta yi mata, a hankali ta miƙe ba tare da furta komai ba. Tana fita ta nufi sashen Mommy a kan step ɗin bene ta ci karo da Mama Uwani, tana ganinta ta washe baki ta ce, "Barka da hutawa uwar ɗakina." Sama-sama Raihan ta amsa, "Yauwa Mama Uwani ina Mommy take?" Mama Uwani ta nuna ɗakin mommy ta ce, "Tana ciki yanzu na kaiwa baƙi abinci ko na yi miki jagora." Raihan ta dakatar da ita da cewar, "A'a Mama Uwani ki je kawai." Mama Uwani ta yi murmushi tana faɗin, "Hutawarki lafiya uwar ɗakina." Raihan bata amsa ba ta wuce cikin ɗakin. Kafin Mama Uwani ta sauka daga kan bene Intisar ta doshi wurin, kallon-kallo suka fara yi wa junansu don ma mutane na zaune a falon, Mama Uwani ta saki wani malalacin murmushi ta wuce ba tare da ta tanka wa Intisar ba.

Intisar na shiga ta yiwa Mommy sallama don a cewarta za ta tafi gida, amma koda ta yi wa Raihan magana ko ƙurarta bata kalla ba balle ta tanka mata. Tun da ta ga haka ta sha jinin jikinta, don haka tana fita daga gidan ta ɓace daga ƙofar bata tsaya a ko'ina ba sai a tsibirin ƙungiyar asirinsu.

Raihan na zuwa jiki a sanyaye ta zauna, tana son sanarwa da mahaifiyarta cewar Mama Hasiya bata mutu ba amma tana tsoron abin da zai sake faruwa da ita. Tana nan zaune Daddy ya kira wayar Mommy ta waya yake sanar da ita, ɓacewar su Inno da Goggo sannan ta ce ta haɗa duk wani kayan sakawarsu don ya sa a ɗauke su daga gidan da suke zuwa gidansa da ke Unguwar sharaɗa. A cewarsa gidan cike yake da miyagun dabbobi, ba za su ci gaba da zama a ciki ba.

(Abin da bai sani ba duk in da zai je indai yana tare da Raihan tana tare da ZAUJATU JINNUL-ASHIQ😂 Idan kuma yana tare da Mama Uwani yana tare da JINNUL-ASHIQ😂 Mu je zuwa.😎)

Duk yadda Daddy ya so hukunta Kabiru ya ji zuciyarsa ta gagara ɗaukan mataki akansa, sai dai abu ɗaya ya riƙe duk abin da ya samu Raihan sai ya ɗauki mummunan mataki a kansa.  A wunin ranar suka tare a sabon gidan Daddy da ke sharaɗa, da sauran ƴan gaisuwa suka tare.

Ɗakin da ke jikin gate aka bawa Kabiru, yana shiga ɗakin ya ga akwai komai na buƙata sai dai lokaci guda ɗakin ya rikiɗe masa zuwa tafka-tafkan maciji masu fasalin irin wanda ya kashe a ɗakin Raihan. Yana shirin ja da baya ya ji wani ya faɗ masa a gadon baya lafin ya yi wani yunƙuri, ya fara nannaɗe masa jikinsa.

Intisar na zuwa ta kwashi gaisuwa wurin Hatsabibiya bungulu, bayan ta yi gaisuwa Hatsabibiya ta dubi Intisar ta ce, "Me yake tafe da ke da tsakar rana?"

Fuska ba walwala ta ce, "Hatsabibiya akwai tarin matsaloli domin Huzaifa ya saka ni a gaba, bayan Huzaifa akwai wani bafulatanin maigadinsu da alama zai kawo mana matsala. Amma wanda ya fi kawo mana matsala Huzaifa ne, don haka na ce ba zan yi ƙasa a gwiwa ba sai mun san abin yi don yanzu haka..."

Tun Intisar bata rufe baki ba Hatsabibiya Bungulu ta katseta da cewar, "Duk na ga abin da ya faru har ɗaukan Raihan da ya yi zuwa tsibirinsa." Intisar ta jinjina kai cikin huci tana cewa, "Da alama ya tsoratar da ita kuma a kowanne lokaci tana gabda bijirewa umarninmu."

"Sai mu kashe Huzaifa idan zai kawo mana matsala." Hatsabibiya ta faɗa kanta tsaye ba tare da ji shakku ko shayi ba." A firgice Intisar ta ɗago cikin tashin hankali ta zubawa Hatsabibiya ido, bakinta na rawa ta furta. "Kin manta wanene Huzaifa a wurina? Mijina ne fa." Hatsabibiya ta wara hannuwa cikin halin ko'inkula ta ce, "Ci gabanki ya fi zamantakewarki da shi don haka bana ganin zai amfane ki da komai." Intisar ta turɓune fuska ta ci gaba da cewa, "Ba zan lamince a kashe mijina kuma uban ƴaƴana ba, amma tabbas dole a nemi wata hanyar da za a samu mafita."

🤭 NA SAN DA YAWA ZA KU YI MAMAKIN JIN INTISAR MATAR HUZAIFA CE, KO KUN TUNO MUGAZA😂 ITA CE INTISAR. AMMA MAI YA SA HUZAIFA BAI GANE TA BA HAR SUKE TAKUN-SAKA, SHIN WACCE RIBA MUGAZA ZA TA CI DA TA JEFA RAIHAN A ƘUNGIYAR ASIRI? IDAN SU MOMMY SUKA KOMA SHARAƊA SUN TSIRA KO DA SAURAN TAFIYA?

Share pls🌚
[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

© *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 8

Ilahirin jikin mommy rawa ya ɗauka Aunty lubna ta zaro ido hankali a tashe don ko a mafarki bata taɓa cin karo da wannan mummunan abin da Raihan ta aikata ba. Mommy tana son tunkarar Raihan amma tana gudun hukuncin da za ta zartar a kanta, murya na rawa ta dubi Raihan ta ce, "Raihan lafiya me kike yi haka? Ƙadangare ne fa a hannunki." Raihan da har lokacin idonta jawur suke ta sake kai kallonta kan ƙadangaren hannunta, ta sake saka wurin jelarsa a baki ta cisgeta da ƙarfin tsiya ta kalli saitin da su Mommy suke ta tofar a wurin. Wani irin huci ta fara yi idanunta na sake firfitowa ta ce, "Ɗana yake shirin cinye min don haka dole na hallaka shi." Mommy ta tunkari wurin tana son Raihan ta wurgar da ƙadagaren hannunta amma tsoron abin da kaje ya zo ya hanata. Don a lokacin da take da shekara goma ntana da makamancin ciwon ta ya tashi ta taɓa cirewa wani almajiri ɗan yatsa, a lokacin shi ma zuwa ya yi zai ƙwaci agwagwar malaminsu da ta fito kiwo Raihan da Mommy sun fito daga mota, a lokacin da suka kai ziyara Albasu. Tuno da haka ya sa mommy take son tunkararta amma tana jin tsoro. Daga nesa da ita Mommy ta leƙa fuskarta tana faɗin, "Raihan ki yarda abin hannunki." Cikin wani irin ƙaraji ta nufo wurinsu gadan-gadan da ihu tini ba shiri su Mommy suka fice a guje kowa yana gudun ceton ransa.

Hankali a tashe mommy ta nufi sashen Daddy tana ƙwala masa kira. A bakin ƙofa ta ci karo da shi tana ganinsa ta fara nuna masa hanya tana faɗin, "Alhaji Raihan ce..." Maganarta ta maƙale saboda yadda take sauke ajiyar zuciya. A zabure Daddy ya kama kafaɗarta yana jijjigawa yana faɗin, "Me ya samu Raihan ɗin ki faɗa min tana ina?" Hanya ta riƙa nuna masa tana faɗin, "Tana can ta tsintsinka ƙadangare da haƙoranta." Da gudu ya nufi hanyar ɗakin Raihan hankali a tashe. Nan take ragowar mutanen da ke cikin gidan suka yi tsilli-tsilli, kallo ɗaya za ka yi musu ka fahimci tana cikin matsanancin tashin hankali.
Daddy kai tsaye ɗakin da Raihan take ciki ya tunkara yana shiga ya same ta a cen gefe ta faɗi da alama bata numfashi. Kallon ɗakin ya fara yi saboda yadda jinin ƙadangaren ya ɓata saman carpet ɗin ɗakin, daga gefen hannunta ya hangi gangar jikin ƙadangaren hannunta ya jiƙe sharkaf da jini. A hankali ya ƙarasa wurin ya mirgino da ita yana ambatar sunanta muryarsa a raunace, shiru ne ya ratso a ɗakin babu abin da yake tashi sai karar AC da saukar numfashin Daddy. Tsugunnawa ya yi a gabanta ya tallafo da kanta zuwa kan cinyarsa, murya na rawa ya furta: "Me yake samunki ne Raiha? Me ya sa waɗannan abubuwan suke faruwa da ke?" Kuka ne ya ci ƙarfinsa ya kafa kansa a jikinta yana wani irin kuka mai tsuma zuciya. Daga bakin ƙofa Mommy ce ta shiga jiki a sanyaye, ita kanta lamarin Raihan ya fara bata tsoro. Kusan shekara goma sha biyar kenan suna fama da abu ɗaya, babban tashin hankalin da ciwon kullin gaba yake yi baya raguwa. A sanyaye ta zauna a gefen Daddy ta ce, "Daddyn Raihan." Ɗagowa ya yi ya dube ta idonsa na ci gaba da zubda ƙwallah, ita ma hawaye ne ya fara zuba a fuskarta ta sa hannu ta share sannan ta ci gaba da cewa, "Ka daina kuka don yanzu babu buƙatarsa a gurbin halin da muke ciki..." Tun bata rufe baki ba Daddy ya katseta da cewar, "Ido yana zubda hawaye ne ba don gangar jiki da ruhi suna buƙata ba, sai don samun sauƙi ga raɗaɗin ƙunan

zuciya. A da na ɗauka rashin haihuwa babban masifa ne a gare ni sai ga shi a yau na wayi gari Allah ya bani gudan jinina ga kuma masifar da tafi min rashin haihuwar..." Da sauri Mommy ta rufe masa baki tana girgiza kai ta ce, "Bai kamata ka riƙa furta irin kalmomin nan ba, domin duk abin da ya samu bawa yana daga Ubangiji shi ya fi mu sanin dalilinsa na yin haka." Mommy ta numfasa sannan ta ci gaba da cewa, "Ya zama wajibi ciwon yarinyar nan a koma yin da Islamic don wannan yana da alaƙa da shafar aljanu..." A razane ya katse ta yana faɗin, "Kina hauka ne? Na gargaɗe ki da ki daina danganta jinina da jinsin aljanu." Wanna karon mommy ita ma hassala ta yi ta ci gaba da cewa, "Kar ka sake furta kalma ta ƙasƙanci a kaina, don duk taƙamar da kake yi ba kai kaɗai ka haifeta. Raihan ƴata ce idan kai ba za ka nema mata maganin Islamic ba dole ni zan nema mata." Tana gama maganar ta fice daga ɗakin, Daddy ko a jikinsa tana fita ya ɗauki waya ya kira likitan da ke duba Raihan, zayyana masa komai ya yi sannan suka yi sallama ya ci gaba da zubawa Raihan ido yana tunane-tunane a zuciyarsa.

Lokacin da Macijiyar ta ɓace daga ɗakin Kabiru, daga gefen hagunsa ya fara jin wani irin gurnani irin na riƙaƙƙun kumurcin maciji, a hargitse ya sake miƙewa yana kalle-kalle bakinsa na furta Amanarrasulu don a tunaninsa macijin ne zai sake bayyanar masa. Ya jima yana jin wannan gurnanin daga baya ya ji shiru komai ya ɗauke daga dodon kunnensa, daga jikin hannun rigarsa wata fata ya ga ta kwakkwaɓo irin saɓar fatar maciji wacce yake yi. Da sauri ya ɗago ta cikin tashin hankali don lamari ya fi ƙarfin tunaninsa, ido ya zurawa gwiwar hannunsa ta wurin da fatar ta faɗo ya ga wurin ya sake yin sheƙi tamkar bayan maciji. Kwalla ce ya ji ta zubo masa saboda duk wanda ya lura da halin da yake ciki ba zai taɓa zama a kusa da shi ba, kallo ɗaya za ka yi wa jikinsa ya firgita ka don bambamcinsa da maciji kai, hannu da ƙafafuwa. A hankali ya ƙarasa wurin buhun kayansa, nan take ya fara zazzagewa yana birkito kayan da zai saka don ya rufe jikinsa. Sanin kansa ne ko masu aikin gidan suka fahimci halin da yake ciki zamansa a cikin gidan ya ƙare balle kuma a ce Alhaji ya lura da yadda surar jikinsa ta koma. Sai da ya tura ƙofarsa ya rufeta ruf don kar wani ya turo, sannan ya tuɓe rigar jikinsa da yake mai gajeren hannu ce. A jikin mudubin ya tsaya yana ƙarewa jikinsa kallo fatar jikinsa ta koma sak irin ta maciji, wani hawayen ne ya sake gangaro masa ya sa hannu ya share sannan ya ɗauko wata tsohuwar rigar shadda mai dogon hannu, ya ɗauko wani tsohon mayafinsa da wanda ya gada a wurin mahaifiyarsa ya naɗe wuyansa da shi. A jikin bango ya jingina a fili ya fara magana cikin karyewar zuciya, "Allah sarki Baffajo ba don rashin lafiyarka ba, da babu abin da zai hanani barin wannan gidan, don da alama wannan ba wurin zama ba ne." Kabiru ya ɗaga hannu sama ya ci gaba da cewa, "Allah ka bawa Baffajo lafiya, da yardar Allah sai na bar gidan nan don na nemawa kaina lafiya." Daga gefensa ya ji an bushe da dariya, yana juyawa ya hangi matashiyar budurwa tana tsaye tsirara babu kaya a jikinta. Hannuwa biyu ta wara masa tana faɗin, "Ina da hanyar da zan kawo maka mafita matuƙar za ka bani dama." Kabiru ya kauda kansa gefe yana faɗin, "Wa'iyazubillah." Ɓangaren da ya juya fuskarsa ta sake komawa tana faɗin, "Indai akan matsalar abin da ya faru da jikinka ne zan warkar maka da shi matsawar za ka bani haɗin kai." Kabiru ya ɗago da kansa yana shirin yi mata magana, karaf idonsu suka haɗu wuri ɗaya nan take ya ji tsigar jikinsa na tashi. Da ƙyar ya iya saita kansa sannan ya furta, "Ki taimaka min ki raba ni da wannan fatar macijin, ki gaya min me kike buƙata daga wurina yanzu na aiwatar miki?"

Duk wani shige da fice da su Mommy suke yi akan idon Mama Uwani, lokacin da ta ji labarin abin da ya faru ta shiga tashin hankali don ta san wannan abin da Raihan ta aikata baya daga cikin abubuwan da take saka Raihan tana aikatawa. Fitowa ta yi ta fara kaiwa da kawowa nan take wata dabara ta faɗo mata, sai da ta shige ɗakinta da yake babu kowa a ciki sannan ta ɓace daga ɗakin. A lokacin da ta ɓace Dr Hamza yana gidansa ya gama shiri don zuwa gidansu Raihan, Huzaifa na zuwa da ya ga haka don kar ya kawi masa matsala ya bige shi a kan gado nan take bacci ya yi gaba da Dr Hamza. Cikin siffar Dr Hamza ya kira lambar Daddy bugu ɗaya kawai ya yi ya ɗauka, a gaggauce Daddy ya furta, "Dr ka ƙaraso ne?" Huzaifa da ke ɗauke da surar Dr Hamza ya amsa masa, nan take Daddy ya bashi umarni da ya shiga. Daddy da Huzaifa a harabar gidan suka haɗu, Huzaifa sai murmushi yake ƙasa-ƙasa don ko ba komai ya samu damar da zai aiwatar da abin da yake ransa. Suna shiga Raihan tana nan kwance kamar gawa bata numfashi ko hannunta baya motsawa, ido ya zura mata yana son sanin musababbin abin da ya sa ta tsinka ƙadangare gida biyu don ko kaɗan babu sa hannunsa a ciki. Yana tsaka da nazari ya riski muryar Daddy yana faɗin, "Dr don Allah ayi wani abu ciwon nan sai ƙara gaba yake yi." Huzaifa ya miƙe tsaye yana zare gilashin idonsa, ya yi jim kamar wanda yake damuwa sannan ya fara magana, "Gaskiya yanayin ciwonta ya fara bani tsoro Alhaji, amma abin da ya fi akwai wani abokina a India ina tunanin sai an fita da ita, amma a yanzu zan yi bakin ƙoƙarina na ga ta dawo daidai kafin wani lokaci. Amma idan ba shawo kan matsalar aka yi ba lamarin zai rinƙa yin gaba, tun da sannin kanmu ne a da ciwonta bai yi tsanani haka ba." Daddy kamar jira yake ya ce, "Hakan ma ya yi min daidai, abin da ya sa ma ban sake tunanin fita ba saboda ka san ba irin yawon da ba mu yi ba tun Raihan tana ƙarama."
Hamza yana shirin yin magana Inno ta turo ƙofa tana tafe Goggo na biye da ita, Inno cike da faɗa tana faɗi:

"Saboda Allah haka kawai ace duk wani tashin hankali bai faru ba sai a ranar da Ƴata Hasiya ta kwanta dama, ina dalili yarinya sai rikiɗa take kamar wahainiya. To Allah ya sani idan ban watsa mata albarka ba Mamman mai ƙawa'idi bai haife ni ba, ku bar ni yau ko ni ko Rihanu a gidan nan." Daddy ya waiga wurin Inno da niyyar zai yi magana, suna gano halin da Raihan take ciki da sauri su goggo suka yi baya cike da tashin hankali. Goggo ta dafe ƙirji jikinta sai tsuma yake yi kaɗan ya rage fitsari bai zubo mata ba, ta nuna wurin da Raihan take ta fara faɗin, "Laƙadi ja'akum yau na shiga uku. Allah ya sani duk garin Albasu babu mayya ko guda ya aka yi aka samu maita a zuri'ata, a'a wannan lamarin dole akwai ayar tambaya wallahi idan Raihanu bata shiga ƙungiyar asiri ba Na koma Albasu a ƙafa." Huzaifa ya waigo wurinsu yana faɗin, "Iya don Allah ku yi shiru ina kan Patient bana buƙatar hayaniya." Inno ta riƙe haɓa saboda takaici don gani take abin nasa kamar har da cin fuska, ƴarta ta mutu ba a yi zaman makoki yadda ya kamata ba kuma a kawo mata maganar Patient. A zuciye ta ƙarasa gaban Huzaifa sai da saita daidai fuskarsa ta wara hannunta a kai tana faɗin, "Ƙaniyarka ka ji, fitsararre kana fama da fuska kamar teba." Huzaifa ya kalli Inno a zuciyarsa yana ayyana idan da ya ga dama wurgi ɗaya zai yi da ita ta baje a ƙasa. Bai dawo daga tunani ba ya ji ta sake nuna shi da yatsa tana ci gaba da cewa, "Kai baƙin munafuki ka gaya min idan da ƴarka ce ta musu waɗannan masifun suke faruwa me za ka yi?" Daddy ya zagayo ta wurinta yana cewa,

"Inno don Allah ki yi haƙuri shi fa wannan babu ruwansa a ciki." Goggo ta leƙa fuskar Huzaifa tana kwaɓe baki ta ce, "Akan wannan baƙin munafukin kake shiga gaban mahaifiyarka?" Ta waiga wurin Huzaifa ta ci gaba da cewa, "Wallahi ka fito ka gaya masa gaskiya ko na watsa maka albarka, ka san dai ciwon Yarinyar nan bana mai jan kunne ba ne." Huzaifa ya dubi Daddy kamar abin bai dame shi ba ya ce, "Alhaji a kawo min ruwa." Daddy na jin haka da sauri ya fita daga ɗakin, yana fita Huzaifa ya warto su Inno a hannu ya matse su wuri ɗaya. Kamar waɗanda aka naɗe su da igiya aka ɗaura haka su Goggo suka ji, suna shirin yin ihu bakinsu ya yi musu nauyi. Sai da ya yi hajijiya da su sannan ya watsa su can gefe kamar kayan wanki, zannuwa da ɗankwalen su Inno tuni suka maƙale a saman fanka.

Lokacin da Raihan ta faɗi a lokacin ne Abar bauta ta bada umarnin ga Raihan da ta kawo mata ziyara, nan take ruhinta ya fita daga jikinta zuwa tsibirin da ƙungiyar asirinsu take. Tana zuwa ta russuna ta yi gaisuwa ga Hatsabibiya, a take ta turɓune fuska ta dubi Raihan tana faɗin, "Mun aika kiran gaggawa ne don Abar bauta na buƙatar ku sha jinin mai naƙuda tare da ke, kuma yau ita ce ranar da za a yi miki wankan tsarki dole ke ce za ki kawo mana jinin da za mu sha daga jikinki, Muna buƙatar jinin mahaifiyarki daga yau zuwa gobe idan ba haka ba Abar bauta za ta iya yi wa danginki ɓarna." Ruhin Raihan wata irin zabura ya yi da jin wacce aka ce ya kawo daga cikin danginta, sai dai hakan bai hanata amincewa da buƙatarsu ba. Cikin girmamawa Raihan ta russuna tana faɗin, "Fansar Mahaifana yana gare ku na baku wuƙa da nama, mai naƙuda a ko'ina take zan kawo mana ita yanzun nan." Tana gama maganar ta bi ta iska ta fice daga tsibirin.
Ruhin Raihan na fita bai tsaya a ko'ina ba sai cikin wani babban asibiti, kai tsaye daƙunan majinyata ta fara shiga har za ta fice ta hango wata tsohuwa da alama tana jin jiki, a kan ruwan cikinta ta dira har ta kafa bakinta za ta tsotsi jini majinyaciyarta ta ƙaraso gabanta tana karanta mata ayatulkursiyyu tana tofa mata saboda tuni sun samu bacci ya ɗauketa, ta karanta mata addu'a saboda ita ma bacci take son yi. Da sauri Raihan ta tashi daga kanta ta matsa gefe tana sauke numfashi,  daga can gadon ƙarshe ta hango wata mara lafiya bata jinkirta ba ta hau kanta tuni ta kafa bakinta a kanta ta fara zuƙar jini. Nan take jikin matar ya rikice ganin haka ya sa majinyaciyarta kiran nurses, sun kai mutum huɗu a kanta duk yadda suka kai ga bakin ƙoƙarinsu abin ya ci tura, nan take rai ya yi halinsa. Raihan na ganin haka miƙe ta fice daga ɗakin kai tsaye ta wuce can ɗakin haihuwa. Raihan na shiga ta hangi mata kusan uku masu naƙuda, a kan idonta ɗaya ta haihu ta cikin mutum biyun ta dira a gadon ta tsakiya. Tana niyyar kafa kanta a ƙirjinta daga bayanta ta ji an ce, "Jinin Matata ya fi ƙarfinki." A zabure ruhin Raihan ya waiga don ganin wanda ya dakatar da ita ga abin da take shirin aiwatarwa.

A MIN SHARE FISABILILLAH🌚
[11/5, 3:26 PM] Mai Agogo: *ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

©  *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

FREE PAGE 9

Rangaji ta fara yi tamkar bishiyar dalbejiyar da take kaɗawa da iskar damuna, a hankali Kabiru ya ɗan fara ja baya don ko kaɗan hankalinsa bai kwanta da ita ba. Cikin wata irin murya mai jan hankali ta fara magana, "Ka amince min da buƙatata ƙwaya ɗaya ce tal na yi maka alƙawarin yaye maka wannan matsalar da take jikinka." Kabiru da yake jin wani abu yana yawo a zuciyarsa game da ita ya runtse idonsa sannan ya fara magana cikin wata irin kasalalliyar murya, "Ba na buƙatar ganinki cikin wannan yanayin." Tun bai rufe baki ba ta ƙarasa wurinsa ta sa hannu tana ƙoƙarin taɓa shi ta furta, "Laƙani aka bani domin cikar burina a kan Daularmu ta Daulatul jinnul-Turabiy. Idan har ka amince min za ka kusance ni kuma zan warkar da kai, idan ka yi min haka zan mallaki Daularmu da abin da yake cikinta, na zo a sirrance ne ta sanadi ƴar uwata wacce ta yi maka haka..." Tana tsaka da magana ya katse ta da furta, "A'uzubillahi minnasshaiɗanirrajim." Da sauri ta ja da baya tana hakki saboda yadda ta ji wani irin hucin zafi daga jikinsa. A hankali ya tattaro jarumta ya ci gaba da karanta ayoyin kariya da duk wata addu'a da ya san ya taba biyata. Nan take ta ɓace daga gabansa don yadda take ji tamkar zai halakar da rayuwarta, ajiyar zuciya ya sauke yana runtse idonsa saboda yadda hankalinsa ya sake tashi fiye dana da. A wannan lokacin ya yanke ƙauna don ji ya yi zama a gidan ya fice masa daga rai, gani yake zai iya haƙura da zaman gidan idan ya so duk wata sana'a da ya sani zai fita ya nema don ganin ya ci gaba da nemawa mahaifinsa lafiya. Yana gama nazarin ya miƙe ya ɗauki buhun kayansa, sai da ya leƙa ta window ganin hankulan mutane baya wurinsa ya sa ya yi zaraf ya fice daga ɗakin sannan ya zare sakatar gate ɗin ya fice daga gidan. Gudu-gudu sauri-sauri haka Kabiru ya fara tafiya, kasancewar unguwar shiru babu mutane ya sa bai haɗu da kowa a hanya ba, ta bayan wata doguwar katanga ya raɓa yana tafiya ba tare da ya san inda yake saka ƙafarsa. Yana tsaka da tafiya ya ji ya ci karo da mutum a gabansa, a hankali ya fara ja baya yana ƙoƙarin sake hanya ya ji mutumin da suka yi karo da juna yana faɗin, "Assalamu alaikum." Kabiru da ya fara tsorata a ɗan ja da da baya sannan ya amsa masa sallamar, don gabaɗaya a rikice yake. Mutumin da har lokacin Kabiru bai tantance ko shi waye ba ya ci gaba da cewa, "Bawan Allah da wa ka dogara?" Kabiru ya fara sakin jikinsa don ya fahimci ɓoyayyan baƙonsa ne, murya can ƙasa ya ce, "Da Allah na dogara." Mutumin ya ƙara taku biyu zuwa gaban Kabiru ya ce, "Ka dogara da shi a ko'ina kake shi zai isar maka." Kabiru ya jinjina kai yana shirin yin magana, mutumin ya ci gaba da cewa: "Ina ƙaunarka fisabillahi don haka zan baka shawara karka ji tsoron kowa idan ba Allah ba." Kabiru na jin haka ya zaburo da sauri da niyyar kama hannun mutumin yana faɗin, "Don Allah wanene kai da kake yawan zuwa kana gaya min maganganu masu daɗi, da shawara akan al'amuran rayuwata?" Tun bai ƙarasa wurinsa ba mutumin ya ɓace, da sauri Kabiru ya hau waiwaye don neman wurin da zai ƙara

ganin ɓullowarsa. Daga can bayansa ya ƙara jin muryarsa yana faɗin, "Karka damu da sanin wanene ni domin mai ƙaunarka na tare da kai a koyaushe, ni masoyinka ne ina mai ƙara tunasar da kai muhimmanci dogaro ga Allah." Yana gama maganar ya sake ɓace wa daga wurin. Jiki a sanyaye Kabiru ya jingina a jikin katangar, ban da kukan kwaɗi da ƙananan ƙwari babu abin da yake tashi a wurin. Lokaci ɗaya ya ji zuciyarsa ta aminta da nasihar da bawan Allahn nan ya yi masa, nasihar da Mahaifinsa yake yi masa ta sake dawo masa, a fili ya fara furta Astagfirullah sannan ya koma ya nufi hanyar gidansu Raihan.

Inno kusan suma suka yi ban da juwa babu abin da suke ji, Huzaifa ya ƙarasa gabansu ya ya zaro musu ido. Suna haɗa ido suka ga ƙwayar idonsa na ci da wuta, kakin yawu ya yi ya tofar a kan tafin hannunsa nan take wuta ta tashi. Goggo tuni ta saki fitsarin da take matsewa ta sunne kai ƙasa cikin tashin hankali, Huzaifa ya buga musu tsawa yana faɗin, "Duk wacce ta sake gangancin shiga lamarin Raihan sai na banka mata wuta ta ƙone ƙurmus, kuma duk wacce ta sake ta furta wata magana a kaina da abin da ya faru sai na hallata shi cikin dare." Huzaifa ya ɗago ya damƙi wuyansu sannan ya ci gaba da cewa, "Kuma duk wacce ta ce za ta bar gidan nan tana fita zan ɗaye fatar jikinta." Inno da idonta yake runtse ta ce, "Babana mun gode, ko a ɗakin nan ka ce mu dauwama har ranar mutuwarmu mun bar sauka ƙasa." Huzaifa bai bi ta kansu ba ya ɗebe su ya watsa a saman fanka, sai ga su Inno a maƙale jikin fanka sai ciccila ƙafafuwa suke yi. Sai da suka jigata sannan ya miƙa hannunsa ya ɗauko su yana nuna musu zannuwansu dake can gefe ya ce, "Maza ku ɗaura zaninku ku fice daga ɗakin nan." Tun bai rufe baki ba Su Inno suka fara wawurar zannuwansu suna yi suna layi kamar waɗanda suka maku saboda juwar da take ɗibansu. Suna zuwa bakin ƙofa Daddy ya turo ya shigo mommy tana biye da shi Inno ta kusa tafiya luuuu za ta faɗi da sauri Daddy ya ruƙota yana faɗin, "Inno lafiya?" Inno ta fisge jikinta tana faɗin, "Sake ni ka ji Audullahi, jeka kan Raihanu Allah dai ya watsawa Likitanan albarka." Daddy ya yi murmushin jin daɗi don ya ga sauyi a wurin Tsofaffin saɓanin kafin fitarsa da ya tafi suna kwashe wa Likita albarka. Su Inno na fita suka zube a bakin ƙofa suna mayar da numfashi, Goggo ce ta fara rarrafawa tana sauka daga ƙafar bene, Inno ta leƙa tana faɗin: "Kai jama'a yanzu a daren nan za ki rarrafa Zinaru sai makarai sun makeki a hanya." Goggo da ta gama zuwa wuya a zuciye ta juyo ta ce, "Yooo shi wanda kika kuɓuto daga hannunsa Mutum ne? Ki yi ta kanki daga nan ni kam Albasu zan wuce don na tabbata ko ba aljani bane yana cikin ƙungiyar asiri, don wallahi mutum ba zai aikata abin da ya yi ba idan ba haka ba Malam mai allo bai haife ni ba." Nan take cikin Inno ya sake kaɗawa da sauri ta fara rarrafawa ta bi bayan Goggo suka sauka, suka wuce ɗakinsu.

Su Inno na fita Huzaifa ya koma kan Raihan tare da gayyato Jabin Raihan don ta maye masa gurbin Raihan ko ya samu ya sake dulmiyar da su Daddy ga zuwa ƙasar Indiya, saboda matuƙar suka je Indiya hakan zai taimaka masa wurin gano takamaimai abin da yake faruwa da ita. Kafin ƙiftawa ido sai ga Jabin Raihan ta fara motsawa tana sauke ajiyar zuciya, Sai dai babban abin da ya fi ɗaga masa hanakali da ya so ɗaukar gangar jikin Raihan zuwa Tsauninsa abin ya gagara, wannan ya sake tabbatar masa da akwai ɓoyayyan al'amari a dangane da ciwon Raihan, tashin farko Mugaza ce ta faɗo masa don ya san akan baƙin kishinta tana iya

aikata komai don biyan buƙatarta. Daddy ne ya tsinke masa tunanin da yake yi yana faɗin, "My Raihan barka farkowa." Mommy da ke gefe ta ce, "Sannu Raihan." Da ido take bin su da kallo tana gyaɗa musu kai tamkar ƙadangaruwa. Mommy ce ta koma daga ɓangaren Raihan ta tsugunna ta fara karanta ayatulkursiyyu tana tofa mata, da sauri Huzaifa ya zabura ya matsa gefe cikin huci a gaggauce yana faɗin, "Shi kenan yanzu zan wuce Alhaji duk abin da ake ciki za ku ji ni saboda akwai wani patient da yake jirana." Daddy ya miƙa masa hannu suka gaisa cikin jin daɗi ya ce, "Ba damuwa na gode sosai Dr." Da sauri Huzaifa ya yi gaba har ya je bakin ƙofa Daddy ya ce, "Dr babu wani magani da za a ƙara mata akan na da ka san fa wancen ya ƙare." Huzaifa ya fara sosa kai sannan ya ce, "Babu damuwa zan turo maka text ta waya." Tun bai jira cewar Daddy ba ya fice daga ɗakin.

A hankali Mommy ta ɗago Jabun Raiha tana yi mata sannu, Daddy ya zauna a ɗaya ɓangaren sannan ya riƙo hannunta ya ce, "Allah ya baki lafiya My Raihan." Jabun Raihan ta ɗago tana gyaɗa kai. Mommy ta miƙe tana faɗin, "Mu je na raka ki, ki yi sallah kin ga Magriba ta wuce ga Isha'i ita ma tuni an yi ta." Ras gaban Jabun Raihan ya faɗi don ko kaɗan bata ƙaunar sallah ba abin da ta ƙi jini irin ta ji an ambace ta. Idan aka ce ta yi ma bata san ta inda za ta fara ba tun da ba addininta bane, tana cikin nazari ta riski muryar Daddy yana faɗin, "Haba Zainab yaushe yarinyar nan ta farfaɗo, don Allah ki bari ta huta ta ci abinci ta sha magani tukunna." Mommy ta ɓata fuska tana faɗin, "Daddy babu wani uzuri game da mara lafiya a kan sallah, hatta majiyacin da yake kwance baya iya tashi matuƙar yana cikin hayyacinsa dole a yi masa alwala ko yana daga kwance ya gabatar da sallah..." Daddy ya katse Mommy cikin ɓacin rai yana faɗin, "So kike ki kafirta mu ni da Ƴata kenan? Ce miki na yi ba za ta yi sallah ba? Ki fita idona Zainabu akan katsalandan ɗin nan da kike min yana neman wuce gona da iri." Mommy ta miƙe cikin fushi ta fice daga ɗakin don ranta ba ƙaramin ɓaci ya yi ba.

A hargitse Raihan ta waiga don ganin wanda yake shirin dakatar da ita ga cika umarnin Abar bauta, tana waigawa ta hangi Alhaji Ƙarami abokin mahaifinta. A hankali ya fara takowa gabanta cikin izza yana faɗin, "Matata ce irin dana dasa don ya ci gaba da yaɗo domin samun farinciki da rayuwa mai morewa." Raihan cike da ƙarfin gwiwa ta juya wurinsa tana cewa, "Wa'adin yabanyarka ya zo ƙarshe don a yanzu ba sai gobe ba zan sallamawa abar bauta jininta, ko mahaifana basu isa su dakatar da ni ga aiwatar da wannan kudurin ba." A zabure Alhaji Ƙarami ya fisgo Raihan da niyyar illata ruhinta, da sauri ta kauce ya kaiwa ƙasa duka. Duk abin da yake faruwa babu wanda ya lura daga masu naƙudar dake cikin halin naƙuda har zuwa Nurses ɗin da suke taimaka musu. Raiha ta kalle shi a fusace ta nuna shi da yatsa tana faɗin, "Ka fita a ido tun ban hallaka ruhinka kai da matarka ba, ka barni na yi abin da ya kawo ni tun ban fusata na yi ɓarnar da za ta girgiza ruhinka ba." Ko ba a faɗa ba Alhaji Ƙarami ya san wacece Raihan a cikin Daular ƙungiyar asiri, dukda ba ƙungiyarsu ɗaya ba ya samu labarinta da jimawa a wurin Babban Dodo, tun da jimawa ya so ya ringajayi ruhinta zuwa ta su ƙungiyar amma Huzaifa ya yi kaka gida ya hana shi aiwatar da abin da ya yi niyya. Amma dukda ya san wannan ƙarfin iko nata ba zai hana shi tsayawa tsayin daka don ganin ya ƙwato rayuwar Matarsa ba don ita ce komai na shi a rayuwa. Ya kalleta cikin dakiya da ƙarfin zuciya ya ce, "Na

salwantar da rayuwar Mahaifana don cimma burina, na sadaukar da ƙwayoyin haihuwar jikin matata don samun farincikina, duk wani ɗigon numfashi da matata take yi ƙarin arzikina ne, matsawar babu ita duk wahalar da na yi ta tsawon shekaru ta kau don haka dole na dakatar da ke." Raihan na cikin sauraronsa ta ji kuka jariri a gefenta tana dubawa ta ga ta biyun ce ta haihu sai Matar abokin mahaifinta da suke taƙaddama akanta ita kaɗai ta rage, Raihan ta bushe da wata mahaukaciyar dariya haɗe da dukan ƙasa wurin, nan take wasu manyan kunamu suka fara fitowa suna tunkarar wurin da Alhaji ƙarami yake, da sauri suka fara rarrafawa har suka mammaƙale a jikinsa suka fara kai masa sara ta ko'ina. Da sauri ta koma kan matarsa da take cikin wani hali tana nishi da alama ita ma kan jariri ya fara hararamar fitowa, juyawa ta yi wurin da Kunamun nan suke fitowa ta sa hannu ta ɗauko guda ɗaya ta leƙa ƙarƙashin matar ta tura mata kunamar ta cikin gabanta. Lokaci ɗaya matar ta ƙwalla wata irin gigitacciyar ƙara, Raihan ta saki wani shu'umin murmushi ta waiga wurin da Alhaji Ƙarami da yake ta ƙoƙarin ganin ya ƙwaci kansa ta hanyar amfani da tsafi da sihiri, amma tuni kunamun suka kaishi ƙasa. Takawa ta yi har gabansa ta tsugunna a saitin furkarsa ta furta, "Da ka barni na yi abin da yake gabana da ka ceci rayuwarka, ba na son shisshigi a lamurana don haka bana jira ga duk wanda zai kawo min matsala." Tana gama maganar ta miƙe zuwa gaban Matar Alhaji ƙarami da Nurses suka rufu a kanta don ganin sun kawo mata ɗauki, tana nan tsaye Likita ya ƙaraso kanta don har ya fara tunanin a yi mata CS Raihan ta fara bin su ɗaya bayan ɗaya da kallo sannan ta ɗauki ruhin Matar Alhaji Ƙarami ta wuce da ita zuwa kogon tsafinsu.

A gaban abar bauta ta ɗire ta a lokacin tuni ta fara fita daga hayyacinta saboda irin saran da kunamar take yi mata, Abar bauta ce ta miƙa hannunta ɗaya daga cikin hannuwa sama da Ashirin cikin ƙasan matar, da ƙarfi ta fisgo kunamar da aka saka mata. Wata uwar ƙarar ta sake ƙwallawa kamar ranta zai fita, Abar bauta ta sake tura hannunta a karo na biyu ta fisgojaririn cikinta da tuni ƙungiyar asirin Mijinta suka zuƙe masa jini. Abar bauta wurgi ta yi da jariri zuwa ɗaya daga cikin kawunan jikinta nan take suka yayyage shi da haƙwaranta suka fatattaka namansa. Abar bauta ta dubi Raihan da ke tsaya ta fara magana da muryarta mara daɗi, "Aiki ya rage naki yau mun baki wuƙa da nama." Raihan na zuwa ta kafa kanta a ƙirjin matar za ta zuƙu jini da sauri abar bauta ta dakatar da ita da cewar, "Ba iya jininta kaɗai muke buƙata ba, muna buƙatar ki ɗebo mana kayan cikinta kafin mu sha jini, a cirowa Autan kai zuciyarta ya cinye." Raihan na gama sauraronta ta tsugunna tana kallon hannunta nan take wasu irin manyan farata suka fara tsiro mata a hannu masu kaifi da tsini kamar mashi, waɗansu manyan fiƙoƙi masu kama da fiƙoƙin zaki suka fara tsiro wa a cikin bakinta. Hannuwanta ta tura cikin gaban matar farataanta na ratsa cikin jikinta har ta samu nasarar kwaso kayan cikinta, wata irin gigitacciyar ƙara take kwararawa iya ƙarfinta tun tana cikin hayyacinta har ta fita daga hayyacinta. Kamar yadda harshen kare yake lallagi hara Raihan ta zaro harshenta ta fara lasar jinin jikin kayan cikin. Tana gama siɗewa ta wurgawa Abar bauta ta karɓe ta haɗiyesu. Hannuwanta ta ƙara sawa a daidai ƙirjinta a lokacin tuni rai ya fita daga jikin matar, da zaƙwa-zaƙwan farataanta da farke kirjin matar ta zaro zuciyarta ta miƙawa Autan kan da ke jikin Abar bauta, ta saka kanta a saitin wurin da ta ciro zuciyar ta fara zuƙar jinin jikinta.

Raihan sai da ta sha jini ta yi ƙat sannan ta ɗago, tana sauke ajiyar zuciya. Hatsabibiya na zuwa ta ja gawar matar zuwa ɗakin arziki ta wurgata ciki. Wata irin guɗa ce ta tashi a wurin mai haɗe

da walƙiya nan take ƙofar ɗakin ta shafe kamar ba'a taɓa ƙera ƙofa a wurin ba. Abar bauta ta dubi Raihan cikin farinciki ta ce, "Kin haure mataki na farko a cikin ƙungiya yanzu za ki wuce zuwa mataki na gaba, muna buƙatar jinin Mahaifiyarki. Za mu sassauta miki don ba za mu bari ki hallakar da ita da kanki ba, ungo wannan." Abar bauta ta miƙawa Raihan wani kaifaffan ƙashin bil'adama, sai dai kafinsa tamakar kaifaffiyar wuƙa haka yake. Ba musu Raihan ta ƙarasa ta amsa da hannu bibbiyu tana jiran umarninta.

Abar bauta ta miƙe tsaye tana faɗin, "Wannan da kike gani ƙashin bayan mahaifiyata ne, ki je da shi ki yanki ɗan ƙaramin yatsan mahaifiyarki ki kawo mana sauran aikin yana gare mu idan kika yi haka kin haure mata ki na biyu idan kika tafi mataki na ƙarshe tayuwu matsayinki ya zarce namu domin ke ɗin ta musamman ce, kina da bambamci da mu ƙungiya tana alfahari da ke." Raihan ta russuna cikin girmamawa sannan ta fice daga kogon dutsen.
A lokacin da ta koma gida, gidan ya yi tsit babu kowa da alama duk sun yi bacci. A can gefe ta hangi Mama Uwani da wata mai siffarta a cikin ɗakinta. Ko kaɗan bata damu ba don a baya ma ta ga irin haka, sai ta yi tsammanin duk yana daga cikin aikin abar bauta ne. Kai tsaye ɗakin Mahaifinta ta wuce don tasan a cen mahaifiyarta take kwana, Daddy ta hanga a kan kujera yana danne-danne a laptop ɗinsa a gefe ɗaya ga cool misic yana tashi don idan yana aikin dare ya fi jin daɗin aiki yana jin sanyayyar waƙa musamman ta turawa. Bata bi ta kansa ba ta ƙarasa gefen gadon da Mahaifiyarta take kwance.

😰RASHIN TAUSAYIN RAIHAN YA FARA YIN YAWA, INA TSORON TA ZAMA SHUGABA A WURIN. WAI INA LABARIN KABIRU KUMA WANENE MAI YAWAN BASHI SHAWARAR NAN? SHIN ABOKIN DADDY YANA MUTUWA KO ZAI ƊAUKI FANSA AKAN MUTUWAR MATARSA? WANNE DALILI NE YA SA HUZAIFA ZAI SA A KAI RAIHAN INDIA? IDAN YA KAITA INDIA TA FITA DAGA ƘUNGIYA NE KO YAYA?🤷🏻‍♀️🤷🏻‍♀️ CHAKWAKIYAR KARA GABA TAKE YI😂 MAZA HANZARTA KI BIYA NAKI KAR A YI BABU KE DON WANNAN SHI NE SHAFI NA BIYUN ƘARSHE💃

Share Fisabilillah🌚
*ZAUJATU JINNUL-ASHIQ*

© *AMEERA ADAM*

Littafin kuɗi ne idan kina buƙata 300 ne ta Account 3090957579 Aisha Adam, First bank. Za ki turo evidence ta wannan lambar 0706 206 2624 Whatsapp only Idan kati ne 300 MTN.

*FIRST CLASS WRITER'S ASSO...*

LAST FREE PAGES 10

Ilahirin jikin Mommy ban da karkarwa babu abin da yake yi saboda tsananin tsoro, firgici da tashin hankali. A takure take a ƙuryar gado ta sunkuyar da kanta ƙasa saboda tozali da ta yi wata shirgigegiyar mummunar hallita, girman hallitar ta zarce goggon biri ga wasu irin ƙwala-ƙwalan idanu da suka zazzago kamar za su faɗo ƙasa. Bakinta ban da fiƙoƙi babu komai a ciki sai ƙaton hancinta mai ƙofofi takwas, tare da manyan ƙahunhuna guda biyu. Sautin takun Hallitar kan iya nakasta dodon kunne don haka Mommy ta sa hannuwa biyu ta toshe kunnenta da take jin sa kamar zai tarwatse, Hannuwan hallitar kama suke da ƙafafuwan doki don haka a duƙushe take tafiya rafkeken kanta shi ne a gaba. Jin shirun takunta ya sa Mommy ta ɗago da kanta a zatonta ko hallitar ta ɓace daga wurinta, sai dai tana ɗagowa suka haɗa ido da hallitar nan take ta hango Raihan maƙale a hannun hallitar tana kuka tana miƙawa Mahaifiyarta hannu, jikin mommy har rawa yake yi ta yunƙura don zuwa wurin hallitar tana faɗin, "Don Allah ki bani ƴata ita kaɗai na mallaka karki hallakata, Hallitar ce ta fara ja da baya tare da Raihan ta fara yunƙurin kai kan Raihan zuwa bakinta don ta laƙumeta, da sauri Mommy ta yunƙura cikin tashin hankali ta furta, "Raaaaihaaaaan."

(Allah sarki Uwa kenan😰 Duk tsanani Mahaifiya ba za ta so ganin abin da zai cutar da Ƴarta/Ɗanta ba.)

Firgigita Mommy ta farka daga mummunan mafarkin da take yi, har lokacin da ta farka jikinta ban da rawa babu abin da yake yi. Da allon gado ta jingina a hankali bakinta na furta Ayatulkursiyyu don ba ƙaramin tsorata ta yi da mafarkin ba. Raihan na gabda da yankar ɗan yatsan mahaifiyarta ta ji wani irn turiri ya yo kanta da sauri ta ja da baya don kaɗan ya rage bata ƙone ba. Farkawar da Mommy ta yi ba ƙaramin ɓata mata rai ya yi ba don ta yi bakin ƙoƙarinta wurin ganin ta aiwatar da abin da yake tafe da ita. Daddy ne ya ajiye takardar hannunsa ya ɗago yana kallon wurin da Mommy take ya ce, "Lafiya dai Mommyn Raihan na ji kina ambatar sunan Raihan cikin dare." Mommy ta yunƙura da ƙyar jikinta gabaɗaya a sanyaye yake ta zauna a kujera mai kallon ta Daddy ta ce, "Daddyn Raihan wani mummunan mafarki na yi akan Raihan, ina jin tsoro matuƙa kar wani abu ya faru da ita. Maganar gaskiya ina tunanin babu shaiɗanu a lamarinta kuwa, kana gani ƙa'ida bana iya kwanciya ba tare da alwala ba kuma addu'a bakin gwargwado ina yi amma idan mummunan mafarki na tashi yi sai na da yarinyar nan a ciki..." Daddy ya yi murmushi sannan ya katseta da cewar, "Zainabu kenan, duk fa abin da kafi sawa zuciyarka yana tare da kai. Ba tun yau ba na sha gaya miki ki bar danganta ciwon yarinyar nan da wasu shaiɗanu, ki gaya min Raihan ina take zuwa da za ta kwashi shaiɗanu? Ƴarmu a killace take ban da makaranta tana zuwa wani wurin? Karki manta silar ciwon yarinyar nan tun bata fi shekara biyar a duniya ba muka wayi gari da shi, ta yaya za a ce wai wasu shaiɗanu suna bibiyarta kamar wacce take bin kwararo tana jari bola a kan sharar kasuwa." Mommy ta yi guntun tsaki tana sauke ajiyar zuciya ta ce, "Na rasa ya akayi idonka ya rufe haka, kana tunanin shaiɗanu sai a waje ake samun su Daddyn Raihan? Ganin su muke yi da za mu shaida kamanninsu? Idan a baya ta wayi ido da ciwo shin muna da lasisin da za mu tabbatar da cewar babu haɗin jinnu a jikinta..." Daddy ya ɗaga mata hannu da cewar, "Zainabu ni da ke

muka haifi yarinyar nan, don haka ki nema mata maganin Aljanu tun da so kike ki jawo mana wata masifar muna fama da wannan, shi kenan ki sakar min mara na yi fitsari." Daddy ya ƙarasa maganar a fusace yana tattara kayan gabansa, ya miƙe ya wuce kan gado, jiki a sanyaye Mommy ta shiga banɗaki ta ɗauro alwala sannan ta saka hijabinta ta nufi ɗakin Raihan don zuciyarta ta gara amincewa ta bari har gari ya waye, a hankali ta fara sauka daga bene sai dai duk taku ɗaya idan ta yi sai ta ji kamar ana bin ta a baya don sai ta ji takun tafiya, sai da ta kusa sauka daga bene ta yi ƙarfin halin juyawa amma wayam babu wanda ta gani. Idanunta ne suka sauka a kan agogon bangon da ke jikin bango wanda ya yi nuni da ƙarfe biyu da rabi na dare, wucewa ta yi hanyar da za ta sadata da ɓangaren su Raihan don gabaɗaya sashensu ɗaya idan aka cire sashen Daddy da yake ɓangarensa daban, a hankali wata sanyayyar iska ta fara kaɗawa mai haɗe da walƙiya tun iskar na kaɗawa kaɗan-kaɗan har ta fara ɗaga labulaye, ƙofofin ɗaki da na window suka fara rufewa da buɗewa a ƙarfi, da sauri Mommy ta fara waigawa don har lokacin bata daina jin alamun takun tafiyar da ake bin ta a baya ba. Tana cikin tafiya ta ga ƙwan fitilar ya fara ɗaukewa yana kawowa, ba shiri ta fara lalube har ta samu ta taɓa jikin bango ta ci gaba da tafiya a jikin bango. Daga bayanta ta ji ƙarar fashewar kwalba tuuuush, a firgice ta fara lalube tana ƙwalawa Daddy kira don iya tsoro ta gama tsorata uwa uba ga shi har lokacin bata daina jin takun tafiya a bayanta ba. Kwan fitilar ne ya tsaya cak ya daina ɗaukewa, mommy ta sauke ajiyar zuciya ta ci gaba da tafiya a gaggauce cikin sauri. Tana zuwa ta wurin windon da ya fita ta harabar gidan ta hango wata matashiyar budurwa a zaune ta kifa kanta a tsakanin cinyoyinta, da mamaki Mommy ta tsaya tana kallonta sai jikinta ya fara bata kamar Raihan ɗinta don kusan yanayin jikinsu ɗaya, hatta doguwar rigar baccin irinta Raihan ce. Gashin kan yarinyar a barbaje yake ya rufe fuskarta ta yadda ba kya iya ganin ainihin fuskarta.

Duk abin da yake faruwa tsakanin Raihan da Mommy Abar bauta tana kallo a cikin Kogon dutsen ƙungiya, ranta ba ƙaramin ɓaci ya yi da ganin Mommy na son bata matsala ba. Abar bauta na ganin Mommy ta fito don zuwa ɗakin Raihan ta yi wa Raihan magana da cewa, "Ki hanzarta domin samun nasararki, a yanzu a wanni ne kaɗai suka rage miki don samun ci gabanki. Mahaifiyarki za ta fita ki yi ƙoƙari jan hankalinta zuwa harabar gidanku, sauran aikin ki bar min komai a hannuna ki dawo min da ƙashin bayan mahaifiyata don sauran aikin yana gare ni." Raihan da ke biye da a bayan Mahaifiyarta ta furta, "Biyayya gare ki ta zama wajibi fansar iyayena na gareki ya abar bauta." Raihan na rufe baki ta ci gaba da bin bayan Mommy, tana zuwa ta zauna a harabar gidan kamar yadda abar bauta ta tsara mata.

Alhaji ƙarami ba ƙaramar azaba ya ci a hannun kunamun nan ba, sai da suka ga ya daina motsi sannan suka dakata da azabtar da shi, sakamakon umarnin da uwar ɗakinsu ta basu. Daga wurin da yake Dodon tsafinsu ya ƙarasa cikin takaici don ba ƙaramin haushi ya ji ba ganin ƴan wata ƙungiyar sun azabtar da ta su ɗan ƙungiya ba. A fusace ya kafawa Alhaji Karami haƙora tun yana masa magiya har rai ya yi halinsa, sai da ya tabbatar da baya numfashi ya ɗaga shi yana faɗin, "Da ka mutu ta sanadin wasunmu gara mu ƙarasaka da hannunmu." Kusan lokaci ɗaya Alhaji Karami da matarsa suka Mutu, Likitoci na kan matarsa ta jima tana wani irin fisge-fisge daga ƙarshe ta ce ga garinku nan.

Kabiru yana tafe cikin zuciyarsa yana saƙa da warwara har ya ƙarasa cikin gidan, a lokacin

da ya je ƙofar gidan a buɗe ya samu gate ɗin don haka yana turawa da ya shiga ya wuce ɗakinsa da yake a bakin ƙofa yake idan baka lura ba ma ba za ka san ya fita ba. Yana shiga ya ajiye buhun kayansa ya fito ya ɗaura alwala ya gabatar da sallar Isha'i ya yi shafa'i da wuturi . Ya jima yana addu'a da kaiwa Allah kukansa akan mummunar ƙaddarar da ta same shi daga ƙarshe bayan ya idar ya zauna ya fara tilawar alƙur'ani. Ya kusa awa guda yana karatu sai da ya gama sannan ya fito harabar gidan da babu mutane kowa ya kama gabansa, sai da ya kira Daddy a waya ya tambaye shi ko zai ƙara fita ya tabbatar masa da ya rufe gidan babu inda za shi kuma baƙi duk masu tafiya sun tafi.

Sama-sama Mommy ta fara jin kamar ana ambatar sunanta, har ta yi kamar ta wuce ta ji ba za ta iya giftawa ta bar yarinyar da take ji kamar Raihan ɗin ta ba, don tuni zuciyarta ta fara ayyana mata ko ciwon Raihan ne ya tashi ta buɗe ƙofa ta fita harabar gidan ta zauna. Kai tsaye ta nufi hanyar da za ta sada ta da ƙofar fita, sauri-sauri ta fara yi har ta samu nasarar zuwa barandar harabar waje. Kamar wacce ake fisga haka Mommy ta fara jin zuciya da gangar jikinta na azalzalarta zuwa wurin da wannan matashiyar budurwar take bakin ta na furta, "Hasbunallahu..." Ta fara tunkarar wurin gabanta na ci gaba da tsananta faɗuwa, lokaci ɗaya ta ji wani irin tsoro ya mamaye ta sakamakon jin kukan wasu irin tsuntsaye na tashi a saman kanta. Ta maza ta yi ta ci gaba da takawa har ta ƙarasa wurin da Raihan take zaune, Mommy ta fara ƙoƙarin kai hannu za ta taɓa gadon bayanta tana kiranta, "Raihan!" Shiru ne ya biyo baya ba tare da ta amsa ba, Mommy ta sake sunkunyawa ta ce, "Raihan." A haukace Raihan ta ɗago tana bin Mommy da kallo, da sauru Mommy ta yi baya sakamakon tozali da ta yi da mummunar hallita. A madadin da ga fuskar irin ta bil'adam kamar yadda gangar jikinta ya nuna sai gani ta yi ta yage mata baki mai kamar na kura, cike suke da manyan haƙora da fiƙoƙi ga hancinta tamkar na kare haɗe da idanu jawur kamar garwashi. Mommy da ta faɗi can gefe ta fara ja da baya jikinta na rawa, Gadan-gadan Raihan ta fara takawa gabanta don ta bawa Abar bauta damar aiwatar da abin da yake gabanta. Cikin gigita Mommy ta fara karanta duk wata addu'a da ta zo bakinta, tana yi tana kiran sunan Daddy don ya kawo mata ɗauki.  Tana cikin wannan halin sai gani ta yi wannan hallitar da ɓace daga gabanta, da ƙarfin gaske ta ji ana fisgarta kamar za a yagi naman jikinta.

Kamar wanda aka tasa daga bacci haka fitsari ya farkar da shi, kasancewar ƙafa ta ɗauke ya sa Kabiru ya fito bakinsa ɗauke da addu'a don ya kewaya banɗaki. Bayan ya fito daga can bayan ɗakinsa ya fara jin motsi, har cikin zuciyarsa ya ji kamar ya leƙa ya ga abin da yake motsi amma sai ya yi tunanin dare ne ta yuwu ɓeraye ne suke dabdalarsu. Mommy na jin motsin Kabiru ta riƙa ƙwalla masa kira amma a banza ko kaɗan bai san ana yi ba, sai dai har lokacin bakinta yana ci gaba da karanta ayoyin Ubangiji, da abar bauta ta zo kawo mata cafka sai ta ga mommy ta zille mata kamar tarwaɗa. Kabiru na shiga ɗaki ya koma ya kwanta sai dai fir idanunsa sun bushe bacci ya ƙaurace masa, tashi ya ƙara yi ya fito a ƙofar ɗakinsa ya ɗaura alwala yana shirin shiga ɗaki ya ji ƙusur-ƙusur ɗin ya yi yawa. A hankali ya fara takawa yana haske-haske da ƙaramar fitilarsa, daga can bayan ɗakinsa ya hango Mommy a kwance sai shure-shure take yi tana motsa baki da alama magana take yi. Tsoro ne ya kama shi don ko a mafarki bai taɓa ɗauka mommy bace a wurin, a tsorace ya fara faɗin, "Hajiya lahiya kuwa?" Mommy hannu ta fara miƙa masa tana kiran sunansa, ganin haka ya sa Kabiru ya fara ƙoƙarin

miƙa hannu don ya taimaka mata amma tunowa da abubuwan da suka faru da shi ya sa ya ja da baya yana karanto aytulkursiyyu ya fara tofa mata tare da falaƙi da nasi. Kamar wanda aka yi wa wankin kunne raɗau ya ji maganar Mommy a kunnensa saɓanin da; da baya jin abin da take faɗa, tsugunnawa ya yi a wurin yana faɗin, "Hajiya me ya fito da dake a tsakar daren nan?" Mommy da ta ji jikinta ya fara sarara mata ta ce, "Kabiru taimaka min ka kaini ciki kar su halaka ni." Kabiru ya zaro ido yana dube-dube yana shirin magana mommy ta dafo hannunsa da sauri ya yi baya yana kurma ihu don ya gama tsorata gabaɗaya. Abar bauta da take laɓe ta fara Allah-Allah akan Kabiru ya basu wuri don ta dawo ta ci gaba da abin da take niyyar aiwatarwa, donma ita kanta Mommy ba ƙaramar wahala suka sha akanta ba amma so take ko ta wanne hali ta samu ta lakuci jinin jikinta idan ya so ko da sihiri ne in sun kaiwa ɗakin arziƙi jininta magana ta ƙare. Kabiru har zai shige ɗaki da gudu sai wata zuciyar ta ayyana masa ta yuwu ita ma shaiɗanu sun yi mata abin da suka yi masa ne har suka tsorata ta fito. Bakinsa ɗauke da addu'a ya sake tunkararta Mommy ta dafa kafaɗarsa ta miƙe tsaye tana layi, da ƙyar ta iya tsayawa a kan ƙafarta ta fara takawa da ƙyar kanta na ci gaba da sara mata. Kabiru na raka ta bakin ƙofa zai juya fir mommy ta ƙi yarda don har sa da ta saka Kabiru ya rakata har ƙofar ɗakin Daddy sannan ya koma ɗakinsa, tana shiga ta zube a bakin ƙofa tana ci gana da karanta duk ayar da ta zo bakinta. A lokacin da ta koma ɗakin tuni Daddy ya yi bacci, da rarrafe ta fara rarrafawa zuwa bakin gadon tana kiran sunansa. Sai dai babban abin da ya sake firgitata yadda ta ji yana sauke wani irin munshari mai ban tsoro, ga ƙwan ɗakin da fara ɗaukewa yana kawowa.

Raihan da abar bauta kusan tare suka koma kogon dutsen ƙungiya kowannensu fuska babu walwala, abar bauta ta dubi Raihan rai a ɓace ta ce: "Mahaifiyarki za ta bamu matsala domin tana da riƙo da addini. Sannan wannan Bafulatanin yana ƙoƙarin wargaza shirinmu tabbas za mu ɗau mummunan mataki a kansa, amma fa duk da haka Mahaifiyarki bata sha ba domin za mu ɓullo mata ta sigar da ba za ta taɓa tsammani ba. A yau saura kwana biyar ta fara al'ada don haka zan yi amfani da wannan lokacin, domin alƙawarinta na yi ga ɗakin arziƙi." Raihan ta jinjina kai cikin girmamawa, abar bauta ta nuna wata ƙaramar ƙorama ta ce,: "Ki ɗebi ruwan wanke zunubi ki yi wanka domin kin karya ƙa'idoji da dokar ƙungiya." Raihan na yin wanka kamar yadda Abar bauta ta umarceta ta fice daga kogon dutsen.

Intisar ce ta ɓullo daga ƙarƙashin ƙasa ta yi gaisuwa ga abar bauta, kusan cikin haɗin baki suka furta, "Huzaifa zai aika da Raihan ƙasar India don bincike na musamman akan Raihan." Abar bauta ta yi murmushin takaici ta ce, "Na san da haka shi ya sa na nemo ki yanzu. Zai kaita India ne wurin Kakansa Jibbul-Kasi don ya yi mata bincike a kanta, ya ɗora zarge-zarge akanta ciki kuwa har da ke." Intisar ta jinjina kai sannan ta ce, "Tabbas na san za a yi haka domin na san wanenen Huzaifa da bin didiginsa." Abar bauta ta miƙe tsaye sai da ta yi zagaye wurin sau uku sannan ta ce, "Ba zai yi nasara a kanmu ba, domin za mu mallakawa Raihan duk wani ƙarfin iko, idan a da bata san wacece ita ba ya zama dole mu sanar da ita ta hanyar sakata a ɗakin arziƙi." Hankali a tashe Mugaza ta ɗago tana faɗin, "Kina nufin tun yanzu za ta mallaki shuɗaɗɗan ruhi ba sai nan gaba ba ya Abar bauta." Abar bauta ta ci gaba da tafiya tana jinjina kawunan jikinta ta ce, "Alƙawarin ƙungiya baya tashi, matsawar Huzaifa ya kaita wurin kakansa

tabbas sai ya gane shirinmu kuma sai Kakansa ya wargatsa ƙungiyar nan. Idan kuwa muka saka mata shuɗaɗɗan ruhi dole zai zama garkuwa a gare ta, za ta gagari Jabbul-Ƙasi da dukkan wani shirinsa.

WASAN YA FARA ƊAUKAN ZAFI🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️🤸🏻‍♀️ RAIHAN TA KUSA ZAMA SHUGABA LIKAFA TA CI GABA😂😂 MENENE ALAKAR SHUƊAƊƊAN RUHI DA RAIHAN, SHIN DAMA RAIHAN NA DA WANI A ƘUNGIYAR ASIRI NE DA HAR RUHINSA ZAI MAYE GURBINTA KO YAYA? WACCE ALAƘA CE TSAKANIN SHUƊAƊƊAN RUHI DA KAKAN HUZAIFA JUBBUL-ƘASI? CAKWAKIYAR ƘARA GABA TAKE🥵 MAZA HANZARTA KI BIYA DON JIN YADDA ZA TA KASANCE GARA KI BIYA 300 KI KARANTA AMMA IDAN NA KAMMALASHI SAI KIN SAKA 500 ZA KI SAME SHI🥱🥱🥱 WANNAN SHI NE SHAFIN ƘARSHE WATO SHAFIN ƘAUTA😎 MU JE ZUWA ƳAN GROUP ƊIN *ZAUJATU PAID* A CI GABA DA GASH SUYA SAI RANAR BIKIN NAƊIN 👸🏻 RAIHAN A ƘOGON DUTSEN ƘUNGIYA🤸🏻‍♀️💃🏽

SHARE HILIS🌚